# SHAN AZABA DOMIN KRISTI




Richard Wurmbrand

# Tortured for Christ

## Hausa Ajami Edition

Copyright 2015 Voice Media

info@VM1.global
Web home: www.VM1.global

All rights reserved. No part of the publication may be reproduced, distributed or transmitted in any form or by any means, including photocopying, recording, or other electronic, or mechanical methods, without the prior written permission of the publisher, except in the case of brief quotations embodied in critical reviews and certain other noncommercial uses permitted by copyright law. For permission requests, email the publisher, addressed "Attention: Permission Coordinator," at the address above.

This publication **may not be sold, and is for free distribution** only.

**ABIN DA YASA NA RUBUTA WANNAN LITTAFI**

Ina kawowa kowanne Kirista wanda yake da 'yanci sako daga Ikilisiya ta karkashin kasa wadda ke a bayan labulen karfe wato kasar **KWAMINIS** da kasar **ISLAMA.**

Ikilisiyar karkashin kasa, wadda nake shugabanta har tsawon shekaru da dama, ta yanke shawara cewa lallai ne in yi iyakar kokarin da zan iya in zo duniyar dimokaradiya in bada sako na gaggawa gare ku. Ta wurin al'ajibi, dimbin abin da zaku karanta game da shi, na rayu kuma na iya isowa duniyar dimokaradiya inda mutane suke da 'yanci.

A cikin wannan littafi na bada sako wanda amintaciyar Ikilisiyar karkashin kasa wadda ke cikin kasar Kwaminis. Domin wannan sako daga Ikilisiya ta karkashin kasa ya sami cikakkiyar kulawarku cikin sauri. Da farko na bada shaida kuma na fadi

Irin aikin da Ikilisiya ta karkashin kasa take yi.

**ZUWA GA REV. W. STUART HARRIS:**

Babban Darektan European Christian Mission, London, Wanda, bayan an sako ni daga kurkuku cikin 1964, ya zo Rumania a matsayin masinjan farko na Kirista na kasashen Yammacin Turai. Ya shiga gidanmu da dare, bayan daukar matakan kariya, ya kawo mana kalmomin kauna da ta'aziya na farko da kuma taimako domin jarumawan Kiristi. Ina mika godiyarmu a madadin su.

Wanda ya rubuta gabatarwa

**Rev. W. Staurt Harris, F.R.G.S.**

(Babban Darektan, "European Christian Mission).

## ƘAME DA MARUBUNCI:

Rev. Richard Wurmbrand wani mai aikin bishara ne wanda ya share shekaru goma sha hudu a kurkuku gwamnatin Kwaminis ta kasar Rumania a inda aka gana masa azaba. Yana daya daga cikin fitattun shugabannin kirista, shi kuma mawallafin litattafai ne kuma mawallafi ne. Mutane kima ne suka fi shi suna a duk fadin kasarsu. Acikin shekarar 1945, a lokacin da yan kwaminis suka kwace mulkin kasar Rumania kuma suka yi kokarin sa Ikilisiya karkashin ikon gwamnati domin cimma burinsu, sai nan da nan Richard Wurmbrand ya fara wani yunkuri mai fa'ida, na yadda bishara, ta karkashin kasa, ga mutanensa da Kwaminis suka bautar da kuma sojojin Rasha wadanda suka mamaye kasarsu. A kwana a tashi, sai aka kama shi a 1948 tare da uwargidansa Sabina. Aka kai uwargidansa bauta shekara uku, shi kuma Rishard ya kasace shekara uku a kadaice ba ya ganin wani mutum baya ganin masu gana masa azaba. Bayan shekara uku, sai aka maida shi wani kurkuku wanda yake da fursuna da yawa, a nan ma aka cigaba da gana masa azaba har tsawon shekara biyar.

Saboda matsayinsa na kasancewa shugaba a cikin kirista, sai jami'an ofisoshin jakadanci na kasashen waje dake a kasarsu suka roki gwamnatin Kwaminis ta basu bayani game da lafiyarsa. Sai aka ce da su wai ya gudu ya bar Rumania.'Yan sandan asiri na kasar suka je suka yaudari matarsa da cewa wai su abokan zaman fursunan maigidanta ne, suka fada mata cewa wai sun halarci jana'izar mijinta da aka yi a,makabartar fursunoni. Aka fadawa iyalinsa a Rumania da abokansa na kasashen waje su manta da shi, wai ya mutu.

Bayan shekara takwas sai aka sako shi, nan take ya koma da aikinsa na yadda bishara ta karkashin kasa. Bayan shekara biyu, sai aka sake kama shi a 1959 kuma aka yanke masa hukumcin daurin shekara ashirin da biyar a gidan sarka.

An sako shi a 1964 a lokacin da aka yi wa mutane da dama ahuwa, kuma ya cigaba da aikin bishara ta karkashin kasa. Da Kirista na kasar Norway suka fahimci cewa akwai alamun za a sake kama shi, a tsare karo na uku, sai suka shirya da gwamnatin Kwaminis ta Rumania ta basu shi. Da ma a lokacin gwamnatin 'yan kwaminis ta fara saya da fursunonin siyasa na kasar ta kan kudi fam dari takwas (£800.00). Amma shi an sayar da shi akan fam dubu biyu da dari biyar (£2,500.00).

A cikin watan Mayu 1966 ya je ya bada shaidar azabar da Kwaminis suka ba shi a gaban reshen kwamitin tsaro na majalisar dattawa ta Amerika. Ya tube rigarsa sanadiyar azabar da aka gana masa a kurkukun gwamnatin 'yan Kwaminis na Rumania. Jaridu na kasashen duniya suka dauki wannan labari suka yada shi a kasashen Turai, da Asiya da kuma Amerika. A watan Satumba 1966 sai ya sami kashedi cewa gwamnatin Kwaminis na kasar Rumania ta yanke shawarar yi masa kisan gilla. Duk da wannan barazana bai yi shiru ba. Mutane suka rika kiransa "muryar Ikilisiya ta karkashin kasa." Shugabannin Kirista kuma suna kiransa "jarumi cikin ruhaniya" da kuma "Bulus na kasar Kwaminis."

## SHAIDAR GODIYA

Kungiyar Bishara ta

**" VOICE OF THE CHRISTIAN MARTYRS NIGERIA**

na godiya mai yawa ga Malam Sule Auta, Rev.K.U.Dannat, Rev.G.Y.Na'Allah wanda sun juya wannan Littafi daga Turanci zuwa Hausa, da kuma Pastor.Engr.S.O.Omale, Damaris L. Gwom, da Na'omi Dung,da Emmanuel Ipinyomi, da Nuhu Meck Taime, da David Awarunda kuma Rhoda Suleiman Wadanda suka taimaka cikin wannan aiki.



## TSARIN ABUBUWAN DA KE CIKI


1. YAN RASHA NA JIN KISHIN KRISTI...... 11

2. MUTUM BASHI DA KAUNA .................. 34

3. CETO DA YANCI DOMIN AIKI A KASASHEN YAMMA.......................... 49

4. CIN NASARA AKAN KWAMINISANCI DA KAUNA RUHUN KRISTI...................... 53

5. YARDUWA IKILISIYAR KARKASHIN KAṢA.................................................. 85

6. YANDA KIRISTANCI KE CIN NASARA AKAN KWAMINISANCI.................... 105

7. YANDA KIRISTOCI KASARKSHIN YAMMA ZASU IYA TAIMAKO...................... 126

## GABATARWA:

A cikin watan Disamba 1964 ne na shiga kasar Rumania karo na farko. Kafin wannan lokaci, baya ga kasar Albania, Rumania ce kadai, a cikin duk fadin nahiyar Turai, wadda ban taba sa kafa ba. Na dauki watanni ina samun alamu daga wurin Allah cewa lallai ne in je wannan kasa. Saboda haka sai ni da Rev. John Moseley muka ketare iyaka daga kasar Hungary muka shiga Rumania.

Nan da nan muka gane cewa a kasar 'yan kwaminis hukuma tana lura da duk motsin da za mu yi. Duk da haka nan masubi sun marabce mu sosai kuma ran lahadi da yamma muka je German Baptist Church a Bucharest. A nan aka ba kowanne dayanmu zarafi ya bada shaida. Bayan taron, masu bi da dama suka zo muka gaisa har da wani dogon mutum wanda fuskarsa ta nuna kagarar ya sami zarafin Magana damu. Yayi tambaya ko zai sami yin Magana damu, kuma ya ce zai yi kasadar kai mu gidansa idan zamu yarda mu je. A wannan maraice da kamar karfe goma muka kama hanyarmu ta zuwa gidan da Richard Wurmbrand da iyalinsa suke zama wani dan karamin daki a saman bene.

A hankali muka shiga tare da, wanda a lokacin shine Faston da na sha samun labarinsa a kasashen Yamma, ya warware mana labarin abubuwan da ya ratso da kuma yadda ya rika samun kubuta a cikin shekaru goma sha hudu da yayi a kurkuku. Dansa ya fara lekawa waje daga nan sai uwar gidansa Sabina ita ma ta je da duba ta dawo ta fada mana cewa 'yan sanda sun kewaye gidan. Ko har yaushe zasu kasance kewaye da gidan? Menene za ya zama sakamakon? Richard Wurmbrand ya cigaba har ya gama labarinsa daga nan muka yi addu'a. Wannan addu'a ce wadda ta zauna a zukatanmu, mun roki'Allah domin ya tsare bayinsa. Mun ga tabban raunukan da aka yi masa a lokacin da aka gana masa azaba a kurkuku, akwai hasken daukaka da kauna dake haskakawa. Allah ya amsa addu'oinmu, bayan mun gama hirarmu sai muka duba, muka ga 'yan sandan da suka kewaye gidan sun tafi.

Mun sadu da wannan iyalin Allah, karon farko mun ji shaidu na jarumtaka domin Yesu Kristi, sai dukan mu da muka ji mun sami canji a cikin rayuwarmu. Saboda wannan ne na ga cewa wata daukaka ce aka bani da aka bukaci in gabatar da wannan littafi kuma na yi hakan tare da addu'a Allah ya mori wannan littafi ya motsa zukatan mutane su kaunaci mutanen gabacin nahiyar Turai kuma da fatan nuna masu karamci za ya zama da taimako sosai ga wadanda suke shan wahala saboda Yesu Kiristi, kuma ya cike gurbin da ya biyo bayan wahalar da suka sha saboda Kiristi a cikin jikinsu saboda shi, wato Ikilisiya.



# BABI NA DAYA: ONE

## YAN RASHA NA JIN KISHIN KRISTI

**ARNE YA SAMI KRISTI:**

An rene ni a gidan daba wani addini. A lokacin yarantaka ban sami wani horo game da addini ba.Lokaci da na kai shekara goma na rigaya na zama rikakken arne. Wannan sakamakon mawuyaciyar rayuwa ce lokacin ina yaro. Tun ina da shekara biyu da haifuwa na zama maraya kuma na san abin da ake kira fatara a lokacin shekarun yakin duniya na fari. Lokacin da na kai shekara goma sha hudu na yi imani cewa babu Allah kamar yadda 'yan kwaminis na yau suka yi imani. Na karanta littatafan da mutanen da ke cewa babu Allah, kuma ba wai ban yarda cewa akwai Allah ko Kiristi ba, amma dai na sani wannan ra'ayina ne domin ina ganin yana da hadari ga zuciyar mutum. Saboda haka sai na yi girma da kiyayya ga addini.

Amma daga baya sai na gone na sami alherin zama daya daga cikin wadanda Allah ya zaba saboda dalilai da bani iya fahimtar su. Wadannan dalilai ne wadanda ba su shafi wani abu game da hali na ba, saboda hali na mumuna ne.

Ko da yake ina zaman arnanci wanda nake dauka cewa babu Allah, wani abu wanda bashi da wani tasiri ko da yaushe yana ja na zuwa majami'a. Sai ya zamar mani da wuya in wuce kusa da wata majami'a ba tare da na shiga ciki ba. Duk da haka ban taba fahimtaar abin da ke faruwa a cikin wadannan majami'u ba. Na kan saurari jawabai ko wa'azi, amma basu sukar zuciyata. Na hakikance babu Allah. Na sani zancen cewa akwai Allah wanda shi ne Ubangiji kuma dole in yi biyayya gare shi. Na sani gurgun ra'ayin da nake da shi game da Allah a cikin zuciyata. Amma kuma zan so da na san cewa akwai inda zan sami soyayya a wani wuri a cikin duniya.

Jin dadin da yara da samarai kan samu ni dan kadan na taba dandanawa. Ina marmarin samun wani wuri inda zan sami mai kauna ta.

Na san cewa babu Allah, amma ina bakin ciki da babu irin wannan Allah mai kauna. Wata rana ina cikin irin wannan damuwa ta ruhaniya sai na shiga wata majami'ar katolik na ga mutane a durkushe suna fadi wani abu, na yi tunani, zan durkusa kusa da su, zan kama abin da suka fada kuma zan maimaita addu'oin da suke yi domin in gani ko wani abu za ya faru. Suka yi addu'a ga budurwa mai tsarki. "A gaishe ki, Maryamu, cike da alheri," Na yi ta maimaita kalmonin da suke fadi, na dubi mutum-mutumi na budurwa Maryamu amma babu abin da ya faru. Sai bakin ciki ya kama ni.

Kuma wata rana, ganin cewa ban yarda akwai Allah ba, sai na yi addu'a gare shi ko da yake na yi imani ba shi. Ga yadda na yi addu'a: "Allah, na sani hakika ba ka. Amma idan aka yi katari ka kasance, wanda na hakikance ba hakki na bane in gaskanta da kai, hakkinka ne ka bayyana kanka gare ni." Ni arne ne ban yarda akwai Allah ba amma wannan ra'ayi bai bani salama a zuciyata ba.

A wannan lokaci da nake cikin damuwa da rudu kamar yadda na gano daga bisani - a can a wani kauye cikin tsaunukan kasar Rumania, akwai wani tsoho kafinta da ya yi addu'a kamar haka: "Ya Allahna, na yi maka hidima a nan duniya, kuma ina so in sami lada na a nan duniya da kuma a sama. Kuma lada na a nan duniya shi ne kada ka karbi raina sai na kawo bayahude guda wurin Yesu Kiristi domin Yesu Kiristi ta wannan al'ummar ya zo. Amma ni talaka ne, na tsufa kuma bani da lafiya. Ba zan iya zagayawa ba in nemi bayahude. A cikin kauyenmu kuma babu bayahude. ·Ka kawo wani bayahude cikin kauyenmu, zan yi iyakar kokari na in kawo shi ga Kiristi."

Wani abu wanda ya fi karfi da ya ja ni zuwa wannan kauye. Ba ni da wani abin yi a kauyen, amma na tafi. Rumania tana da kauyuka dubu goma sha biyu.

Da wannan kafinta ya ga cewa ni bayahude ne sai ya kama tashi na kamar yadda ake tashin kyakyawar yarinya. Ashe yana gani na a matsayin amsar addu'arsa saboda haka sai ya bani littafi Mai-tsarki in karanta. Kafin wannan lokaci na sha karanta littafi Mai-tsarki domin sha'awa kawai.

Amma littafi Mai Tsarki wanda ya bani na dabam ne kamar yadda ya fada mini daga baya, sun sha kasha awayi, shi da mafarsa, suna addu'a domin ni da mata mu tuba. Kuma littafi Mai-tsarki wanda ya bani cike yake da kauna wadda addu'oin sa suka lura. Da kyar nike iya karanta shi. Sai kuka kawai ni ke ta yi ina kwatanta muguwa ta da rayuwa Yesu, rashin tsarki na da tsarkinsa. Kiyayya da kaunarsa, kuma duk da haka, ya karbe ni in zama daya daga cikin membobin iyalinsa.

Ba da dadewa ba, bayan na tuba sai mata ta, ita ma ta tuba. Ta kuma kawo wasu mutane cikin garken Kiristi kuma wadanda ta kawo su ma sun kawo matane cikin iyalin Allah da haka sai muka kafa taron sujada na 'yan darikar Lutheran a cikin Rumania.

Ana nan sai lokacin 'yan jamaiyar Nazi ya zo. Akwai wahala a gabanmu. A Rumania, sai ra'ayin Nazi ya sami lasin na mumunan mulkin kama-karya wanda ya jawo tsanani ga Kirista 'yan Fentikostal da Yahudawa.

Tun kafin a kebe ni, kafin ma a shirya ni domin aikin bishara, a gaskiya, nine shugaban wannan sabuwar Ikilisiya wadda na kafa. Nauyin gudanar da aiki a wannan Ikilisiya ya rataya bisa wuya na. Sau da dama ana kama ni da mata ta a yi mana duka kuma a kai mu gaban alkalai na Nazi. Azabar da 'yan Nazi suka yi wa mutane ba kadan ba ce, amma ashe dandanon abin da zai zo karkashin 'yan kwaminis ne. Dole ta sa aka ba dana Mihai sunan da ba na Yahudawa bane domin a kare shi daga kisa.

Amma akwai wata babbar fa'ida ga wannan lokaci na 'yan Nazi. Sun koya mana cewa mutum na iya jimrewa duka kuma ruhun mutum, da taimakon Allah, yana iya jimrewa tsanani.

Suka sa muka koyi yin aikin bishara cikin asiri wanda ya zama, ashe ana shirya mu ne domin wani zamanin da ya fi wannan muni wanda ke gab da auka mana.

**Bishara Ga Mutanen Rasha.**

Saboda damuwa da nike da ita game da rayawar arnanci, tun daga ranar da na tuba na ke marmnarin in kai bishara ga mutanen Rasha.

Mutanen Rasha mutane ne da, tun daga lokacin da aka haife su ake koya masu cewa babu Allah. Allah ya san burina, na yin bishara ga mutane Rasha. Na fara samun cimma wannan buri nawa a lokacin Nazi, saboda muna da dubban fursunonin yaki Rashawa a kasar Rumania kuma muna iya yin ayyukan mu na Kirista a cikinsu.

Aikin ya gudana ta hanya mai ban mamaki. Ba zan taba mantawa da ranar da na fara saduwa da wani fursuna mutumin Rasha ba. Ya fada mani cewa shi injiniya ne. Na tamabaye shi ko ya bada gaskiya ga Allah. Idan da ya ce "a'a" da abin bai dame ni ba sosai. Domin kowanne mutum yana da 'yanci ya gaskanta ko kuma ya ki gaskantawa. Amma lokacin da na tambaye shi ko ya bada gaskiya ga Allah, sai ya daga idanunsa yana kallo na ba tare da ya fahimci abin da nake cewa ba, ya ce. "Ba ni da Odar soja wadda ta ce in gaskanta wannan. Idan an bani Oda, zan gaskanta."

Sai hawaye suka gangaron daga idanuna. Na ji duk zuciyata ta karairaye. Ga mutum tsaye a gabana wanda zuciyarsa ta mutu, mutum wanda ba shi da babbar baiwar da Allah ya yiwa dan adam wato kasancewa mutum wanda ke da 'yanci sanin ciwon kansa. An sangarta kwakwalwarsa, ya zama kayan aiki a hannun 'yan kwaminis wanda yake a shirye, bisa ga irin Oda da ya samu, ko ya bada gaskiya ko kuwa kada ya bada gaskiya. Ba ya iya yin tunani don kansa. Wannan shine misalin mutumin Rasha bayan shekaru masu yawa a karkashin ikon kwaminis. Bayan na murmure daga gigitawar da ganin abin da kwaminis ke yiwa dan adam ta yi mani, sai na yi wa Allah alkawari cewa zan bada raina ga irin wadannan mutane, in mayar masu da 'yancin sun a sanin ciwon kansu kuma in basu bangaskiya ga Allah da kuma Yesu Kiristi.

**Ban bukaci zuwa kasar Rasha ba kafin in sadu da Rashawa**



*Pastor Richard Wurmbrand da kungiyar Ibraniyawa Krista da ya kawo su ga Almasuhu an kuma yi masu Baptisma a boye a zamani Nazi na Romania.*

Daga farkon 23 ga watan Augusta 1944, sojojin Rasha miliyan guda suka shigo cikin Rumania kuma, nan da nan bayan wannan, Jimi'iyar 'yan kwaminis ta kama mulkin kasar. Nan da nan, kamar a cikin mafarki, wahala ta fado mana wadda ta maida waccan wahala karkashin 'yan Nazi wasan yara.

A wannan lokaci, Rumania tana da yawan mutane miliyan goma sha takwas kuma daga cikin wannan adadi jimiyar kwaminis tana da membobi dubu goma kacal. Amma sakataren harkokin waje na Tarayyar Rasha, Vishinsky, ya fada ofishin kaunataccen sarkinmu Michael na daya, ya buga tebur yace, "Dole ka nada yan kwaminis su gudanar da mulkin kasar nan." Aka kwance sojojinmu da 'yan sandanmu dammara, saboda haka ta wurin nuna karfi da kiyayya 'yan kwaminis suka kama mulkin kasar. Kuma da hadin kan shugabanni Amerika da Britaniya na wannan lokaci. A gaban Allah, mutane zasu dauki hakki ba na zunubinsu kadai ba, amma har da na zunubin kasar su. Hakkin wahalolin dukkan kasashen da aka mamaye yana a zukatan Kirista na Amerika da Britaniya. Dole Amerikawa su gane, cewa wani lokaci, cikin rashin sani, suna taim akwa Rashawa wajen dora mana mulkin kisan kai da firi'aunanci. Dole Amerikawa su gyara wannan abu a wurin taimakawa mutanen da aka danne, su sami hasken Kiristi.

## DA HARSHEN KAUNA DA HARSHEN BATANCI DUKA DAYA NE:

Da dai kwaminis suka kama mulki, sai suka shiga shirya wa Ikilisiya makirci. Harshen bayyana kauna daya ne da harshen yaudara da batanci. Mutumin da ke son yarinya da aure da kuma wanda ke so ya kwana da ita kawai da safe ya kore ta dukkan su suna cewa, "Ina son ki." Yesu ya fada mana mu koyi rarrabe harshen yaudara da na kauna dabam, kuma ya fada mana cewa akwai kerketai sanye da fatar tumaki.

Lokacin da 'yan kwaminis suka kama mulki, dubban firistoci da fastoci da masu aikin bishara basu san yadda zasu rarrabe wadannan muryoyi biyu ba.

Jami'iyar kwaminis ta kira taron dukkan kungiyoyin Kirista a ginin majalisar kasar. Firistoci da fastoci da masu bishara dubu hudu

ne suka hallara sun fito daga dukkan darikun Kirista na kasar. Wadannan firistoci da fastoci suka zabi Joseph Stanlin a matsayin shugaban wannan taro, bayan wannan lokaci shine shugaban kingiyar marasa Allah ta duniya kuma jagoran hallaka Kirista. Daya da daya, fisitocin nan da fastoci suka rika tashi a cikin wannan taro suna cewa wai kwaminisanci da Kiristanci daya ne, saboda haka zasu iya yin kafada-da-kafada da juna-wato zasu iya tafiya tare. Daya da daya suka rika tashi suna yabon kwaminisanci kuma suna tabbatarwa sabuwaar gwamnatin goyon bayan Ikilisiya.

Ni da mata ta mun halarci taron. Uwargida na ta zauna kusa da ni ta ce mani, "Richard, ka tashi ka wanke wannan abin kumya daga fuskar Kiristi. Suna tofa masa miyau a fuska." Na ce da uwargida na. "Idan na yi haka, zaki rasa maigidanki." Sai ta ce, "Ba na so in zauna da maigida matsoraci."

Daga nan sai na tashi, na yi Magana ga wannan taro, ban yabi masu kisan Kirista ba, amma na yabi Kiristi da Allah, kuma na ce shi zamu ba girma da matsayin farko. Aka sa jawaban da aka yi a wannan taro a gidan radio kuma dukkan kasar kowa yana iya jin shaidar bisharar Yesu Kiristi daga zauren majalisar 'yan kwaminis. Bayan wannan taro sai da na dandana kuda ta a sakamakon abin da na fada.

Shugabannin Ikilisiya suka rika yin gasar mika wuya ga kwaminisanci. Wani bishop na wata darika ya sa hoton guduma da lauje alamar kwaminis a jikin rigarsa ta limanci kuma ya ce da firistocinsa kada su kara kiransa da gaisuwa irin wadda ake yiwa bishop "Your Grace" amma su kira shi da irin gaisuwar 'yan kwaminis, "Comrade bishop." Na halarci babban taron 'yan

darikar Baftis a garin Resita. An yi wannan taro a karkashin jar tuta ta 'yan kwaminis, a inda aka raira taken Tarayyar kasar Rasha a tsaye. Shugaban darikar Baftis ya kada baki ya ce, abin da shugaban Tarayyar Rasha, Joseph Stalin ya yi, cika dokokin Allah ne. Ya yabi Stalin ya ce Stalin yana kamar wani rikakken malamin Littafi Mai-tsarki ne. Firistoci kamar su Patracoiu da Rosianu sun fi fitowa kiri-kiri a jawabansu. Suka zama jami'an yan sandan asiri
na 'yan kwaminis. Mukaddashi bishop na Ikilisiyar Lutheran a Rumania, Rapp ya fara koyarwa a makarantar tauhidi Seminari cewa Allah ya bada wahayi uku daya ta wurin Musa, daya ta wurin Yesu kuma na uku ta wurin Stalin shugaban Tarayyar Rasha kuma shugaban kwaminisanci. Ya kuma ce kowanne wahayi yana da fifiko akan wanda ya gabace shi

Ina so a fahimta cewa, 'yan Baftis na gaskiya, wadanda nake kauna kwarai da gaske, ba su yarda da wadannan abubuwa da limamansu suka yi ba, kuma sun tsaya da aminci sosai cikin Kiristi, kuma suna sha wahala kwarai. Duk da haka, 'yan kwaminis ne suka zaba masu shugabanni kuma su 'yan Baftis babu wani abin da za su iya yi illa su karbi wadannan shugabanni da aka cusa masu. Wannan batu haka yake a yau game da wasu manyan shugabannin addini.

Wadanda suka zama 'yan-amshin-shata na 'yan kwaminis wato bayin 'yan kwaminis a maimakon bayin Kiristi, sai suka fara kin 'yan uwansu wasanda suka ki bin ra'ayinsu.

Kamar yadda Krista na Rasha suka kafa Ikilisiya ta karkashin kasa bayan juyin-juya hali na kwaminis a Rasha, haka nan kamar mulki da kwaminis suka yi a Rumania da kuma cin amanar Ikilisiya da wasu shugabannin Ikilisiya suka yi, wannan ya tilasta mana kafa Ikilisiya ta karkashin kasa a Rumania wadda take mai aminci wajen yada bishara zuwa ga mutane domin su san Kristi kuma su karbe shi. Yan kwaminis sun hana yin bishara da wa'azi kuma Ikilisiyar da gwamnati ta amince da ita, ta yarda da haka.

Tare da sa hannun wasu masu bi, na fara Ikilisiya ta karkashin kasa. A sarari ina da wani muhimmin mukami wanda ba shi da alaka da wa'azin da ni ke yi ta karkashin kasa, saboda haka wai wannan ya zama wato kaariya kawai. Ina fasto a Norwwegiau Lutheran Mission kuma duk a lokaci guda ina aiki a matsayin wakili a World Council of Churchesa Rumania. (A Rumania ba mu taba zaton wannan kungiya zata iya hada kai ga 'yan kwaminis ba. Domin a wannan lokaci aikin da take yi a kasarmu aikin agaji ne kawai ta sa gaba). Wadannan matsayi guda biyu sun bani martaba a idanun hukuma domin basu rigaya sun san aikin da nike yi a karsashin kasa ba.

**Wannan yan da rassa biyu**

Reshe na farko shi ne aikin bishara da muke yi ga sojojin Rasha a asirce.

Reshe na biyu shi ne bishara a karkashin kasa ga mutanen Rumania da aka bautar.

## RASHAWA - MUTANE NE WADANDA RUHUNSU KE JIN 'KISHI.'

A gare ni, yin wa'azin bishara ga Rashawa wata ni'ima ce. Na yi wa'azin bishara ga mutane daga al'ummomin duniya dabam dabam, amma ban taba ganin mutanen dake shan bishara kamar ruwa kamar mutanen Rasha ba. Ruhunsu yana jin kishin bishara kwarai.

Wani abokina Firis na Ikilisiya masu ra'ayin rikau ya yi mani waya, ya fada mani cewa wani Ofisa na sojan Rasha ya je wurinsa ya tuba ya karbi Yesu Kristi. Abokina ba ya san harshen Rasha ba, saboda haka, ganin cewa na iya Rashanci, sai ya ba shi adireshi na. Washegari sai wannan mutum ya zo wuri na. Yana kaunar Allah, yana marmarinsa, amma ba ya taba ganin Littafi Mai-tsarki ba. Ba ya taba halartar sujada ba (da wuya ka ga

majami'a a Rasha). Ba shi da wani sani ko kadan game da addini. Yana kaunar Allah ba tare da ya san wani abu game da shi ba.

Sai na fara karanta masa wa'azin da Yesu ya yi akan Dutse da kuma misalai da Yesu ya yi. Bayan ya saurari wadannan, sai ya kama rawa da murna yana cewa, "Abin mamaki! Yaya zan yi rayuwa ba tare da Yesu Kiristi ba?" Wannan shi ne karo na farko da na ga mutum ya Zabura da murna cikin Kiristi.

Na dube shi, sai kunya ta kama ni saboda na kira kaina Kirista da kuma fasto, malamin wasu. Domin ban taba nuna bakin ciki kan wahalar da Kristi ya sha kamar yadda wanna hafsan na Rasha ya yi ba. Lokacin da nake kallonsa sai na ga kamar ina kallon Maryamu Magadaliya tana kuka da aniya a wurin giciye har ma a lokacin da Yesu ya zama gawa a cikin kabari.

Daga nan sai na karanta masa labarin tashin Yesu daga matattu. Ba ya san cewa mai cetonsa ya tashi daga cikin kabari ba. Da ya ji wannan labari mai ban al'ajibi, ya buga gwiwoyinsa kuma yayi rantsuwa wadda, ina jin, rantsuwa ce mai "tsarki." Sai ya sake yin murna yana cewa, yana da rai! Yana da rai!" Sai kuma ya sake kecewa da rawa yana zagayawa cikin dakin da matukar farin ciki.

Na ce, "Bari mu yi addu'a!" Ba ya san abin da ake kira addu'a ba. Ba ya san kalaman mu masu tsarki ba. Ya durkusa tare da ni, ya yi addu'a kamar haka, "Ya Allah, kana da kyau! Idan da nine kai, kuma kai ne ni, da ba zan taba gafarta maka Zunubanka ba. Amma lallai kai mutumin kirki ne! Ina kaunarka da dukkan zuciya ta."

Ina jin dukkan mala'ikun dake cikin sama sun daina abin da suke yi domin su saurari wannan addu'a daga hafsan sojojin Rasha. An ribato mutumin ga Kiristi.

A wani kanti, na hadu da wani kaftin na sojan Rasha tare da wata mata hafsan soja. Suna sayen abubuwa dabam dabam amma suna samun wahalar yin Magana da mai sayar da kayan saboda bai fahimtar Rashanci.

Na nuna ina so in taimaka masu in yi masu tafinta daga nan sai muka saba. Na gayyace su su zo su ci abincin rana a gidanmu. Kafin mu fara cin abinci, na fada masu cewa, "kuna a gidan kirista kuma muna da al'adar yin addu'a." Na yi addu'ar cikin harshe Rashanci! Sai suka ajiye cokullansu suka daina sha'awar abincin suka fara jefo mani tambayoyi game da Allah, da Kiristi da kuma Littafi Maitsarki. Ba su san kome ba game da wadannan.

Ba abu mai sauki bane yin Magana da su. Na fada masu zancen misalin da Yesu ya yi da mutum mai tumaki dari da daya daga cikinsu ta bata. Basu fahimta ba. Suka yi tambaya suka ce, "Yaya aka yi ya sami tumaki har guda dari? Masu kula da gonar gandu ta 'yan kwaminis ba su kwace su ba?" Sai na ce da su, Yesu Sarki ne. Sai suka ce, "Dukkan sarakuna azzalumai ne saboda haka mutanen da kuma Yesu lallai miyagu ne." Da na fada masu misali na ma'aikatan gona, sai suka ce," Ai wadannan mutane sun kyauta da suka yiwa mai gonar tawaye. Kamata ya yi gonar ta zama ta gandu." Kome babu ne a gare su.

Lokacin da na basu labarin haifuwar Yesu, sai suka yi tambaya wadda a
wurin mutanen yammacin turai sabo ne, suka ce, "Maryamu matar Allah ce?" Ta wurin tantaunawa da su, na gane cewa yin Wa'azin bishara ga Rashawa, bayan sun rigaya sun yi shekaru da yawa cikin kwaminisanci, dole mu mori sabobin kalamai dabam da wadanda muka saba yin amfani da su.

Mishanarin da suka je Afrika ta Tsakkiya sun sami wahala wajen juya maganar annabi Ishaya. "Idan zunubanku sun yi ja kamar mulufi zasu yi fari kamar snow." Afrika ta tsakkiya babu wanda ya taba ganin snow domin basu da snow saboda haka basu ma da kalma snow. Saboda haka dole suka juya maganar zuwa, "Zunubanku zasu yi fari kamar cikin kwakwa."

Saboda irin wannan ya zama dole ne mu juya bishara zuwa cikin yaren Makisanci kuma mu shirya ta yadda zasu iya fahimta.

Wannan wani abu ne wanda ba mu iyawa da kanmu, amma Ruhu Mai-tsarki za ya yi aikinsa ta wurin mu.

Wannan kaftin da wannan mata hafsan soja sun tuba sun karbi Kiristi a wannan rana. Daga baya, sun taimake mu sosai a cikin aikinmu na yadda bishara ga Rashawa ta karkashin kasa.

A asirce, muka buga dubban littatafan bishara da na addini muka rarrabar a cikin Rashawa. Ta wurin sojojin Rasha da suka tuba muka iya samun damar yin sumogal na Littafi Mai-tsarki da wasu sassan Littafi Mai-tsarki masu yawan gaske zuwa cikin kasar Rasha.

Muka yi amfani da wata dabarar domin kai maganar Allah cikin hannun Rashawa. Sojojin Rasha sun dade suna bakin daga suna yaki da yawa daga cikinsu suna da 'ya'ya da suka baro a gida kuma a duk tsawon shekaarun da suka yi a bakin daga basu ga wadannan iyali nasu ba. (Mutanen Rasha suna son 'yara kamar me). Dana, Mihai, da wasu yara kanana 'yan kasa da shekara 10 sai su je wurin sojoji Rashawa a bisa hanya ko a wuraren shakatawa dauke da Littafi Mai-tsarki, da Litattafan bishara da yawa a aljihunan su. Sai sojojin Rasha sù rika dafa kawunansu suna yin magana da su cikin kauña, suna tunanin nasu yaran da basu sami gani ba shekaru da yawa. Sai sojojin su basu cakulat ko alewa sai su yaran su ba sojojin su amsa da sauri. Yawancin lokaci abin da ya zama da hadari kwarai mu yi a sarari, sai yaranmu su yi ba tare da wani abu ya same su ba. Suka zama yara mishanari ga Rashawa. Kuma an sami sakamako mai kyau gaske. Sojojin Rasha da yawan gaske suka karbi bishara ta wannan hañyar lokacin da babu wata hanyar da za a iya basu bishara.

WA'AZI A BARKIN SOJOJIN RASHA:

Mun yi aiki a cikin Rashawa ba ta hanyar mutum da mutum ba kawai, har ma da yin taro cikin kananan kungiyoyi.

Rashawa suna son agogo sosai suna satar agogo duk inda suka same shi. Sukan tsayar da mutane a hanya su amshe agogonsu.

Kana iya gani mutumin Rasha da agoganni da yawa hannuwansa. Zaka iya ganin matan hafsoshin sojan Rasha sun rataya agogon tebur a wuyansu. Ba su taba mallakar agogo ba sai zuwansu nan, saboda haka agogo ba ya isar su. Rashawa wadanda suke so su sami agogo sai su je barikin sojojin tarayyar Rasha su sayi wadanda aka sato, wani lokaci ma suna sayen agogonsu da sojojin suka sato ko aka kwato. Sai ya zama mutanen Rumania suna iya shiga barikin sojojin Rasha ba tare da wata damuwa ba. Mu 'yan Ikilisiyar karkasahin kasa muka sami hujjar zuwa wurinsu da sunan sayen agogo.

Karon farko na zabi in jaraba yin wa'azi a wata majami'a ta Ikilisiya mai halin rikau wato Orthodox a barikin Rashawa ranar bukin tunawa da manzo Bulus da Bitrus. Na je barikin na soja bisa hujjar sayen agogo. Sai na rika nuna cewa wancan ya yi mani tsada; wancan kuma ya cika kankanta, wani kuma ya cika girma. Sojoji da yawa suka keways ni, kowanne yana kanga mani wani abu in saya, sai cikin wasa na tambaye su, na ce, a cikin ku akwai mai suna Bulus ko Bitrus? Wasu daga cikinsu sunansu ke nan. Daga nan sai na ce. "Ko kun san cewa yau ce ranar da majami'ar orthodox take girmama Manzo Bulus da Bitrus?" (wasu daga cikin Rashawa da suka kwana biyu sun san wannan). Saboda haka sai na ce. Ko kun san ko su wanene Bulus da Bitrus?" Daya daga cikin sojojin Rashan wanda ya dan kwana biyu ya yi zaraf ya katse mani hanzari ya ce, "Ba sayen agogo ya kawo ka ba. Ka zo ne ka yi mana wa'azi. Zauna nan tare da mu ka yi Magana da mu. Amma ka yi hankali. Mu san ko wanene zamu yi hankali da shi! Wadanda ke kewaye da ni duk mutanen kirki ne. Lokacin da na dora hannu na bisa gwiwarka kada ka yi maganar kome sai agogo. Lokacin da na cire hannu na daga bisa gwiwarka sai ka cigaba da bayyane sakon ka." Taro mai girma suka kewaye ni kuma na basu labarin Bulus da Bitrus da kuma labarin Kiristi wanda saboda shi ne Bulus da Bitrus suka mutu. Lokaci zuwa lokaci sai wani wanda basu amince da shi ba ya matso kusa da ni sai sojan nan ya dora

hannunsa a gwiwata nan da nan sai in fara maganar agoganni. Idan wannan mutum ya tafi, sai in cigaba da wa'azin Kiristi. Haka muka yi ta yi da taimakon sojojin Rasha wadanda suke kirista na yi wa'azi sosai. Rashawa 'yan kwaminis da yawa suka zama kirista kuma aka rarraba masu dubban Litattafan Bishara.

An kama 'yan uwanmu na Ikilisiyar karkashin kasa maza da mata da yawa aka basu dan karen wahala amma basu yarda sun tona asirin kungiyar tamu ba.

A lokacin da muke yin wannan aiki, mun sami farinciki saduwa da 'yan uwa daga Ikilisiyar karkashin kasa cikin Rasha kuma mun ji labarin abubuwan da suka gamu da su. Da farko dai mun ga alamun su

rikakkun masu bi ne. Sun ratso shekarun masu dubban Litattafan

Bishara masu yawa a karkashin koyarwar kwaminisanci. Wadansun su ma har sun yi karatu a jami'ar 'yan kwaminis, amma kamar yadda kifi ke zama a cikin ruwan gishiri amma namansa da zaki, haka nan wadannan mutane sun ratso makarantun 'yan kwaminis, amma sun kiyaye ruhunsu da tsarki cikin Kiristi.

Wadannan Rashawa Krista suna da ruhu mai kyau. Suka ce, "Mun sani cewa wannan hoton tauraro da hama da kuma lauje dake a jikin hulunanmu tauraron magabcin Kiristi ne." Suna fadin wannan da bakin ciki mai yawan gaske. Sun taimake mu kwarai da gaske wajen yada bishara cikin sauran sojojin Rasha. Ina iya cewa suna da dukkan halayen Kirista amma basu da halin jin dadi; sun sami farin ciki a lokacin da suke karbi Yesu kawai daga nan farin cikin ya bace. Na yi mamakin abin kwarai da gaske. Na taba tambayar wani dan Baftis, "Yaya baka farin ciki?" Ya amsa ya ce, "Yaya zan yi farin ciki bayan dole ne in boyewa faston Ikilisiya ta cewa ni Krista ne na gaskiya kuma ina yin addu'a ba fasawa kuma ina kokarin jawo mutane zuwa ga ceto cikin Kiristi? Faston majami'arsu dan koren 'yan sandan asiri ne. Makiyayinmu shine dan leken asirinmu kuma makiyayanmu sune suke

bayarda tumakin. A can cikin birnin zuciyarmu akwai murna da farin cikin ceto da muke da shi, amma farin ciki na waje wato a sarari, bamu iya sake samunsa.

"Kiristanci ya zama kamar mafarki a garemu. Lokacin da kai Kirista mai 'yanci ka ribato wani zuwa ga Kiristi, ka ribato memba na rayayyiyar Ikilisiya. Amma a duk lokacin da muka ribatu mutum zuwa ga Kristi, mun sani cewa mai yiwuwa ne a jefa shi kurkuku, mai yiwuwa ne 'ya'yansa su zama marayu. Sai murna da muke da ita ta kawo wani ga Kristi ta garwaye da wannan tunanin cewa dole a biya da wannan."

Mun gamu da wasu irin Krista dabam:



*Hoto na farko na Iyalin Richard Wurmbrand da dansu. Mihai (Michael). Yayinda dukan iyayen suna kurkuku da sansani aikin tukuru. Michael ya rayu kamar "maraya" da wasu Krista suka lura da shi; Amman an rika yi masa ba'a da gwalo a makarantan. Daga baya Michael ya zama Darekta Na Murya Kuntattatu a U.S.A. (Amerika) (Octoba 1967).*

**KRISTA NA IKILISIYAR KARKASHIN KASA.**
**A nan mun ga abubuwan ban mamaki.**

Kamar yadda akwai da yawa wadanda suka dauka cewa su
Kirita ne amma a kashin gaskiya su ba Kirista ba ne, haka nan muka gano cewa a cikin Rashawa akwai mutane da yawa wadanda suka dauka cewa su arna ne irin masu cewa babu Allah, amma a gaskiya su ba arna bane. Akwai wasu Rashawa miji da mata, dukkan su masassaka ne. Lokacin da na yi masu Magana game da Allah, sai suka ce ai babu Allah. Suka ce su 'yan "Bexboshniki" ne wannan wata kungiya ce mai cewa babu Allah. Suka cigaba da cewa, "Amma zamu fada ma wani abu mai ban-shi'awa wanda ya faru da mu.

"Wata rana muka yi aikin sassaka mutum-mutum na Stalin. A lokacin da muke yin aikin, uwar gidana ta tambayi ni ta ce, "Mai gida,
yaya zamu yi babban dan yatsan? Ba zamu iya yin sauran yatsu amma
mu yi watsi da babban yatsa ba, domin idan da dukkan yatsun hannu suna kama da babban yatsa, da ba zamu iya rike kome ba. Dá babu babban yatsa da mutum ba zai iya rayuwa ba. To yanzu, wanene ya yi wannan babban yatsa? Dukkan mu mun koyi akidar Makisanci a makaranta kuma mun sani cewa sama da kasa sun kasance ne don kansu babu wanda ya yi su. Ba Allah bane ya halitta su. Haka na koya kuma na gaskanta da hakan. Amma, idan Allah ne ya halitta sama da kasa, idan da babban dan yatsa ma kawai ya halitta, to da ya isa a yabe shi domin wannan kankanen abu.

"Mun yabi Edison da Bell da kuma Stephenson wadanda suka kago lantarki, da kwan lantarki da tarho da jirgin kasa da kuma sauran abubuwa na hikima. "Kada ki yi maganar sakarci! Kin san cewa babu Allah. Kuma ba zaki taba sani ba ko ana daukar maganarmu a asirce a gida nan, haka nan ba ki sani ba ko zamu fada cikin rikici. Ki shiga hankalinki, babu Allah, kada ki kara yin wani tunani. Babu wani a can cikin sama."

Sai haushi ya ƙama mai gidan, kamar yadda sauran mazaje sukan yi lokacin da matansu suka fada masu abubuwa na hikima. "Kada ki yi maganar sakarci! Kin san cewa babu Allah. Kuma ba zaki taba sani ba ko ana daukar maganarmu a asirce a gidan nan, haka nan ba ki sani ba ko
Zamu fada cikin rikici. Ki shiga hankalinki, babu Allah, kada ki kara yin wani tunani. Babu wani a can cikin sama."

Sai ta amsa masa ta ce, "Ai wannan ma zai fi ban mamaki, idan a cikin sama akwai Allah mai girma wanda a cikinsa ne, cikin sakarci, iyayenmu suka bada gaskiya gare shi, ai abin ya fi mana kyau da yake muna da babban yatsa. Allah mai girma zai iya yin kome, saboda haka yana iya yin babban yatsa ma. Amma ko da babu kowa a sama, Ni, daga waje na, na yanke shawara zan bauta wa babu nan da dukkan zuciyata wanda ya yi babban yatsa." Saboda haka sai suka zama masu bautawa "babu" dake cikin sama. Bangaskiyarsu a cikin Allah da babu sai ta yi ta habaka, suna ta bada gaskiya cewa shi ne kadai wanda ya iya halitta babban yatsa, amma har da taurari, furanni, yara, da duk wani abu mai kyau a cikin rayuwa.

Abin dai kamar yadda ya faru a Atina a zamanin Manzo Bulus lokacin da ya sami wasu a Atina suna sujada ga Allah da ba a sani ba.

Wannan miji da mata sun yi matukar farin ciki da na fada masu abin da suka yi ya yi daidai, domin gaskiya ne a cikin... Sama akwai wani shi ne Allah, wanda shi Ruhu ne: Ruhu kauna, hikima, gaskiya da kuma iko, wanda yake kaunarsu, har ya aiko da tilon Dansa ya bada kansa hadaya a bisa giciye domin su.

Sun zama masu bada gaskiya ga Allah ba tare da sun san da haka ba. Na sami gatancin taimaka su kara yin take guda zuwa samun ceto da gafarar zunubai. Wata rana na ga wata mace hafsan sojan Rasha tana tafiya a hanya. Sai na matsa wajenta na ce da ita ta yi hakuri domin na sani rashin da'a ne mutum ya matsa kusa da matar da bai sani ba, amma ni fastone kuma niyata ta alheri ce. Ina so in yi mata

Magana game da Kiristi. Sai ta tambaye ni ta ce, "Kana kaunar Kiristi?" Na ce "I, da dukkan zuciyata." Daga nan sai ta rungume ni ta yi mani sumba. Wannan abin da rudarwa ga fasto, saboda haka sai ni ma na yi mata sumba domin mutane su yi zaton 'yar uwata ce. Sai ta ce, "Ni ma ina kaunar Kiristi." Na kai ta gidanmu. Da muka tantauna sai na gano cewa bata san kome ba game da Kiristi sai dai sunansa kawai amma duk da
haka tana kaunar sa. Ba ta san cewa shi ne mai ceto ba, kuma bata ma
san abin da ake nufi da ceto ba. Ba ta san inda yake zaune ba, ta kuma san yadda ya mutu ba. Bata san koyarwarsa, rayuwarsa da aikin da ya yi ba. Sai ta zama abin ban mamaki a gare ni. Yaya mutum zai kaunaci wanda sunansa kawai ya tabaji?

Dana yi mata tambayoyi, sai ta bayyana mani cewa, lokacin da take karama, an koya mata karatu ta wurin hotuna. Lokacin da ta je makaranta sai aka koya mata cewa babban aiki mai tsarki dake gabanta a cikin rayuwarta duka shi ne ta tsare akidar kwaminisanci da kuma kasarsu. Ta ce, "An koya mani abubuwa da 'yan kwaminis suke dauka sune daidai. Amma ban san abin da aiki maitsarki yake ba. Ina bukatar ganin hotonsa. Yanzu na gane cewa kakanninmu suna da hoton duk wani abu da yake mai kyau, wanda ya isa yabo kuma wanda yake gaskiya ne cikin rayuwa. Kakata koyaushe takan durkusa a gaban
wannan hoton, tana cewa hoton wani ne da ake kira Kiristi. Kuma ina son wannan suna a cikin raina. Fadin wannan sunan kawai yana bani wani irin farin ciki.

Lokacin da nike sauraren ta, sai na tuna da abin da aka rubuta a Filibiyawa cewa a cikin sunansa kowacce gwiwa zata durkusa. Me yiwuwa ne magabcin Kiristi zai iya samun damar kawar da sanin Allah a cikin duniya har tsawon wani karamin lokaci, amma akwai iko a cikin wannan suna na Kiristi kuma wannan suna ne zai yi jagora zuwa ga haske.

A cikin murna da farin ciki ta karbi Kiristi ya zama mai cetonta a gidana. Yanzu shi wanda take kaunar sunansa yana zaune cikin zuciyarta.



*Sa'annan aka kiro aiakakken "Yesu zuwa ga Richard da Sabina Wurmbrand da yaronsu Mihai, da wasu membobinsu "Ikilisiya "Kalkashin kas". Wanda da yawansu sun kasance a kurkuku tare. Pastor Wurmbrand ya shirya kungiyar masu bi yan Fasakwarin (sumogul) Littattai masu bi dan Tsarki (Bibles) da wasu littattafai zuwa cikin Rasha (Russia). Sun yi tafiya ta baya ta cikin kankara, suna rudun jami'an tsaron iyakan kasa da sun shiga tunanin cewa mutanen suna "kubuta ne" daga Rasha (Russia)*

**Duk take take da na yi da mutanen Rasha cike take da ma'ana mai zurfi.**

Wata 'yar uwa cikin Kiristi wadda ta yada bishara a tashar jirgin kasa ta ba wani hafsan soja, wanda ke sha'awa, adireshi na. Wani maraice ya zo gidana wani dogo kyakyawan laftana na sojan Rasha. Na tambaye shi irin taimakon da yake so in yi masa,. Sai ya ce, "Na zo ne domin in sami haske."

Sai na fara karanta masa wasu sassa na Litafi Mai tsarki wadanda suka wajaba ya sani. Ya dora hannunsa bisa hannuna yace, "Ina rokonka da dukkan zuciyata, kada ka batar da ni. Na fito daga cikin mutanen da aka ajiye cikin duhu. Ka fada mani, idan ka yarda, wannan, hakika, maganar Allah ce? Na tabbatar masa cewa maganar Allah ce. Ya dauki awoyi yana saurare...a karshe ya karbi Kiristi a matsayin mai cetonsa.

Mutanen Rasha, basu daukar maganar addini da wasa lokacinda suke yaki da addini ko kuma suke goyon bayansa kuma suna neman Kiristi. Sukan yi da dukkan ransu. Shi yasa, a Rasha, kowanne Kirista mai aikin bishara ne. Shi ya sa babu wata kasa a duniyar nan wadda lokacin shukawa da samun 'ya'yan bishara ya yi sosai kamar Rasha. Mutanen Rasha suna daga cikin mutanen da suka fi son addini a duniyar nan. Za a iya kawo canji a duniyar nan idan za a kai bishara gare su ta kowanne irin hali. Abin bakin ciki ne yadda kasar Rasha da mutanenta su suka fi kowa yunwar maganar Allah, amma kusan kowa ya manta da su.

A cikin jirgin kasa, wani hafsan sojon Rasha ya zauna a gaba na. Na yi masa maganar Kiristi 'yan mintoci kadan, da suka wuce, sai ya tada da gardama akan cewa babu Allah. Sai yanko maganganun sukar Littafi Mai tsarki da su Mary, Stalin, Voltaire, Darwin da sauransu yake ta yi baya ma bada zarafi a maida murtani. Ya yi Magana kusan awa guda yana kokarin ya shawo kaina in yarda wai babu Allah. Lokacin da ya gama, sai na tambaye shi na ce, "Idan babu Allah, me yasa kake yin addu'a lokacin da ka shiga wahala?"

Kamar barawon da aka same shi yana cikin yin sata ya yi mamaki, sai yace, "Yaya ka yi ka sani ina yin addu'a?" Ban sake ya kufce ba sai na yi masa tambaya ta farko. Na ce masa me yasa yake yin addu'a, "In ka yarda ka amsa mani." Ya sunkuyar da kansa ya furta cewa,:" A bakin dagar yaki, lokacin da jamusawa suka kewaye mu, mu duka mun yi addu'a. Allah da ruhun uwa" wadda kuma a gaskiya addu'a ce mai kyau a idanun shi wanda yake duban zuciya.

**Aikinmu a cikin mutanen Rasha ya bada 'ya' ya da yawa.**

Na tuna da wani mai suna Bitrus. Babu wanda ya sani ko a wane kurkuku ne ya mutu a Rasha. Shi saurayi ne, dan kamar shekara shirin. Ya zo Rumania tare da sojojin Rasha. Ya tuba ya karbi Yesu a wani taro na karkashin kasa ya ce in yi masa baftisma.

`Bayan an yi masa baftisma, na tambaye shi ya fada mana ayar da tafi sukansa har ya rinjayu zuwa ga karbar Kiristi.

Ya ce, ya tuba a wani daga cikin tarurukanmu na asiri, ya saurare ni da kyau a lokacin da na karanta Luka 24, labarin haduwar Yesu da almajirai biyu a kan hanyarsu ta zuwa Imwasu. Lokacin da suka gabaci kauyen, "Bitrus ya ce, "Ina mamakin abin da yasa Yesu ya fadi wannan. A gaskiya yana son kasancewa a tare da almajiransa. To me yasa yace da son sa ne da ya kara matsawa gaba tare da su? Bayani na shine, Yesu yana nuna kawaici ne. Yana so ya tabbatar cewa ana marmarinsa. Lokaci da ya ga lallai an marabce shi, ya shiga gidan da murna tare da su. "Yan kwaminis basu da kawaici, suna shiga cikin zukatanmu da karfin tsiya. Suna tilasta mana mu saurare su tun daga safe har zuwa tsakar dare. Suna yin hakane ta wurin makarantunsu, da gidan radio da jaridu, da fosta, da majigi da tarurukan da ake cewa babu Allah da kuma ko'ina ka juya. Dole ne ka yi ta sauraren furofagandarsu ko mutum yana so ko baya so. Yesu Kiristi yana mutunta yancinmu. Yana kwankwasa kofa a hankali. Yesu ya ribato ni da kawaicinsa."

Wannan babban bambancin dake tsakanin kwaminisanci da Kiristi shi ne ya rinjaye ni.

Ba shi kadai ba ne mutumin Rasha wanda halin Yesu ya rinjaya. (Ni, a matsayi na na fasto ban taba tunanin abin ba ta wannan hanyar).

Bayan ya tuba, Bitrus ya sake saka 'yancinsa da ransa cikin hadari ta wurin yin sumogal na litattafan bishara da kuma taimako domin Ikilisiya ta karkashi kasa daga Rumania zuwa Rasha. A karshe dai aka kama shi. Na sani dai har 1959 yana cikin kurkuku. Ko ya mutu? Ko yana sama ko kuwa yana nan yana cigaba da yakin a nan duniya? Allah kadai ya san inda yake a yau.

Kamar sa, akwai da yawa wadanda ba tuba kadai suka yi ba, amma har da shiga aikin yada bishara gadan-gadan. Kada mu tsaya ga jawo mutum ga Kiristi kawai domin idan muka yi haka, to, mun yi rabin aiki ne kawai. Duk mutumin da aka jawo zuwa ga Kiristi dole ne a maida shi mai jawo wasu zuwa ga ceto cikin Kiristi.

. Mutanen Rasha ba tuba kawai suka yi ba, amma suka zama mishanari a Ikilisiya ta karkashin kasa. Basu da tsoron shaida Kiristi, kodayaushe suna cewa abin da suke yi domin Kiristi, wanda ya mutu domin su, bai isa ba.

## Aikin Bishara Ta karkashin kasa Da Muke Yi Ga Al'ummar Da Aka Bautar:

Reshe na biyu na aikinmu shine aikin mishanari ta karkashin kasa a cikin mutanen Rumania kansu.

Nan da nan 'yan kwaminis suka kware lullubin da suka yi, launinsu ya fita a sarari. Da farkon kama mulkinsu, sai suka rika amfani

da yaudara domin samun goyon bayan shugabanin Ikilisiya, amma ba a kai ko'ina ba suka fara gwada karfi. Suka kama dubban masu bi suka tsare. Sai samun masu tuba su karbi Kiristi ya fara zama kamar almara a gare mu, kamar yadda yake a Rasha tuntuni.

Ni kaina daga baya an sa ni a kurkuku tare d^ ..su bi wadanda Allah ya taimake ni na kawo ga Kiristi. An sa ni daki guda da wani wanda ya baro 'ya'ya shidda a gida yanzu an kawo shi kurkuku saboda ya bada gaskiya ga Yesu. Matarsa da 'ya'yansa suna can suna fama da yunwa. Mai yiwuwa ne ba za ya kara ganinsu ba a nan duniya. Na tambaye shi na ce, "Kana da wata dabara game da ni saboda na jawo ka zuwa ga Kiristi kuma saboda wannan iyalinka suke shan wannan irin wahala?" Ya ce, "Bani da kalmomin da zan iya bayyana godiya ta gare ka saboda ka jawo ni zuwa ga mai ceto. Da babu wata hanya da zan same shi.

Wa'azin Kiristi a cikin sabon halin da muke ciki ba abu mai sauki bane. Mun yi nasarar buga kasidu da yawa na Kirista, muna rarraba su duk da tsananin bincike da 'yan kwaminis suke yi. Mu ba daya daga cikin masu bincike takadun da ake shiga da su wasu litattafai wadanda a bangonsu na gaba akwai hoton Karl Marx wanda ya kago kwaminisanci. An ba litattafan suna, **Addini abin sa Mutane maye ne.** Ya dauka litattafan na kwaminisanci ne kuma sai ya buga hatiminsu a kansu. A cikin wadannan litattafai, bayan an jera kalamai na Marx, Lenin da Stalin, a shafuffukan farko, kuma wannan ne ya sa mai binciken ya gamsu da litattafan, sai muka cigaba muka sanya sakon Kiristi a sauran shafuffukan litattafan.

Ikilisiyar karkashin kasa ba dukkan aikin da take yi ne ke karkashin kasa ba, amma akwai wasu ayyukan da take yi a fili. Muka rarraba wadannan litattaafai masu kama da na kwaminisanci. Da 'yan kwaminis suka ga hoton Karl Marx a bangon sai suka yi ta rubibin sayen litattafan. Lokacin da zasu karanta su kai shafin da ke dauke da zance Allah da Yesu mun rigaya mun yi nisa.

Yin wa'azi a cikin wannan sabon yanayi ba abu mai sauki bane. Ana tsanantawa mutanenmu. 'Yan kwaminis sun kwace kome daga hannun kowa. Daga manomi sun kwace filaye da bisashe.

Daga mai aski ko tela an kwace dan shagon da yake mora. Ba wai 'yan jari hujja wato, masu dukiya kawai aka yiwa wulakanci ba, amma har matalautan gaske su ma suna shan wahala. Kusan kowanne gida suna da mutumin da aka kama aka jefa kurkuku. Talauci da fatara sun yi kamari a wajen mutanen kasar. Mutane suka rika tambaya suna cewa, "Yaya Allah mai kauna ya bari mugunta ta yi nasara?"

Da ba ya zama abu mai sauki ba ga manzanni su yi wa'azin Kiristi a rana Jumma'ar da Yesu ya mutu a bisa giciye yana fadin. "Ya
Allahna, Ya Allahna don me ka yashe ni?" Idan da sun jaraba yin wa'azin.

Amma dashike an iya yin aiki, wannan ya tabbatar da cewa abin daga Allah ne, ba daga gare mu ba. Bangaskiya ta Kirista tana da amsa domin wadannan tambayoyin da mutanen suka rika yi.

Yesu Almasihu ya bada labarin wani talaka mai suna La'azaru, wanda aka zalumce shi kamar yadda aka zalumce mu yana mutuwa da yunwa da gyambuna, har ma karnuka ke lasar gyambunan amma a karshe, mala'iku suka dauke shi zuwa kirjin Ibrahim.

## Yadda Ikilisiyar Karkashin Kasa Ta Yi Wani Sashe Na Aikinta A Fili:

Yan Ikilisiya ta karkashin kasa sukan taru a wani gida cikin daji ko cikin duwatsu duk dai inda suka sami dama. A can, a asirce sukan shirya yadda suke yin aiki na sarari. A karkashin bakin mulki na 'yan kwaminis, muka kago dabarar yin wa'azi a rariya ko hanya wadda, a kwana a tashi ta zama da hadarin gaske, amma duk da haka, ta wurin wannan dabarar mun iya samun damar shaida wa mutane da yawa maganar Allah wadanda da ba mu yi haka ba, da babu yadda za su ji bishara Uwar gida na ta yi aiki tukuru a cikin wannan shirin. Sai kungiyar Kirista su taru a wata kusurwar hanya su kama waka. Sai mutane

u kewaye su domin su ji wakoki masu dadi da suke yi daga ıan sai nan da nan mu bar wurin kafin 'yan sanda su zo.

Wata rana, ina aiki wani wajen dabam, uwar gida na ta yi wa'azi a gaban dubban ma'aikata a kofar harabar wata ma'aikata mai suna MALAZA a birnin Bucharest. Ta yiwa ma'aikatan jawabi game
da Allah da kuma ceto. Wannan shekara, aka harbe da dama daga cikins har lahira a sakamakon zanga-zanga da suka yi ta una rasahin jin adinsu da rashin adalcin 'yan kwa. ıinis. Sun sami sakon a kan lokaci kafin a kasha su.

Mu dai 'yan Ikilisiya ne wadda take aiki a karkashin kasa, amma kamar Yohanna mai Baftisma, muna fada wa mutane da mahukumta sakon Kiristi a sarari.

Wata rana a daya daga cikin gineginen gwammatinmu, wasu yan-uwa Kirista su biyu, suka kutsa kansu zuwa wurin Furaiministan kasarmu Gheorghiu Dej. Cikin 'yan mintoci kadan da suka yi, a gabansa sun sami shaida masa Yesu Kiristi, suka gardade shi ya juya daga aikata zunubansa ya daina tsanantawa mutane. Ya sa aka jefa su kurkuku saboda sun shaida masa bishara. Bayan wasu shekaru, lokacin da wannan furaiminista Gheorgahiu Dej, ya kama rashin lafiya, bishara da suka shuka shekaru dadama da suka gabata, wadda saboda ita ne suka sha wahala, ta bada 'ya'ya. A lokacin da furaiministan yake cikin bukata, sai ya tuna da kalmomin da suka fada masa. Wadannan kalmomi suna daidai da abin da Littafi Maitsarki ya ce, "Gama maganar Allah mai rai ce, mai aikatawa, ta fi kowane takobi mai kaifi biyu ci..." Kalaman suka ratsa kangararriyar zuciyarsa kuma ya bada kansa ga Kiristi. Ya furta zunubansa, ya karbi mai ceto kuma ya fara bauta masa a cikin rashin lafiyarsa. Ba a dade ba sai ya mutu, amma ya tafi wurin sabon mai ceton da ya samu ta dalilin wadannan Kirista guda biyu wadanda suka yarda suka sha wahala a sakamakon shaida masa bishara. Wadannan mutane, suna nuna irin karfin zuciya da Kirista na kasar 'yan kwaminis suke da shi a yau.

Saboda haka wannan ya nuna cewa Ikilisiyar karkashin kasa ta yi aiki ba a taruruka a asirce da wasu ayyuka a lullube kawai ba, amma har da gaba gadin shaida bisharar a bisa titinan 'yan kwaminis da kuma ga shugabannin kwaminis. Akwai sakamako wanda a shirye muke mu bayar. Kuma Ikilisiyarmu ta karkashin kasa har yanzu a shirye take ta fuskanci sakamakon.

'Yan sandan asiri suka tsanantawa wannan Ikilisiya domin sun gane cewa a cikinta ne kadai ake da masu tsayayya da kwaminisanci. Kuma wata irin tsayayya ta ruhaniya, wadda, idan ba a tare ta ba, zata karya ikon arnanci wato rashin gaskantawa da Allah. Sun gane, kamar yadda shaidan kawai zai iya ganowa, cewa wannan Ikilisiya ta fi kome zama barazana a garesu. Sun sani idan mutum ya bada gaskiya ga Kiristi ba za ya taba zama mutum mara tunani wanda sai yadda aka juya shi ba. Sun sani suna iya jefa mutum cikin kurkuku amma basu iya saka bangaskiya ga Allah cikin kurkuku su tsare ta domin wannan al'amari ne na zuciya da ruhun mutum, ba wani abu bane wanda ake iya kamawa. Saboda haka sai suka tashi yaki da Ikilisiya ba ji ba gani.

**Amma kuma Ikilisiyar tana da masu tausaya mata har ma a cikin gwamnatin kwaminis da kuma cikin 'yan sandan asiri.**

Muka umurci Kirista su shiga aikin 'yan sandan asiri kuma su sa wannan inifom din da aka ki jinin a kasar mu domin su iya kawo mana rahoton ayyukan 'yan sandan asiri ga Ikilisiyar mu. 'Yan uwa da yawa na Ikilisiyar suka yi biyayya da wannan umurni suka shiga aiki amma suna rike da bangaskiyarsu a boye. Ba abu mai sauki ba ne iyalinku da abokanka su ki ka saboda kana sa inifom na 'yan kwaminis ba tare da ka fada masu gaskiyar abin da ya kai ka ga yin wannan ba. Duk da haka suka yarda suka shiga. Kaunar da suke yi wa Kiristi mai girma ce.

Lokacin da aka kama ni a rariya kuma aka tsare ni har wasu shekaru a wani wuri na asirin gaske, domin a samo labarin

inda nike, sai wani likita Kirista ya zama cikakken memba na 'yan sandan asiri domin ya binciko inda aka tsare ni. A matsayinsa na likitan 'yan sandan asiri yana da damar shiga kowanne daki a kurkuku da sa ran zai gano ni. Duk abokansa suka guje shi domin suna tunanin ya zama dan kwaminis. Mutumin ya rika yawo cikin inifom na masu bada azaba; ya fi sa inifom na fursuna zama babbar hadaya domin Kiristi.

Wannan likita ya gano ni a can cikin wani dan karamin daki mai bakin duhu kuma ya aika da sako cewa har yanzu ina da rai. A cikin shekaru takwas da rabi da na yi a kurkuku shine aboki na farko da ya gano ni. Ta dalilinsa, labari ya bazu cewa ina da rai kuma, lokacin da aka sako fursunoni a lokacin da dangankar shugaban Amerika Eisenkower da shugaban Rasha Khruschew ta dan inganta a 1956, Kirista suka yi ta kururuwar a sako ni, ni ma kuma aka sako ni har tsawon wani dan lokaci.Ba dan wannan likita Kirista wanda ya shiga aikin 'yan sandan asiri musamman domina ba, da ba za a taba sako ni ba. Da har zuwa yau ina can tsare a kurkuku.

Ta wurin yin amfani da matsayinsu a cikin aikin 'yan sandan asiri, wadannan membobi na Ikilisiyar mu sun sha gargadar mu kuma suka zama da taimakon gaske a gare mu. Har yanzu wannan Ikilisiya tana da mutane a cikin 'yan sandan asiri wadanda suke karewa da kuma gargadar Kirista akan hadarin dake jiransu. Wadansun su suna da manyan mukamai a cikin kusoshin jama'iyar kwaminis duk da haka suna rike da bangashiyarsu cikin Kiristi a asirce kuma suna taimakon mu sosai. Wata rana lokacin da muka kai sama zasu shaida Kiristi, wanda suka yiwa hidima a asirce, da kuma a sarari.

Duk da haka dai, an gano membobin Ikilisiyarmu da yawa kuma aka jefa su cikin kurkuku. Domin muna da irin namu Yahuda Iskariyoti da yawa wadanda suke kaiwa 'yan sandan asiri rahoto. To wurin duka, ja a kasa, barazana da kuma bata suna, 'yan kwaminis sun yi kokarin gano masu aikin bishara da membobin Ikilisiyar wadanda zasu bada rahoto kan 'yan uwansu.



## BABI NA BIYU: TWO

### MUTUM BASHI DA KAUNA

Na yi aiki a matsayin ma'aikacin gwamnati da kuma ma'aikacin Ikilisiya ta Karkashin kasa, har zuwa ranar Lahadi 29 ga Fabrairu 1948. A ran wannan Lahadi ne aka kama ni a hanyata ta zuwa majami'a. Yan sandan asiri ne suka kama ni.

Sau da yawa na sha yin mamakin abinda ake kira "satar mutum." Sai da 'yan kwaminis suka koya mana.

A wannan lokaci aka sace mutane da yawa. Wata motar 'yan sandan asiri ta tsaya a gabana, mutane hudu suka fito daga ciki suka tura ni cikin motar. Aka dauke ni aka batar da ni shekaru da yawa. Har sama da shekara takwas babu wanda ya sani ko ina da rai ko kuwa babu. 'Yan sandan asiri suka je wurin uwar gidana da cewa wai fursunoni ne wadanda da suke tare da ni a kurkuku wai aka sako su. Suka fadawa uwar gidana cewa wai sun halarci janai'zata a lokacin suna kurkuku. Ta yi bakinciki sosai.

Dubban mutane daga dariku dabam sun je kurkuku a lokatai dabam dabam. Ba ma'aikatun Ikilisiya kadai aka rika daurewa ba, amma har da manoma, da yara maza da mata wadanda suke shaida bangaskiyarsu. Dukkan gidajen kurkuku suka cika da mutane, kuma zuwa kurkuku a Rumania, ƙamar a sauran kasashen 'yan kwaminis, yana nufin azaba kawai.

Wani lokaci azabar babu misali. Bana son in fadi wasu irin azabun da na sha. Idan na ambata labarinsu, bani barci da dare. Abin da kuna da yawa.

A wani littafin da na rubuta mai suna "In God's Underground" na bada bayini dalla-dalla dukkan abubuwan da na ratsa.



*Sabina Wurmbrand da dukan Iyalin (su yahudawa ne) sun mutu a sansanai talala cikin Nazi. Sabina da Richard sun sami dama gayatar dan Nazi zuwa gidansu sun kuma ribato shi ga Kristi. Pastor Wurmbrand ya tashi Sabina ya kuma ce, "Akwai mutumen da yana man da yazamadole ki sadu da shi. "Mun gaskanta shi ya kashe Iyalinku amma ya tuba kuma yanzu shi danuwanmu ne'. Sabina ta fita ta kuma mika hannuwanta ta rumgume shi, sai dukansu suka yi hawaye sasai". (Duba cikin Allah Kalkashin Kas sashi 7. Sura 9)*

## Azaba wadda tafi gaban misali:

Wani fasto mai suna Florescu an gana masa azaba da wayoyi da kuma wukaken da aka gasa cikin wuta suka yi jazur. An yi masa dan Karen duka. Daga nan aka sako wasu gaffai a

dan dakin da yake wadanda suka dade basu ci abinci ba suka hana shi barci da cizo, dole ya kare kansa. Idan ya tsaya ya dan huta sai gaffan nan su kawo masa hari.

Ta haka ne aka tilasta masa tsayuwa ba zama ba kwanciya dare da rana har mako biyu. 'Yan kwaminis sun sa rai ta wurin yi masa wannan azabar zasu iya tilasta shi ya bayar da asirin 'yan uwansa masu bi, amma ya ki kememe. A karshe dai, sai suka kamo dansa mai shekara goma sha hudu suka fara dukan sa da bulala a gaban uban suna cewa za su yi ta bugunsa har sai wannan fasto ya fada masu abin da suke so ya fada. Da faston nan ya ga abin da ake yiwa dansa sai ya yarda ya fada masu abin da suke so ya fada. Da fasto nan ya ga abin da ake yiwa dansa sai ya yarda ya fada masu. Da ya kasa daurewa sai yace da dansa. "Alexander, dole in fada masu abin da suke so. Ba zan iya jimre ganin ana dukanka ba." Sai dan ya amsa yace, "Baba, kada ka yi mani rashin adalcin zama uba mai cin amana. Ka jimre, ko da zasu kashe ni, zan mutu da kalmomin Yesu da kasarmu a bakina." Wannan ya sa 'yan kwaminis din nan su kara haukacewa don haushi, suka fada wa yaron nan da duka har ya mutu, jininsa yana ta tsartuwa jikin bangon dakin da faston nan yake. Ya mutu yana yabon Allah. Tun daga wannan abu, kaunataccen dan uwana Florescu ba ya kara komawa yadda yake ba.

Aka sa mana ankuwa mai kusoshi a cikinta hannuwanmu. Idan muka tsaya shiru basu sukanmu. Amma a cikin dakuna masu mugun sanyi, lokacin da sanyi ke kada mu, sai kusoshin su rika sukanmu.

Sai a rataye Kirista kai kasa suna lilo ana duka. Ana sa Kirista cikin akwatun sanyi-wato firiji wadanda don tsananin sanyi duk dusar kankara ce a ciki. Aka jefa ni cikin daya daga cikin irin wannan akwatun kuma babu wata daya daga cikin irin wannan akwatun kuma babu wata suturar kirki a jikina. Sai likitocin kurkuku su rika lekawa ta wata taga sai sun ga alamun mutum za ya mutu daga nan sai su yiwa masu gadi Magana sai su ruga su fid da mu su sa mu a wuri mai dumi. Lokacin da muka ji dumi muka dan warware,

sai nan da nan a maida mu cikin wannan akwatai don sanyi ya sake daskare mu kuma a sake fid do mu a dumama a sake mayarwa cikin sanyi. Haka dai za a yi ta yi babu tsayawa. Saboda wannan wahalar da na ratso, har zuwa yau, bani son in bude firiji in leka.

Ana sa mu Kirista, a akwatuna wadanda basu da girma yadda bamu da ikon yin motsi. Sai a buga kusoshi masu tsini a ko'ina a jikin akwatun. Dole mu tsaya shiru acikin akwatuna. Ana tilasta mana mu tsaya acikin wadannan akwaturta awoyi ba iyaka. Idan gajiya ta kama mu har muka nemi mu jingina, sai kusoshin nan su yi ta sukar mu. Ko yaya muka yi motsi sai manya kusoshin nan su soke mu.

Abubuwan da 'yan kwaminis suka yiwa Kirista sun wuce fahimtar mutum.

Na ga 'yan kwaminis suna ganawa Kirista azaba fuskokinsu suna nuna suna jin dadin abin da suke yiwa Kirista. A lokacin da suke yiwa Kirista azaba sai su rika yin kirari suna cewa, "Mu ne Ibilis."

Muna kokawa ba da nama da jinni ba, amma da masarautu da ikoki na mugunta. Mun gane cewa kwaminisanci ba daga mutane bane amma daga Ibilis ne. Iko ne na ruhun Shaidan kuma sai ta wurin ikon ruhun da yafi ruhun Shaidan ne kawai za a iya tarbarsa, wato Ruhu Allah.

Na tambayi masu gana mana azaba na ce, "Baku da tausayi ne a zuciyarku?"

Yawancin lokaci sai su amsa da Karin Magana ta Lenin wadda take kamanta mutum da itace ko kofen kwai wanda bashi da rai balle ya ji zafi. Saboda wannan irin imani na dangana mutum da abu wanda ba ya jin zafi, sai su kara azaba bisa azaba akan fursuna.

Yana da wuya a gaskanta cewa irin rashin imanin da arnan nan suke da shi mutane ne suke kago shi. Lokacin da mutum ya kasance ba ya a bada gaskiya cewa akwai lada domin aikata alheri ba ko kuwa hukumci domin aikata mugunta babu dalilin da zai sa shi ya yi ladama.

Babu wani abin dake katse masu hamzarin aikata mugunta. Babu wani tausayi irin na dan adam a cikin zukatansu. 'Yan kwaminis masu bada

Azaba sukan ce, "Babu Allah, babu gidan gobe, babu wani hukumci domin aikata mugunta. Muna iya yin duk abin da muka gadama." Na ma taba jin daya daga cikin masu bada azabar ya ce, "Na gode wa Allah wanda ban gaskanta da shi ba da na kawo wannan lokaci da zan iya amayarda dukkan muguntar da ke cikin zuciyata." Ya yi wannan Magana ne lokacin da yake ganawa fursuna wata irin azaba wadda tafi gaban misali.

Masali idan kada ya ci mutum, zan yi bakin ciki amma bazan zargi kadan ba domin shi kada ne. Bashi da hankali na sanin nagarta da mugunta. Saboda haka babu wani zargi da za a iya yiwa 'yan kwaminis domin kwaminisanci ya lallata ruhun sanin nagarta dake cikinsu. Suna takama ko kirari cewa basu da tausayi.

Na koya daga garesu. Tun da basu da wani gurbi domin Yesu a zukatansu, ni ma na yanke shawara cewa ba zan bari wani dan gurbi domin shaidan a cikin zuciyata ba.

Na bada shaida a gaban reshen kwamitin tsaro na cikin gida na majalisar dattawa ta Amerika. A can na bayyana munanan abubuwa da 'yan kwaminis suke yiwa Kirista kamar su, daure Kirista a bisa giciye kwana hudu dare da rana. Ana kwantar da giciyen a kasa ne kuma daruruwan fursuna nan zasu yi fitsari da bayan gida abisa fuskoki da jikin wadanda aka daure a giciyen. Daga nan sai su sake tada giciyen tsaye su yita yi masu ba'a suna cewa, "ku dubi kyakyawan Kiristinku. Kai yana da kyau, kai, ya kawo wani irin kamshi daga sama." Na bayyana yadda, aka sa wani firis yayi addu'a kuma ya bada kashi da fitsari a matsayin jibin Ubangiji ga Kiristan dake a kurkuku, bayan an fitar masa da hankali da duka. Wannan ya faru ne a kurkukun Pitesi cikin Rumania. Daga baya na tambayi wannan firis abin da yasa ba ya gayace mutuwa da aikata wannan muguwar ba'a ba. Sai yace, "Kada ka yi mani shari'a, na sha wahala fiye da Kiristi."

Dukkan bayanin jahannama da azaba dake cikin Littafi Maitsarki ba ya isa a kwatanta shi da azabar dake cikin kurkuku 'yan kwaminis ba.

Wannan an gutsuro kadan ne daga cikin abubuwan dake faruwa a kurkuku Pitesti ranar Lahadi. Ba a iya bayyana wasu abubuwa.

Zuciyata ta kan yi sanyi idan ina bada labarin wadannan abubuwa. Muninsu ya wuce a bayyana a rubuce. Wadannan sune wasu daga cikin abubuwan da 'yan uwanku cikin Kiristi suka ratsa kuma suke ratsewa yanzu haka

Daya daga cikin manyan jarumawan Kiristi shine fasto Milan Haimovici.

Kurkuku duk sun cika makil da fursunoni har ma masu tsaron kurkukun basu iya sanin sunayenmu duka. Suka kirawo mutanen da aka yanke masu hukumci na bulala ashirin da biyar domin sun karya wasu dokoki na kurkuku. Sau da yawa a duk lokacin da aka yi irin wannan kiran sai Fasto Milan Haimovici ya je a doke shi a madadin wani. Ta wurin yin haka ya sami daukaka a wurin sauran fursunoni ba don kansa ba kawai, amma domin Kiristi wanda yake wakilta.

Idan zan cigaba da bada labarin miyagun abubuwa da 'yan kwaminis suka yi da kuma yadda Kirista suka bada kai domin Kiristi, ba zan taba iya gamawa ba. Ba wai azabar da aka ganawa Kirista kadai aka sani ba, amma har da jarumtakar da Kirista suka nuna. Misali na jarumataka da wadanda aka daure suka bayar ta zama dalilin karfafawa da zuga 'yan uwa masu bi wadanda suke da 'yancin walwala.

Daya daga cikin ma'aikatanmu wata budurwa memba ta Ikilisiyar karkashin kasa. 'Yan sandan kwaminis sun gano cewa tana yada bishara a asirce kuma tana koya wa yara zancen Kiristi. Sai suka shirya su kama ta. Amma domin a sa kamun ya zama da zafi kwarai da kuma kuna, sai suka shirya su kama ta ranar aurenta. A ranar auren yarinyar ta sa kayan amarci. Ranar da tafi kowace zama da farin ciki a rayuwarta.

Babu zato babu tsammani sai 'yan sandan asiri suka afka dakin da take.

Lokacin da amaryar ta ga wadannan 'yan sandan asiri, sai ta mika masu hannu domin su sa mata ankwa. Nan da nan suka sa mata ankwa a hannuwa. Sai ta dubi kaunataccenta, daga nan ta yiwa ankwar hannunta sumba, kuma ta ce, "Na gode wa ango na na sama domin wannan awarwaron hannu mai kyau da ya bani a ranar aure na. Na gode masa da ya abani ikon shan wahala domin sa," Sai 'yan sandan suka jata, Kirista angon suna ta kuka. Saboda sun san abin da ke faruwa da 'yanmata Kirista a hannun gandirebobin kwaminis. An sako ta daga kurkuku bayan shekara biyar duk ta tsofo saboda wahala. Angonta ya jira har ran da aka sako ta. Ta ce, wannan karamin aikin da zata iya yiwa Kiristi ne. Irin wadannan kyawawan Kirista suna a Ikilisiyar karkashin kasa.

## YADDA SANGARTA HANKALI YAKE:

Mai yiwuwa ne mutanen yamma suna da labarin sangarta hankali a yakin Korea kuma a yanzu haka a Vietnam. Na ratsa yadda ake sangarta hankali. Shi ne azabar da tafi muni.

Shekara da shekaru sai a zaunar da mu har tsawon awa goma sha bakwai a rana guda muna ta ji ana cewa:

Kwaminisanci yana da kyau
Kwaminisanci yana da kyau
Kwaminisanci yana da kyau
Kwaminisanci yana da kyau
Kiristiyaniti sakarci ne
Kiristiyaniti sakarci ne
Kiristiyaniti sakarci ne
Kiristiyaniti sakarci ne
Ku hakura
Ku hakura
Ku hakura
Ku hakura

Har tsawon awa goma sha bakwai a rana kwanaki bisa kwanaki, makonni bisa makonni kuma watanni bisa watanni.

Kiristoci da yawa sun tambaye ni yadda zamu ki a sangarta hankalinmu. Akwai hanya daya kacal wadda zamu ki a sangarta hankalinmu. Idan kaunar Yesu Kiristi ta tsarkake zuciya, kuma zuciyar tana kaunasa, kana iya yin tsayayya da kowacce irin azaba. Menene amarya mai kaunar Kiristi kamar yadda Maryamu take kaunar sa, wadda ta rike Yesu Kiristi a matsayin jaririnta, idan kana kaunar Yesu kamar yadda amarya ke kaunar angonta, to kana iya jimrewa da kuma yin tsayayya da azaba saboda Yesu Kiristi.

Allah za ya sharanta mu, ba akan yawan jimrewanmu ba, amma akan kauna da muke da it. Ina shaida yadda Kirista wadanda ke cikin kurkukun yan kwaminis suke iya nuna kauna. Suna iya kaunar Ailah da mutane.

Suka cigaba da gana mana azaba da rashin imani babu mai han su. Lokacin da na suma ko na magagace har masu bani azaba suka fitar da zuciya zan fada masu abin da suke so su ji, sai su mayar da ni dan dakina na cikin kurkuku. Can zan kwanta kamar matacce babu mai kulawa da ni har karfi na ya dan dawo yadda zasu iya sake fito da ni su cigaba da gana mani azaba. Da yawa sun mutu a wannan matakin, amma ban san yadda aka yi ba, karfi na ya rika dawowa. A shekarun da suka biyo, a kurkuku da yawa, sun karya mani kashin baya wuri hudu da kuma wasu kasusuwana. Sun tsatsage jiki na. Suka huda jikina har wurare goma sha takwas da karfen da ya yi ja a wuta. Likitoci a Oslo, da suka ga tabban da kuma tabban tarin fuka da na yi a huhuna. Sun shaida cewa yadda har na rayu abin al'alibi ne tsabarsa. Bisa ga litattafansu na kimiyar magani, ya kamata a ce na mutu tuntuni. Ni kaina na sani abin al'ajibi ne.
Allahnmu, Allahn al'ajibi ne. Na bada gaskiya cewa Allah ne yayi wannan aikin al'ajibi domin ku iya jin muryata a madadin Ikilisiyar karkashin kasa dake

a kasar 'yan kwaminis. Ya yarda wani ya fito da rai kuma ya tada murya ya fadi sakon 'yan uwanku masu aminci dake cikin azaba.

**'Yanci na Dan Lokaci Daga nan aka sake kama ni.**

Shekara 1956 ta zo. Na rigaya na kwashe shekara takwas da rabi a kurkuku. Na rame kuma ga munanan tabbai, na ci bugu da hauri da yunwa, da matsi, da tambayoyi da barazana da kuma rashin kulawa. Dukkan wadannan basu sa masu tsare ni sun sami abin da suke so da ni ba. Saboda haka suka karaya suka sake ni. Wani abun da ya taimaka suka sake ni shi ne rashin amincewa da daure ni wanda duniya ta yi ta nunawa.

Aka bar ni na koma matsayina na da, tsawon mako guda kawai. Na yi wa'azi sau biyu, daga nan suka kira ni kuma suka ce da ni ba ni da izinin in sake yin wa'aazi ko in shiga wata harka ta addini. Me na ce? Na ba membobina shawara su yi "hakuri, hakuri, kuma su kara hakuri" "Wato wannan yana nufin kana cewa su kyi hakuri Amerikawa zasu zo su kubutar da su, 'yan sanda suka buga mani tsawa. Na kuma ce sun iya na juyawa kuma lokaci na canjawa. "Wato kana fada masu cewa mulkin kwaminis ba za ya dore ba. Wannan karairayi ne na gaba da juyin juya hali na kwaminis" suka tsauta mani. Wannan ne karshen wa'azi na a bainar jama'a.

Me yiwuwa ne hukuma ta dauka cewa zan ji tsoron karya dokarsu in koma yin bishara ta karkashin kasa. Anan ne suka yi kuskure. A asirce, na koma aikin da, dama nake yi. Iyalina suka bani goyon baya.

Kuma na rika shaidawa kungiyoyin amintattu maganar Allah, na rika kai-da-kawowa cikin mutanen da na amince da su. Wannan karon ina da tabbai wadanda suka zama hujja mai nuna muguntar marasa Allah kuma ina moron tabban domin karfafa masu rauni su dogara ga Allah kuma su nuna jarumtaka. Na zama darekta na kungiyar masu bishara a asirce, wadanda suka rika taimakon juna wajen yada bishara ba tare da 'yan kwaminis sun gani ba. Ko dayake ma, mutumin da idanunsa suka rufe har ba ya iya ganin hannun

Allah yana aiki ba me yiwuwa ba za ya iya ganin aikin da masu bishara suke yi ba.. A karshe dai, shi'awar da 'yan sanda suka yi ta nunawa game da kai-da-kawo da ni ke yi sun sami biyan bukata. Suka sake gano aikin bishara da ni ke yi, suka sake kama ni suka jefa kurkuku. Saboda wasu dalilai, wannan karon basu hada da iyalina ba, me yiwuwa ne saboda yadda sunana ya tafi cikin duniya. An kulle ni har tsawon shekaru takwas da rabi daga nan na sami 'yanci na shekara uku. Yanzu kuma an sake daure ni har tsawon shekaru biyar da rabi.

Zama na kurkuku na biyu yafi na farko muni ta hanyoyi da dama. Na rigaya na san abin da zan gamu da shi. Nan da nan lafiyar jiki na ta tabarbare. Amma muka cigaba da aikin bishara ta karkashin kasa a kurkukun 'yan kwaminis.

## MUKA YI WA'ADI MU YI WA'AZI KUMA SU BUGE MU:

An hana yin wa'azi ga sauran furusunoni. An fahimci cewa duk wanda aka kama yana yin wa'azi za ya sha duka. Da yawa daga cikin mu suka yarda su amshi sakamakon yin wa'azin. Sai ya zama kamar wata yarjejeniya. Muna yin wa'azi kuma suna bugunmu. Muna jin dadin yin wa'azi su kuma suna jin dadin dukanmu. Saboda haka dukanmu muna jin dadi.

Wani abu ya faru wanda an sha yin irin sa har ba na iya tuna ko sau nawa irin haka ta faru. Wato wani dan uwa yana cikin yiwa wani fursuna wa'azi, sai gandireba suka afko masa ba zato, suka ja shi zuwa dakin duka. Bayan sun doke shi har sun gajji, sai suka maido shi suka jefar jini yana ta fasowa jikinsa bisa daben kurkuku. A hankali ya maro, cikin radadi ya mike ya ce, "Yanzu, dan uwa, ina na tsaya kafin a katse mani hanzari?" Sai ya cigaba da wa'azin bishara.

Na ga abubuwa masu ban sha'awa.

Wani lokaci masu wa'azi ba fastoci bane. Masu bine wadanda Ruhu Maitsarki ya zuga su, yawancin lokaci suna yin wa'azi da kyau.

Suna yi da dukkan zuciyarsu, domin yin wa'azi a cikin irin wannan mawuyacin hali ba abu mai sauki bane. Sai gandireba su zo su tafi da mai yin wa'azin su je su yi masa dukan kawo wuka. A kurkukun Gheria, wani Kirista mai suna Grecu aka yanke masa hukumcin duka har ya mutu, hukumcin ya dauki mako guda ana aiwatar da shi. An rika dukansa sannu-a-hankali. Sai ai yi masa duka daya kwakwara a kyale shi sai bayan wasu mintoci kuma a zo a kara masa wani mumunan duka a sake barin sa har wasu mintoci. Ana bugunsa a golaye ne. Daga nan sai likita ya bashi allura. Idan ya maro, sai a bashi abinci mai kyau kwarai domin ya sami karfin jiki, daga nan sai a kara bugunsa har ya mutu da irin wannan bugun ana yi ana tsayawa. Wanda ya jagoranci bada azabar memba ne na kwamintin kololuwa na jami'iyar kwaminis, sunansa Reck.

Lokaci zuwa lokaci sai Reck ya fadi wata kalma wadda 'yan kwaminis sukan fadawa Kirista. "Kun sani, ni Allah ne. Ina da ikon rai da mutuwa bisan ku. Shi wanda yake cikin sama baya iya baku rai. Kome ya dogara a kaina. Idan na ga dama zaku rayu. Idan na ga dama sai in kashe ku. Ni Allah ne." Da haka yake yi wa Kirista ba'a.

A cikin irin wannan mumunan hali, Grecu ya ba Reck wata amsa mai ban sha'awa wadda, daga baya, na ji daga bakin Reck kansa. Ya ce da shi, "Ba ka san zurfi maganar da ka fada ba. Lallai kai wani Allah ne. Kowacce tsutsa a gaskiya filfilo ce idan ta yi girma yadda yakamata. Ba a halicce ka don ka zama mai azaba ba, mutum mai kisan kai. An halicce ka domin ka yi rayuwa irin ta Allah. Yesu yace da Yahudawan zamaninsa. 'Ku alloli ne.' Ran Allah yana cikin zuciyarka. Mutane da yawa iri-irin ka wadanda suka rika ganawa masu bi azaba, kamar su manzo Bulus, sun gane cewa abin kumya ne mutum ya rika aikata ta'asa irin wannan; kuma zasu iya yin abubuwan alheri sosai. Sun zo sun tuba sun zama daga cikin 'ya'yan Allah. In tabbatar maka Reck, a gaskiya Allah ya kiraye ka ne ka zama wani Allah, yayi ka cikin kamannin Allah, ba na mai bada azaba ba."

A wannan lokaci Reck ba ya kula da abin da Grecu ke fada masa ba, kamar yadda Saul na Tarsus bai kula da shaida mai kyau da Stephen ya fada lokacin ana cikin kisan sa a gaban Saul ba. Amma wadannan kalmomi sun yi aiki a cikin zuciyar Reck. Daga baya Reck ya gane wannan Magana da Grecu ya yi masa lallai kira ne na Allah mai iko duka.

Wani babban darasi ya taso daga duka, da azaba da haukan da 'yan kwaminis suke yi mana: darasin shi ne, mun gane cewa ruhu shi ke iko da jiki. Yawancin lokaci idan ana gana mana azaba, muna jin azabar amma sai mu ji kamar wani abu ne nesa damu kuma nesa da ruhunmu wanda ke nutse cikin darajar Kiristi da kuma kasancewarsa tare da mu.

Lokacin da aka bamu gutsuren burodi guda a mako da kuma wata kazamar miya kullum,, sai muka shawarta zamu rika bada zakka daga wadannan abubuwa. Kowanne.

Mako na goma, sai mu dauki gutsuran burodin nan mu ba dan uwanmu wanda ya fi mu jikata a matsyin zakkarmu zuwa ga Ubangiji.

Aka yanke wa wani Kirista hukumcin kisa. Kafin a kashe shi, sai aka kyale shi ya ga matarsa. Kalmominsa na karshe ga matar tasa sune: Dole ki sani cewa na mutu ina kaunar wadanda suka kashe ni. Basu san abin da suke yi ba kuma rokona na karshe gare ki shi ne, ki kaunace su ke ma. Kada ki rike su cikin zuciyarki saboda sun kashe kaunataccen ki. Zamu sadu a sama." Wadannan kalmomi sun soki jami'in 'yan sandan asiri wanda ya kasance a wurin lokacin da mutumin yake fada wa matarsa wannan Magana kuma daga baya ya fada mani wannan zance a kurkuku, inda aka sa shi don ya zama Kirista.

Akwai wani saurayi furusuna mai suna Matchevici a kurkuku Tirgu-Ocna. An sa shi a kurkuku yana da shekara goma sha takwas. Saboda tsananin azaba ya kamu da ciwon tarin fuka. Iyalinsa suka sami labari cewa yana cikin wannan mawuryacin hali, sai suka aika masa da magani mai yawan gaske wanda zai iya taimaka masa ya sami lafiya.

. Sai jami'I mai kula da kurkukun ya kira shi ya nuna masa kunshin maganin yace, "Ga maganin da za ya iya ceton ranka. Amma ba a baka izinin karbar wani sako daga iyalinka ba. Bisa ga ra'ayi na, ina so in taimake ka. Kai yaro ne. Bana so ka mutu a kurkuku. Ka taimake ni domin ni ma in iya taimakon ka. Ka bani bayani kan abokan zaman fursunanka, wannan za ya kare•ni a gaban shugabannina idan suka ji na baka wannan sako," Matchevici ya amsa ya ce bana so in rayu, kuma zan ji kumya idan na duba madubi na ga fuskar mai cin amana. Ba zan iya yarda da wannan ka'ida taka ba. Na fi so in mutu." Sai jamin'in 'yan sandan ya kama hannunsa ya ce, "Ina yi maka barka. Bani sa ran wata amsa kuma daga gare ka. Amma ina so in baka wata shawara. Wasu fursunoni sun zama masu kawo mana labari. Suna yin baki biyu. Bamu yarda da su ba. Muna so mu sani ko suna da aminci game da kai ko masu cin amana ne. Suna yi maka batanci da yawa, suna bamu labarin kalamanka da ayukanka. Na fahimta baka so ka bashe da abokanka. Amma ka bamu labarin mutane wadanda suke kin ka ceci ranka.

"Matchevici ya amsa nan take, kamar yadda ya yi da farko, ya ce, "Ni almajirin Kiristi ne kuma Kiristi ya koya mana mu kaunaci har ma wadanda suka bashe mu lallai sun yi mana magunta sosai, amma ba zan rama mugunta da mugunta ba. Ba zan iya baka wani bayani akansu ba. Ina jin tausayinsu, ina addu'a domin su, ba na fata wani abu ya hada ni da kwaminis." Matchevici ya dawo daga wurin tautaunawa da jamin'in 'yan sandan ya kuma mutu a dakin kurkuku inda nake. Ina gani ya mutu yana yabon Allah. Kauna ta yi nasara da har ma marmarin rayuwa.

Idan matalauci yana kaunar kide-kide, yana iya bada kwabon da yake da shi domin ya shiga wurin da ake kide-kide. Daga nan ya zauna ba kudi, amma ba ya jin haushi. Ya ji abubuwa dake yi masa dadi.

Ba na jin haushi na yi hasarar shekaru da yawa a kurkuku. Na gano abubuwa masu kyau. Ni kaina na kasance daga cikin wadanda suke marasa karfi kuma marasa daraja a kurkuku, amma na sami sa'ar kasancewa a daki guda tare da manyan tsarkaka, jarumawan bangaskiya wadanda za a iya kwatanta su da Kirista na karnin farko. Sun je sun mutu cikin farin ciki saboda Yesu Kiristi. Ba a taba iya bayyana kyau na ruhaniya na wadanan tsarkaka da kuma jarumawan bangaskiya.

Abubuwan da na fada a nan suna daga cikin wannan kyau na ruhaniya.

Ikilisiyar karkashin kasa ita ce Ikilisiyar da ta maido da kauna irin ta farkon Ikilisiya.

Kafin in je kurkuku, ina kaunar Kirista sosai. Yanzu, bayan na ga "Amaryar Kiristi" a kurkuku, zan ce ina kaunar Ikilisiya ta karkashin kasa kamar yadda nake kaunar Kiristi kansa. Na ga kyaunta wato ruhun sadaukar da kai ga Kiristi.

## ABIN DA YA FARU DA IYALI NA:

Aka dauke ni daga uwar gida na ban san abin da ya faru da ita ba daga baya. Sai bayan shekaru da yawa na ji cewa an sa ta a kurkuku ita ma. Mata Kirista suna shan wuya a kurkuku kwaminis fiye da maza. Gandireba suna yiwa 'yan mata fyade. Abin da ake yi masu ba ya fado sai oda muninsa. Ana tilastawa mata su yi aiki mai wuya wajen ginin magudanar ruwa, suna yin aiki iri daya da maza. Ana sa karuwai su rika duba su kuma karuwan har gasar ba tsarkaka wuya suke yi. Matata har ciyawa ta ci kamar shanu domin kada ta mutu da yunwa. A wurin ginin magudanar fursunoni suka rika cin beraye da macizai saboda tsananin yunwa. Daya daga cikin abubuwa da gandirebobin suke jin dadinsa shi ne ranar lahadi sai su jefa matan cikin rafin Danube sa'annan su rika tsamo su kamar yadda ake kama kifi. Aka jefa matata cikin rafin Danube kamar yadda ake yiwa sauran.

Aka bar dana yana yawo a rariya, an kame ubansa da uwarsa. Mihai yana da kokari a addini tun yana karamin yaro kuma yana da shi'awa kwarai kan al'amuran bangaskiya. Daga baya, yana da shekaru goma sha tara,. Lokacin da aka dauke babansa da mamansa ya ratsa wahaloli cikin rayuwarsa ta Kirista. Ya zama da bakin ciki sosai har ma ya rika tambayar kansa game da addininsa. A wannan shekaru nasa ya shiga matsaloli irin wadanda yara kamarsa basu faye gamuwa da irinsu ba. Ya zamar masa dole ya ciyar da kansa.

Ya zama laifi ne mutum ya taimaki iyalan Kiristan da aka kama. Wasu mata biyu da suka taimake shi daga baya aka kama su aka yi masu dukan kawo-wuka har suka zama guragu har zuwa yanzu shekaru goma sha biyar da suka wuce. Wata mata da ta yi kasadar daukar Mihai zuwa gidanta aka yanke mata hukumcin daurin shekara takwas domin ta aikata laifin taimakon iyalan wadanda aka tsare a kurkuku. Aka gaggabe dukkan hakoranta. Aka kakkarya kasusuwanta. Ita ma daga nan ta gurgunce.

## "MIHAI YA BADA GASKIYA GA YESU."

Mihai ya fara ciyar da kansa yana da shekara goma sha daya. Wahala ta kawo masa gargadi cikin bangaskiyarsa. Amma bayan shekara biyu da daure uwarsa, an ba shi damar ya ganta. Ya je kurkukun 'yan kwaminis ya ga mamarsa. Duk ta yamutse, ta yi datti, ta rame, tana sanye da mumunan inifan na fursuna. Da kyar ya gane ta. Kalmomin da ta fara fada masa da suka yi ido biyu sune:

"Mihai, ka bada gaskiya ga Yesu." "Nan da nan gandirebobi suka janye ta cikin fushi. Mihai ya yi kuka saboda ganin yadda aka janye mamarsa a wulakance. Wannan saduwa da ya yi da mamarsa ta minti daya itace sassalar da ta sa ya tuba ya karbi Kiristi. Ya gane cewa idan har mutum za ya iya kaunar Kiristi a cikin irin wannan hali da uwarsa take ciki, to lallai Kiristi shi ne mai ceto na hakika.

Daga baya ya ce, "Idan ma Kiristiyaniti bashi da wata hujja dake goyon bayansa, yadda mamata ta gaskanta da shi ma kawai ya ishe ni. "Wannan ce ranar da ya karbi Kiristi a matsayin mai cetonsa.

A makaranta ya yi ta gwagwarmayar rayuwa. Ya zama yaron kirki a makaranta har aka ba shi lada na jan nektayi alamar ya zama memba na matasan kwaminis da ake kira, "Young Communist Pioneers." Da na ya ce, "Ba zan taba sa nektayin mutanen da suka daure uwata da ubana a kurkuku ba." Sai aka kore shi daga makarantar saboda wannan. Bayan ya yi hasarar shekara guda, ya sake shiga makaranta, ya boye cewa shi dan wani Kirista ne fursuna.

Daga baya ya rubuta littafin bincikensa akan Littafi Maitsarki. A ciki ya rubuta, "jayayya da ake akan Littafi Maitsarki bata da tushe kuma duk soke-soken da ake yi akansa ba gaskiya ba ne. Lallai malamin bai karanta Littafi Maitsarki ba. Littafi Maitsarki yana jituwa da ilimin kimiya." Sai aka sake korarsa daga makaranta. Wannan karon ya yi hasarar shekaru biyu.

A karshe dai aka kyale shi ya yi karatu a saminari. Aka koya masa tauhidin Makisanci (Marxist). Ana bayyana kome bisa ra'ayin Karl Marx. Mihai ya nuna rashin amincewarsa a sarari a cikin aji. Sauran dalibai suka goyi bayansa. Sakamakon wannan shi ne, aka kore shi kuma ba ya iya gama karatun tauhidi ba.

Wata rana a makaranta, wani shehun malami ya yi jawabi akan rashin yarda da kasancewar Allah sai dana Mihai ya tashi ya karyata shi ya kuma fada masa alhakin dake wuyansa saboda ya batar da matasa da yawa. Dukkan daliban ajin suka goyi bayansa. Ya zama dole ne mutum ya yi gaba-gadin yin Magana da farko. Daga nan saura sai suka goyi bayansa. Domin ya sami ilimi sai ya yi ta kokarin boye cewa shi dan Wumbrand ne, Kirista fursuna. Amma sau da yawa sai a gane kuma a sake maimaita abin da aka saba, wato a kira shi Ofishin darektan makaranta a ce an kore shi.

Mihai ya sha wahala ta yunwa.

Yawanci lokaci iyalan Kiristan da aka daure a kasashen kwaminis suna kusan mutuwa da yunwa. Babban laifi ne mutum ya taimake su.

Zan ba ku labari guda na irin wahalar da wannan iyali suke sha. Aka jefa wani dan uwa kurkuku saboda aikin da yake yi cikin Ikilisiya ta karkashin kasa.

Ya bar mata da 'ya'ya shidda a gida. Manyan 'ya'yansa suna da shekara sha bakwai da sha tara kuma 'yan mata ne, basu iya samun aiki ba. Saboda a kasar kwaminis gwamnati kadai ce ke bada aiki kuma bata bada aiki ga 'ya'yan Kiristan da aka dauka masu laifi. Idan kun yarda kada ku dubi wannan labari ta fuskar maganar rayuwar tsarki. Ku dai karbi gaskiyar abin da ya faru kawai. 'Yan matan nan biyu 'ya'yan wannan jarumin Ikilisiya su ma Kiristoci ne wuya ta sa suka shiga karuwanci domin su sami abin da zasu rike kannensu da uwarsu wadda take fama da rashin lafiya. Kanensu mai shekara goma sha hudu da ya ga abin dake faruwa da su ya haukace dole aka kai shi gida tababbu. Lokacin da Ubansa ya dawo bayan ya yi shekaru a kurkuku, addu'ar da ya yi kawai ita ce, "Allah ka sake kai ni kurkuku. Ba zan iya ganin wannan abu ba." Allah ya amsa addu'arsa, yanzu yana kurkuku saboda ya yi wa yara wa'azin Kiristi. 'Ya'yansa mata sun daina karuwanci. Sun sami aiki bayan sun yadda da sharuddan 'yan sandan asiri. Sun zama masu kawowa 'yan sanda labarai. A matsayinsu na 'ya'yan jarumin Kirista, ana karbar su da daraja a kowanne gida. Sai su saurara da kyau kuma su kai wa 'yan sanda rahoton dukkan abin da suka ji, kada kawai ka ce wannan mugun abu ne kuma rashin ruhaniya ne i gaskiya ne amma ka tambayi kanka ko wannan ba har da zunubinka yasa wadannan miyagun abubuwa ke faruwa ba? Yadda aka yi watsi da irin wadannan iyalai na Kirista, kun bar su babu taimako daga ku dake da 'yancin walwala.



# BABI NA UKU:THREE

## CETO DA YANCHI DOMIN AIKI A KASASHEN YAMMA.

Na yi shekara goma sha hudu a kurkuku. A lokacin zama na kurkuku ban taba ganin Littafi Maitsarki ko wani littafi ba. Na manta da yadda ake rubutu saboda tsananin yunwa da azaba. Na manta da maganar Allah. Amma a ranar da na cika shekara goma sha hudu sai wata aya ta fado mani a rai mai cewa, "Yakubu ya yi aiki domin Rachel shekara goma sha hudu."

Nan da nan bayan wannan, sai aka sako ni a cikin wata ahuwa da aka yi wa fursunoni a kasar a sanadiyar koke koken da Amerikawa suka yi ta yi game da abin da kwaminis ke yi a kasar. Na sake ganin mata ta. Ta yi hakurin jira na har shekara goma sha hudu.

Mu ka fara sabuwar rayuwa cikin matsananciyar fatara saboda idan an kama mutum an tsare shi a kwashe duk abin da ya mallaka.

Fastoci da Firistoci wadanda aka sako suna iya samun kananan majami'u su dauke su ciki. Aka bani wata majami'a a garin Orsova. Sashen kula da addini na kwaminis an fada mani cewa akwai membobi talatin da biyar a majami'ar kuma kada in sake su karu har su kai talatin da shida. Kuma suka ce da ni dole in zama dan leken asiri in rika kaiwa 'yan sandan asiri rahoton kowanne memba kuma kada in yardar matasa su shiga majami'ar. Wannan ita ce hanyar da kwaminis ke moran majami'u a matsayin kayan aiki mallakar su.

Na sani idan na yi wa'azi mutane da yawa zasu zo domin su ji. Saboda haka ban ma yi tunanin in yi wa'azi a majami'ar da take mallakar gwamnatin kwaminis ba. Na sake komawa aiki da Ikilisiya ta karkashin kasa.

A lokacin zamana kurkuku shekara sha hudu. Allah ya yi mana manyan ayyuka. An tuna da Ikilisiya ta karkashin kasa. Amerikawa da sauran Kirista suka fara taimakawa da kuma yi mana addu'a.

Wata rana ina hutawa a gidan wani dan uwa a wani gari sai ya tashe ni daga barci ya ce. "Yan uwa daga kasar waje sun zo." A yammacin duniya akwai Kiristan da ba su manta ko yin biris damu ba.

Kiristoci sun hadu sun shirya wata kungiya wadda take yin aikin agaji ga iyalan Kiristocin da aka kama. Tana yin wannan aiki a asirce. Tana kuma yin sumogal na litattafan addini.

A guda dakin dake gidana sami 'yan uwa su biyar wadanda suka zo domin yin aikin agaji. Mun yi hira da su sosai. Bayan mun dade muna Magana sai suka fada mani cewa sun ji labari cewa a wannan wurin akwai wani wanda ya yi shekara goma sha hudu a kurkuku kuma suna so su gan shi. Na fada masu ai nine mutumin. Sai suka ce, "Mun zaci za mu ga mutumin cikin bakin ciki. Ba kai bane mutumin domin kai kana cike da farin ciki. 'Na tabbatar masu cewa ni ne aka tsare a kurkuku har shekaru goma sha hudu. Kuma ina da farin ciki ne saboda zuwansu wanda ya nuna cewa yanzu kam ba a manta da mu ba. Taimako ya fara zuwa akai akai ga Ikilisiya ta karkashin kasa. Ta wurin wasu hanyoyi a asirce, muka sami Littafi Maitsarki da yawa da wasu litattafai na addinin Kirista da kuma taimako domin iyalan Kiristocin da aka tsare saboda Kiristi. Yanzu da muke samun taimako, mu 'yan Ikilisiyar karkashin kasa muna iya yin aiki sosai.

Ba maganar Allah kawai suka ba mu ba amma har da kauna. Sun kawo mana ta'aziya.

A cikin shekarun da muka yi ana sangartadda hankalinmu, mun rika jin ana cewa, "Babu wanda ke kaunar ku kuma, babu mai kaunar ku, babu mai kaunar ku." Yanzu mun ga Kiristocin Amerika da Turai wadanda suka sayar da rai domin su nuna mana kauna.

Suka karbi shawarar mu suka tsara dabarar yin aiki a kasarmu a asirce. Sukan lallaba su shiga gidajenda suke kewaye da 'yan sandan asiri ba tare da 'yan sanda sun sani ba.

Kiristocin Amerika ko na Turai, wadanda suke cikin tsakkiyar Littafi Maitsarki iri-iri, ba zasu iya fahimtar irin darajar Littafi Maitsarki da suka yiwo mana sumogal yake da ita ba.

Baicin taimakon da na samu daga 'yan uwa Kirista na kasashen waje, ni da iyali na da ba mu rayu ba. Haka kuma ya kasance da yawanci fastocin Ikilisiyar karkashin kasa na kasashen kwaminis wadanda aka taba daurewa saboda Kiristi. Ina iya bada shaida bisa abin da na sani game da kayan agaji da kuma taimako na fuskar goyon baya da kungiyar "European Christian Mission of Great Brain" suka bam u. A gare mu, mutanensu suka zama kamar malaikun da Allah ya aiko.

Saboda farkawar aiki da aka samu a Ikilisiya ta karkashin kasa, na shiga babban hadari na sake zuwa kurkuku. A wannan lokaci, kungiyoyin Kirista irin su "Norwegian Mission to the Jews" da kuma "Hebrew Christian Alliance" suka biya fan dubu biyu da dari biyar ($2,500) domin fansa ta daga gwamnatin kwaminis. Yanzu ina iya fita daga kasar Rumania.

## ABIN DA YASA NA BAR KASAR RUMANIA

Duk da hadarin da nike ciki, ban so in bar Rumania ba, amma shugabannin Ikilisiyar karkashin kasa suka umurce ni in fito daga kasar domin in zama kakakin Ikilisiyar a kasashen duniya wadanda suke da 'yancin walwala da na addini. Sun bukace ni in yi Magana da ku mutanen yammacin duniya a maddadin su game da wahalolinsu da bukatocinsu. Na zo nan yamma, amma zuciyata tana tare da su. Idan da ban fahimci wajabcin ko jin labarin wahalolinsu da kuma ayyukan jarumataka da Ikilisiyar karkashin kasa ke yi ba, da ba zan taba barin Rumania ba. Wannan shine aikin da ya kawo ni nan.





*Bayan shekaaru fiye da goma sha hudu (14 years) a kurkuku kwamunis cikin Romaniya, Pastor Richard Wurmbrand ya ba Krista masu yawa Yammanci mamaki ta wurin nuna kauna mara sharadi da gafartawa... yana kin zunubin tsarin komunis amma yana kaunar masu komunis din.*

Kafin in baro Rumania, na je wajen 'yan sandan asiri har sau biyu. Sun fada mani cewa an biya kudi domina. (Rumania tana sayar da 'yan kasarta saboda matsalar tattalin arzikin da kwaminisanci ya kawo wa kasar). Suka ce da ni ka tafi yamma ka yi wa'azin Kiristi iyakar yadda kake so, amma kada ka tabo mu.

Kada ka yi ko kalma guda wadda take gaba da mu. Mun fada maka a fili abin da za ya faru da kai idan ka bada. Labarin abin da ya faru. Da farko dai, da £500 zamu iya samun kungiyar 'yan iska su kashe ka ko su sace ka. (Ni kaina na zauna a daki guda a kurkuku tare da wani bishop na Ikilisiya mai ra'ayin mazan jiya mai suna Vasile Leul, wanda aka sato daga kasar Austria aka kawo shi Rumania. Duk an ciccizge masa farota. Kuma na zauna da wasu daga Barlin. Kwana kwanan nan an sato wasu 'yan Rumania daga Italy da Paris). Suka kuma kara da cewa, "Muna iya lalatar da kai ta wurin baza labari akan ka da wata yarinya, ko sata ko kuma wasu zunubai da kayi lokacin kana matashi. Mutanen yamma musamman Amerikawa ba wuya a rude su ko a damfare su."

Bayan sun gama yi mani barazana, sun bar ni in zo kasashen yamma. Suna tunkaho da yadda suke sangartadda hankalin mutane, irin abin da na ratsa. Yanzu a kasashen yamma akwai mutane da yawa wadanda suka ratso irin wannan, amma sun yi shiru. Wadansu daga cikinsu har ma yabon kwaminisanci suke yi bayan azabar da suka sha a hannun 'yan kwaminis. 'Yan kwaminis sun hakikance ni ma zan kame baki na in yi shiru.

Saboda haka a watan Disamba 1965 an yarda mana, ni da iyali na mu bar Rumania.

Abu na karshe da na yi kafin in bar Rumania shi ne, na je kabarin hafsan soja wanda da ya bada umurni a kama ni a kuma gana mani azaba. Na sa fure a bisa kabarin. Ta wurin yin haka, na bada kaina ga kawo farin ciki da salamar Kiristi da nike da su ga 'yan kwaminis wadanda suke da yunwar Ruhu Maitsarki.

Na sani tsarin kwaminisanci, amma kuma ina son mutanen. Na sani zunubi, amma ina kaunar mutumin dake aikata zunubi. Ina kaunar 'yan kwaminis da dukkan zuciya ta. 'Yan kwaminis suna iya kashe Kirista, amma basu iya kashe kaunar da Kirista suke yiwa, har ma wadanda ke kashe su. Bani jin haushinsu ko kadan ko rena 'yan kwaminis ko masu bada azaba.



# BABI NA HUDU: FOUR

## CIN NASARA AKAN KWAMINISANCI DA KAUNAR RUHUN KRISTI

Yahudawa suna da wani labari da suke baiwa 'yayansu cewa,lokacin da Allah ya ceto kakanninsu daga kasar Masar. Masarawa suka hallaka cikin jan teku. Malaiku suka taya su wakokin nasara. Allah yace da malaikun, "Yahudawa mutane ne saboda haka suna iya yin murna game da tsira da suka yi. Amma daga gare ku ina sa ran Karin fahimta. Masarawa su ma ba halitta ta bane? Ban a kunarsu ne su ma? Yaya aka yi baku iya jin bakin cikin da nike yi akan abin da ya afka masu?

Lokacin da Joshua yake kusa da Jericho, ya daga idanu, ya duba,sai ya ga wani mutum tsaye kusa da shi, sai Joshua ya Zare takobi ya je wurin mutumin y ace, "Kana wajenmu ko kuwa kana wajen abokan gabarmu?" (Joshua 5:13). Idan da wanda Joshua ya gamu da shi mutum ne, da amsar da za ya ba shi ita ce, "Ina wajenku," ko, "Ina wajen abokan gabar ku." Ko kuwa. "Ba ruwa na." Wadannan sune amsoshin da mutum za ya iya badawa ga tambaya irin wannan. Amma dashike shi wanda Joshua ya gamu da shi daga wata duniyar ya fito, saboda haka sai ya tambaye shi yana bayan Israi'lawa ne ko kuwa abokan gabar Isra'ilawa? Ya ba shi amsa wadda ba ya zata ba, kuma mai wuyar fahimta, ya ce, "A'a." Menene wannan a'a take nufi? Ya fito daga duniyar da babu masu gaba da juna, amma sai fahimtar kowa da kome, kuma ana duban juna da tausayi da kauna.

Akwai mataki na dan adam, a wannan mataki, akwai kwaminisanci kuma dole ne a yaki wannan kwaminisanci. Har yanzu dai a wannan mataki dole a yaki 'yan kwaminis domin sune masu goyon bayan munanan ayyukan kwaminisanci. Amma Kirista sun wuce mutane kawai, su 'ya'yan Allah ne, wadanda suke da Ruhu Allah zaune cikinsu.

Saboda haka, azabar da na sha a kurkukun 'yan kwaminis bata sa ni kin jinin 'yan kwaminis ba. Allah ne ya halicce su. Yaya zan ki jininsu? Haka nan kuma ba zan yi abuta da su ba. Saboda suna gaba da kasancewar Allah. Ni ko ina kaunar Allah.

Idan da an tambaye ni, "kana wajen 'yan kwaminis ko kuwa baka wajensu?" Amsar da zan bayar zata zama da tsauri. Kwaminisanci shine babban abokin gaba dan-adam. Bana kaunar sa ko kadan kuma ina so in yi yaki da shi har sai an kawar da shi. Amma, a cikin ruhu, ina zaune a tsarkakan wurare na sama tare da Yesu. Ina zama a duniyar "a'a" inda, duk da wadannan mayan laifufuka da suke aikatawa, an fahimce su kuma ana kaunarsu; Duniya wadda take da malai'ku suna kokarin taimakon kowa ya kai ga gol na rayuwar mutum, wato ya zama kamar Kiristi. Saboda haka, manufa ta ita ce, yada bishara ga 'yan kwaminis, in basu labarin rai na har abada.

Kiristi, wanda yake Ubangijina yana kaunar 'yan kwaminis. Shi da kansa ya ce yana kaunar kowanne mutum kuma ya gwammace ya bar tumaki tasa'in da tara masu adalci daya bar guda daya ta bace. Manzanninsa da manyan malamai na Kiristiyaniti duk sun koyar da wannan kauna da yake yiwa duniya a cikin sunansa. St. Macary ya ce sai dai akwai wani mutum guda wanda yake jin ba za ya iya kaunatarsa ba, mutumin da ya fadi wannan ya tashi daga zama Kirista, saboda kaunar Ubangiji ta hada da kowa." St. Augustine ya koyar cewa, "Idan da dukkan mutane sun yi adalci kuma mutum guda ne kawai mai zunubi, duk da haka da Kiristi ya zo ya mutu akan wannan giciye saboda wannan mutum guda, saboda yana kaunar kowanne mutum." Koyarwar Kiristi a fili take. 'Yan kwaminis mutane ne kuma Kiristi yana kaunar su. Haka nan kuma kowanne mutum wanda yake da Kiristi a cikin zuciyarsa yana kaunar su. Muna kaunar mai zunubi ko dayake ba mu son zunubin nasa.




*Farkon tsarin na "kunttattatu Don Kristi" Krista na yammanci sun ji kadan ne game da wahalar Iyalansu cikin kuntattatun kasashe. Ikilisiyoyi da yawa cikin Yammanci sun ki su wallafa irin wadannan sadarwa*

Muna iya sanin kaunar Kiristi zuwa ga 'yan kwaminis ta wurin kaunarsu da muke yi.

Na ga Kiristoci a kurkuku 'yan kwaminis da sarkoki masu nauyi a kafafunsu, ana gana masu azaba da karfen da ya yi ja a wuta, ana zuba masu cikin cukali na gishiri kuma a hana su rowan sha, a bar su da yunwa, a yi masu bulala, a bar su cikin sanyi amma duk da haka suna addu'a da zuciya daya domin ceton 'yan kwaminis. Wannan ba yin mutum bane. Kaunar Kiristi ce wadda ke cikin zukatansu.

Daga baya, 'yan kwaminis wadanda suka gana mana azaba, su ma aka kawo su kurkukun a matsayin fursuna. A karkashin kwaminisanci, 'yan kwaminis, kuma har ma da yan kwaminis masu mulki ana saka su kurkuku bisa ga zargin abokan gabarsu yanzu da masu bada azaba da wadanda suka basu azabar sun hadu a kurkuku guda. Yayinda marasa bi suke nuna wa Kirista kiyyayya har suna dukansu, Kiristan suna kare kansu har ma a fuskar hadarin samun duka da zargin cewa suna da hadin baki da kwaminisanci. Na ga Kirista suna bayar da dan guntun burodin su (a lokacin guntun burodi daya ake bamu a mako) kuma da maganin da za ya ceci rayukansu ga 'yan kwaminis marasa lafiya kuma wadanda suke gana masu azaba a da kuma yanzu suka zama abokan zama a kurkukunsu.

Kalmomin Luliu Maniu, shugaban Rumania Kirista wanda ya mutu a kurkuku sune, "Idan aka hanbare gwamnatin kwaminis a kasar mu, wannan za ya zama aiki mafi tsarki da kowanne Kirista za ya fita bisa rariya ya kare, bakin ransa, 'yan kwaminis daga fushin jama'a wadanda suka gana wa azaba."

Kwanakin farko bayan tuba na, na ji kamar ba zan dade ba zan mutu. Idan ina tafiya a rariya sai in rika jin ciwo a zuciyata domin mutane da suke wucewa. Ina jin kamar an soka mani wuka cikin zuciyata saboda tunanin ko sun sami ceto ko kuwa babu. Idan wani memba na majami'armu ya yi zunubi, ni kan yi kuka da bakin ciki dominsa har tsawon awoyi. Marmarin kowanne mutum ya sami ceto yana zuciyata kuma har da marmarin ceton 'yan kwaminis

Lokacin muna tsare, ban iya yin addu'a fiye da yadda muke yi kafin a tsare mu ba. Muna cikin matsananciyar yunwa wadda tafi gaban misali, an sangarta hankalinmu har mun koma kamar sakarkaru. Mun zama kasusuwa kawai. Addu'ar Ubangiji ma ta yi mana tsawo. Ba mu da isashen karfin fadin ta. Addu'ar da nike iya yi kawai ita ce, "Yesu ina kaunarka" wannan nake ta maimaitawa.

Wata rana mai daraja, na sami amsa daga Yesu, ya ce, "kana kauna ta? Yanzu zan nuna maka yadda nake kaunarka." Nan take sai na ji wuta Ruhu tana ci a cikin zuciyata kamar rana. Almajiran nan na hanyar Imwasu suka ce zukatan su sun haskaka lokacin da Yesu ya yi Magana da su. Haka ya faru da ni. Na gane kaunar shi wanda ya bada ransa a bisa giciye dominmu duka. Irin wannan kauna bata ware 'yan kwaminis ba, kome munin zunubansu.

'Yan kwaminis sun aikata, kuma har yanzu suna aikata munanan abubuwa, amma kome yawan "ruwa ba za ya kashe wannan wutar kaunar Kiristi ba. Kauna tana da karfi kamar mutuwa. Kishi yana da mugunta kamar kabari "kamar yadda kabari yake matsawa yana son duk mai arziki da matalauci, yaro da tsoho, mutanen kowacce kabila, al'umma da kowacce irin akidar siyasa mutum yake, tsarkaka da masu laifi kaunar tana rungume kowa. Kaunar Kiristi ba zata taba karewa ba har sai ta ribato 'yan kwaminis su ma.

## Yadda zamu Iya yin Murna ko a Cikin kurkuku

Idan na duba baya shekara goma sha hudu da na yi a kurkuku wani lokaci ne na farin ciki. Sauran fursunoni, kai har ma da gandirebobi sukan yi mamakin yadda Kirista ke iya kasancewa da farin ciki acikin irin wannan mumunan hali. Ba a iya hana mu yin waka ba, an sha dukan mu saboda waka. Kirista suna rawa don murna a cikin kurkuku. Yaya zasu iya kasancewa da farin ciki a cikin wannan irin mumunan hali?

Lokacin ina kurkuku ina yawan yin nazarin kalmomin dá Yesu ya fada wa almajiransa ya ce, "Masu albarka ne idanun da suka ga abubuwa da kuka gani. A lokacin almajiran basu dade da dawowa daga Falasdinu ba a inda suka gamu da abubuwa masu ban tsoro. Falasdinu kasa ce da aka kuntata mata.

Koina mutane ne da ake tsananta masu. Almajiran sun gamu da rashin lafiya, da annoba, da yunwa, da bakin ciki. Suka shiga gidajen wadanda an kama mutanensu masu kishin kasarsu an kai kurkuku, sun bar iyayensu da matansu cikin bakin ciki. Ba abu mai kyau bane mutum zai gani idan ya duba.

Duk da haka Yesu ya ce, "Masu albarka ne idanun da suka ga abubuwa da kuka gani." Ya fadi wannan saboda ba wahalolin kawai suka gani ba, amma sun kuma ga mai ceton duka, wanda yake da abu mafi kyau, gol wanda kowanne dan-adam yake burin kaiwa. Karon farko, kadan daga cikin munanan tsutsotsin nan da suke rarafe a bisa ganyaye, suka fahimta cewa, bayan rayuwa ta wahala, sai rayuwa mai kyau ta zo, filfilo mai launuka, wanda yake iya tashi daga wannan fure zuwa wancan. Mun sami irin waanan farin ciki.

Kewaye da ni wasu Ayubobi ne, kwadansu daga cikinsu ma sun sha wahala fiye da Ayuba. Amma na san karshen labarin. Ayuba; yadda ya sami ninkin abubuwa da yake da su a da. Kewaye da ni akwai mutane kama da matalaucin nan La'azaru, cikin yunwa kuma babu mai kulawa da su. Amma a sani cewa mala'iku zasu dauke su duka zuwa kirjin Ibrahim. Na gan su kamar yadda zasu kasance nan gaba. Na ga rauwani mai daraja na tsarkaka wanda za a basu ranar gobe kiyama ga wani jarumin bangaskiya wanda ya galabaita kuma ga dauda saboda munin kurkukun da yake.

Amma duban mutane ta wannan fuskar ba kamar yadda suke a halin yanzu ba amma yadda zasu zama nan gaba na iya gane cewa a cikin masu tsanantawa masu bi kamar Saul na Tarsus wanda a gaba ya zama Manzo Bulus kuma wasu ma har sun rigaya sun zama haka. Akwai hafsoshin 'yan sandan asiri wadanda muka shaidawa baishara sun zama Kirista kuma suna jin dadin shan wahala a kurkuku bayan sun tuba sun zama na Kiristi.

A cikin masu tsaronmu wadanda suke yi mana bulala mun ga yiwuwar zasu iya zama kamar mai tsaron kurkuku na Filibi wanda ya yiwa Manzo Bulus bulala kuma daga baya ya zama Kirista. Muka sa rai cewa bada dadewa ba zasu tambaya, "Menene zamu yi domin mu tsira?" A cikin wadanda suke kalo suna yin ba'a lokacin da ake batawa Kirista jiki da kashi, ana daure su ga giciye, mun ga taro Golgotha wanda nan da nan suka buga kirji domin tsoron zunubin da suka yi.

A lokacin muna a kurkuku ne muka sami bege domin 'yan kwaminis, cewa zasu sami ceto lokacin da suka gane, suka tuba. A can ne kuma muka gane babban hakkinsu da ya rataya a wuyanmu. A lokacin da suke gana mana azaba ne muka koyi kaunarsu. Yawancin 'yan uwana duk 'yan kwaminis sun kashe su. A gidana ne kuma wanda ya kashe su ya karbi Yesu Kiristi. Kusan nan ne yafi dacewa gare shi ya tuba. Saboda haka a kurkukun yan kwaminis aka hafi tunanin aikin bishara ga 'yan kwaminis.

Allah yana duban abubuwa dabam da yadda muke dubansu kamar yadda muke ganin abubuwa dabam da yadda dabbobi suke gani. Bisa ga ganin mutum, a daure mutum a bisa giciye a kuma bata masa jiki da kashi wannan mumunan abu ne. Duk da haka Littafi Maitsarki ya kira wahalolin da jarumawan bangaskiya suke sha da cewa basu da tsanani kwarai. Mutum ya share shekaru goma ksha hudu, lokaci ne mai tsawo a wurin mu. Littafi Mai tsarki ya kira wannan dan karamin lokaci, "amma dan lokaci kadan, wanda yake bamu daraja mai yawa." Wannan yana bamu damar dauka cewa mugun aiki na 'yan kwaminis, wanda babu makawa a gare mu, kuma wanda ya zama dole ne mu yi yaki da kwaminisanci iyakar iyawa, duk wannan ba wani abu bane a idanun Allah, kamar yadda yake a idanun mu. Bakin mulkinsu wanda yanzu ya kai kimanin shekara hamsin, a gaban Allah, wanda shekara dubu ke kamar kwana daya, dan karamin lokaci ne na bata. Har yanzu suna da zarafin samun ceto.

Urushalima ta sama tana kama da uwa, kuma tana kauna kamar uwa. Ba a rufe kofofin sama ga 'yan kwaminis ba. Haka nan kuma ba a kashe haske dominsu ba. Suna iya tuba kama sauran mutane. Kuma dole ne mu yi kiran su zuwa ga tuba. Kauna kadai ce zata iya canja 'yan kwaminis (Kauna wadda dole ne ta rarrabe tsakanin amincewa da kwaminisanci, kamar yadda shugabannin Ikilisiya da yawa suke yi). Kiyayya tana makantarwa. Hitler mai gaba da kwaminisanci ne, amma a maimakon ya cinye su da yaki sai ya taimaka masu suka ci kashi daya bisa uku na duniya.

Cikin kauna muka tsara aikin mishanari a cikin 'yan kwaminis a lokacin muna cikin kurkuku. Muka farad a tunani akan shugabanni 'yan kwaminis.

Da kalamun wasu darektocin mishan basu karanci tarihin Ikilisiya ba sosai. Tayaya akaa ribato kasar Norway zuwa ga Kiristi? Ta wurin ribato Sarki Olaf. Da farko kasar Rasha ta sami bishara lokacin da sarkinta, Vladimir, ya karbi Kiristi. An ribato kasar Hungary ta wurin ribato sarkinta St. Stpehen. Haka kuma ya faru da Poland. A Afirka, lokacinda aka ribato sarki sai kabila ko al'ummar wurin su karba. Muka kafa kungiyar mishan wadda ta kunshi mutane dabam dabam wadanda, me yiwuwa ne Kirista ne nagari, amma ba masu fada a ji ba bisa ga matsayinsu, kuma basu iya canja abubuwa.

Dole ne mu ribato masu mulki da 'yan siyasa, da masu rike da tattalin arziki kasa, da masu ilimin kimiya da sauransu. Wadannan sune injiniyoyin rayukan jama'a. Idan aka ribato su, to an ribato mutanen da suke yiwa jagora ko kuwa magoya bayansu. Bisa ga fahimtar mu game da aikin mishan, kwaminisanci yana da wata faida wadda sauran akidodin siyasa basu da ita. Ikon kwaminisanci yana tasowa daga wuri guda daga santa.

Idan aka ribaci shugaban Amerika ya shiga addinin Mormonism, Amerika ba zata zama mai bin Mormon ba saboda shugabanta ya shiga. Amma idan shugaban kasar China (sin) ya tuba ya zama Kirista ko Breshnev na Rasha ko Ceasushesu duka kasar zata ji bishara.

Wadannan shugabanni suna da iko da kuma martaba sosai a idanun jama'arsu. Amma ana iya ribato shugaba dan kwaminis zuwa ga Kiristi? Hakika, domin ba shi da salama da kwanciyar hankali kamar mutanen da yake kuntatawa. Kusan dukkan 'yan kwaminis masu mulki a Rasha suna karewa a kurkuku ko kuma abokansu 'yan kwaminis su harbe su su mutu. Haka nan yake a China. Har ma ministocin harkokin cikin gida na wadannan kasashe, kamar su lagoda, lejov, Beria, wadanda kamar suke da dinbin iko a hannunsu haka suka kare kamar yadda masu adawa da juyin-juya hali suka kare, aka harbe su. Kwanannan aka yi waje da Stephenlin, ministan harkokin cikin gida na Tarayyar Rasha, da Rankovic, ministan harkokin cikin gida na Yugoslavia.




*Tsanani don Kristi an juya ta zuwa fiye da harsuna (70) sabain, wadanda a ciki an nuna wasu a nan.*

## TA YAYA ZAMU IYA KAIWA KWAMINISANCI HARI CIKIN RUHANIYA.

Mulkin kwaminisanci bay a dadadawa kowa har ma da masu cin ribarswa. Har ma masu cin ribarsa suna rawar jiki domin koyaushe motar 'yan sandan asiri tana iya nufowa wajensu ta tafi dasu zuwa kurkuku saboda rawar jami'iyarsu ta canja.

Na san shugabannin kwaminis da yawa. Suna da nauyin zuciya sosai. Yesu kadai zai iya basu hutawa.

A ribato shugabannin kwaminis zuwa ga Kiristi na nufin a ceci duniya daga hallaka da makamin nukiliya, a ceci mutane daga ynwa saboda kusan duk kudaden kasashen kwaminis suna tafiya wajen makaman yaki. Ribato masu mulki 'yan kwaminis na nufin kawo karshen zaman dardar da duniya take ciki. Ribato shugabanni 'yan kwaminis na nufin cika Kiristi da Mala'iku da murna. Yana iya zama nasarar Ikilisiya. Dukkan wuraren da mishanari suka yi aiki tukuru, kasashe kamar su new Guinea, zasu bi cikin sauki idan shugaba nin kwaminis suka karbi Kirisiti domin wannan za ya ba Kristiyaniti wani sabon karfin gwiwa da mutunci.

Na san wasu 'yan kwaminis wadanda suka tuba suka bi Kiristi. Ni kaina da tsagera ne wajen karyata kasancewa Allah a lokacin ina matashi. Masu musun kasancewar Allah da kuma 'yan kwaminis idan suka tuba sun ba kaunar Kiristi sosai, saboda sun yi zunubi da yawa.

Ana bukatar yin tunani da kyau akan aikin mishanari kafin a fara. Bisa ga al'amarin ceto dukkan mutane daya ne babu fifiko; bisa ga tsarin aikin mishanari ba daya bane. Ya fi muhimmanci ka ribato mutum mai fada-a-ji acikin jama'a zuwa ga Kiristi wanda daga baya zai zama sanadin kawo dubban mutane, da ka yi wa wani bakauye a cikin kunkurmin daji wa'azi kana tabbatar masa da samun ceto dominsa shi kadai kawai. Saboda haka Yesu baya zabi ya rufe aikinsa na yawon wa'azi a duniya a wani karamin kauye ba,

amma a birnin Urushalima, hedkwatar addini ta wancan zamani. Saboda wannan dalili ne kuma Bulus ya yi iyakar kokarinsa ya isa birnin Roma.

Littafi Maitsarki ya fada mana, "Zuriyar mace za ya kuje kan macijin." Muna yi wa macijin cakulkuli ne a ciki, muna sa shi dariya. Kan macijin yana tasakanin Moscow Depking, ba a Tunisiya ko Madagascar ba. Dole duniya kwaminis ta zama babba abin damuwa Ikilisiya da kuma darektocin kungiyoyin mishan da kuma kowannne Kirista mai tunani.

Dole mu bar ayukanmu na yau da gobe. "La'ananne shi wanda yake yin aikin Ubangiji da ha'inci," haka maganar Allah ta fada. Dole ne Ikilisiya ta kaiwa kwaminisanci hari.

Ana iya cin nasara a yaki ta wurin kai hari kawai ba ta wurin jan dammarar kare kai ba kawai. Game da kwaminisanci Ikilisiya ta yi ta hasarar kasashe ga kwaminisanci.

Dole Ikilisiya baki daya ta canja nan da nan. Wata Zabura ta ce Allah ya kakkarya shingen karfe. Labulen karfe karamin alhaki ne a wurin sa.

Ikilisiya ta farko ta yi karfi a asirce kuma bada amincewar dokar gwamnatin zamanin su ba kuma ta yi nasara. Dole ne muma mu koyi yin aiki a irin wannan hali da dabarar aiki.

Ban taba fahimtar abin da yasa aka kira mutane da yawa a zamanin Sabon Alkawari da wasu sunaye dabam da sunayensu na asali ba, misali Siman ana kiransa Niger, Yohanna ana kiransa Markus da

sauransu, sai zuwan lokacin kwaminisanci. Yanzu a cikin aikinmu a kasashen kwaminis muna amfani da sunayen asiri.

Da ban gane abin da yasa Yesu, lokacin da yake so ya ci abincin karshe, ya bada adireshin inda za a shirya masa ba, amma ya ce, "Ku shiga cikin gari ku nemi mutumin dake dauke da tulu." Yanzu na gane. Mu ma muna bada alamu ta asiri na gane juna cikin aikin Ikilisiya ta karkashin kasa.

Idan mun yarda mu yi aiki kamar haka mu komo da dabarun aiki irin na Kiristocin farko muna iya yin aiki da kyau kdomin Kirista a kasashen kwaminis.

Amma lokacin da na hadu da wasu shugabannin Ikilisiya na kasashen yamma, a maimakon su nuna kauna zuwa ga 'yan kwaminis, wadda, da tuni ta kawo kafa aikin mishanari a kasasahen kwaminis, sai na sani cewa tsarinsu yana goyon bayan kwaminisanci saboda basu nuna tausayi irin na Ba samariyen nan mai kirki ga batattun rayukan gidan Karl Marx.

Mutum baya gaskantawa da abin da ya haddace game da bangaskiyarsa, amma abubuwan da yake a shirye ya mutu dominsu.

Kiristoci na Ikilisiya ta karkashin kasa sun tabbatar da cewa a shirye suke su mutu saboda imani da suka yi da Yesu. Yanzu na cigaba da yi aikin da za ya iya jawo a sake daure ni a kasar kwaminis, sabuwar azaba kenan da kuma mutuwa saboda ina jagorancin aikin bishara gaa kasashen kwaminis a asirce, ina daukarwa kaina dukkan hadarin dake tattaare da aikin. Na yi imani da abubuwa da na rubuta.

Ina da 'yancin tambayar, shugabannin Ikilisiya na Amerika wadanda suke abuta da kwaminisanci za su shirya su mutu domin wannan imani nasu? Wanene ya hana su bar manyan matsayin da suke a kasashen yamma su zama fastocin da gwamnatocin kwaminis suke yarda da su a kasashen gabas suke yarda da su a kasashen gabas su yi ta ba kwaminis hadin kai a can? Tabbacin irin wannan bangaskiya har yanzu shugabannin Ikilisiya na kasashen yamma basu tabbatar da wannan bangaskiyar ba.

Dan adam ya fara kago kalmomi domin samun biyan bukatar fahimtar juna wajen farauta, kamun kifi da kuma daga baya wajen yin abubuwa da uka zama wajibi wajen rayuwa da kuma bayyana tunanin mutum game da dan uwansa. Babu wasu kalmomi na dan adam da ke iya bada wadataccen bayani game da mu'ujuzai na Allah da kuma girman rayuwar tsarki.





*Pastor Wurmbrand ya tube rigarsa yayinda yake shaida a gaban Haddaden Tarayyar Jihohin (Amerika)? Yana nuna masu zanen tabon tsanani. Sane da harsuna dabam dabam, ya sa a jarida cikin yaron Rasha (Russia) karya da aka buga game da Ikilisiya.*

Haka nan kuma babu wasu kalmomin da zasu iya bayyana zurfin mugunta da rashin imanin shaidan. Kana da kalmomin da zaka iya bayyana yadda mutumin da 'yan Nazi ke gab da jefa shi cikin tanderu na wuta yake ji a ransa, ko kuwa ya ga an jefa dansa cikin tanderun wuta?

Saboda haka babu amfani mutum ya yi kokarin bayyana wahalar da Kirista suka sha kuma har yanzu suke sha a karkashin yan kwaminis.

Na zauna a kurkuku tare da lucretin Patrascanu, mutumin da ya kawo mulkin kwaminisanci a Rumania. Abokansa suka saka masaa da sa shi a kurkuku. Ko dayake lafiyarsa lau, suka sa shi a asibitin tababbu har shi ma ya haukace. Haka suka yiwa Anna Pauker, Sakataren kasa na da. Wani lokaci ana yiwa Kirista irin wannan hukumci. Sai a sa lantarki ya kashe masu jiki. Akan sa masu wata riga wadda ba zama ba tafiya.

Duniya ta razana da abin dake faruwa a titinan kasa China. A idanun kowa jami'an tsaro wadanda ake kira Red Guards suke Gallazawa mutane. Yanzu ka yi kokarin sifantawa a zuciyarka ko kasashen abin dake faruwa da wasu Kirista a kurkuku a China, inda babu mai gani.

Labarin da aka samu na karshe shi ne, wani sanannen marubuci Kirista da wasu Kirista, wadanda suka ki su yi musun Yesu an yanke masu kunnuwa da harsuna da kuma kafafu.

Amma abubuwa da suka fi muni wadanda 'yan kwaminis ke yi basu ne bada azaba da kuma kashe jikkunan mutane kawai ba. Suna sangartar da zukatan mutane su sa wa zukatan yara da matasa dafi. Suna sa mutanensu shugabancin Ikilisiyoyi; Su shugabababanci Kirtista kuma su lalata Ikilisiyoyin. Suna koya wa matasa kada su bada gaskiya ga Allah da Yesu Kiristi kuma su yi gaba da wadannan sunaye.

Da wadanne kalmomi ne zamu iya bayyana wannan abin bakin ciki na jarumawan Kiristi, wadanda idan sun dawo gida, bayan sun yi shekaru a kurkuku, sai 'ya'yansu su rika yi masu kallon reni, wadanda a lokacin sun rigaya sun zama 'yan gani kashenin masu musun Allah?

Yawancin wannan littafi ba da tauwada aka rubuta shi ba, amma da jini.

Yawancin wannan littafi ba da tauwada aka rubuta shi ba, amma da jini.






*Kamar memba na Ikilisiya na kaskashin kas wanda ya tsira ya kuma kubuta, Ina kawo maku sako, da rook,Roko daga yanuwana da na bari a baya. Na fada maku bukatan hamzarin kawo labarin Kristi ga duniyar komunis da wasu kuntattatun kasashe da kuma hamzarin taimako ga Iyalan Krista kuntattatu. Pastor Wurmbrand yayi amfani da kowale dama ya kuma fada wa kungiyoyin addinai da taron yan siyasa, da karfafa Yammancin duniya kada su kyale wadanda suke "Iyalin masu bangaskiya".*

*Galatiyawa 6:10.*

Sai dai a zamanin Daniel ne, samarin nan uku da aka sa a tanderun wuta, bayan an fitto da su daga ciki, basu ko yi warin hayaki ba, haka Kiristocin da suka je kurkukun kwaminis basu warin jin haushin 'yan kwaminis.

Idan ka mutsuke fure da kafarka, sakamakon da zaka samu shi ne kamshin wannan fure. Haka nan yake ga Kiristoci wadanda 'yan kwaminis suka ganawa azaba, suka sakawa masu gallaza masu da nuna masu kauna. Mun kawo da yawa daga cikin masu tsaronmu zuwa ga Kiristi, saboda marmarin da ya cika zukatanmu shi ne mun ba 'yan kwaminis, wadanda suka gana mana wahala, abu mafi kyau da muke da shi, ceto wanda ke zuwa daga Ubangijinmu Yesu Kiristi.

Ban sami dama, irin wadda yan'uwana cikin bangaskiya suka samu ba ta mutuwa saboda Kiristi a cikin kurkuku. An sake ni kuma har ma ina iya fitowa daga kasar Rumania zuwa kasashen yamma. Kuma a nan kasashen yamma na iske yawancin shugabannin Ikilisiya ra'ayinsu akasin ra'ayi mafi rinjaye a Ikilisiyar karkashin kasa wadda ke kasashen kwaminis ne. Kirista da dama a yammacin duniya basu kaunar 'yan kwaminis. Tabbatar hakan shine ba su yin kome domin ceton wadanda ke a kasashen 'yan kwaminis. Suna da kungiyoyin mishan zuwa ga Yaudawa, Musulmi da masu addinin Buddah. Suna da kungiyoyin Mishan masu neman shawo kan Kirista su fita daga wannan darika su shiga waccan. Amma basu da wata kungiyar Mishan wadda zata kai bishara ga 'yan kwaminis. Ba su kaunar su. In ba haka ba da tunani sun kafa kungiyar Mishan domin su, kamar yadda Carey ya yi saboda kaunar indiyawa kuma Hudson Taylor ya yi da mutanen China. Amma rashin kaunar ma bai isa ba da rashin yin wani abu domin ribato su zuwa ga Kiristi amma ta wurin hadin baki, da nuna rashin kulawa, wasu shugabannin Ikilisiyoyi na yamma sun kara wa 'yan kwaminis kwarin gwiwa a cikin makircin su. Sun taimakawa 'yan kwaminis su yi katsalandan cikin Ikiliusiyoyin yammacin duniya kuma sun kwaci shugabancin Ikilisiyoyi da kuma kasashe cikin duniya.

Suna sa Kiristoci basu farka da hadarin kwaminisanci. Ba rashin kaunar 'yan kwaminis da rashin yin wani abu domin ribato su zuwa ga Kiristi (bisa hujjar wai ba a bar su su yi haka ba, sai ka ce Kiristan farko sun nemi izinin Nero kafin su yada bishara) kawai ba, basu ma kaunar tumakinsu. Saboda idan ba mu ribato 'yan kwaminis zuwa ga Kiristi ba, zasu ci kasashen yamma kuma su tumbuke Kiristiyaniti anan ma.

## ANA YIN WATSI DA DARASIN DA TARIHI KE KOYARWA.

A karnin farko, Kiristiyaniti ya yadu a arewacin nahiyar Afirka. Daga can ne rikakkun masu wa'azi kamar su St. Augustine da St. Cyprian da St. Athanasius da kuma Tertullian suka fito. Kiristocin arewacin Afirka suka ki kulawa da wani abu guda, shine, su ribato musulmi zuwa ga Kiristi. Sakamakon wannan shi ne, Musulmi suka mamaye arewacin Afirka kuma suka tumbuke Kiristiyaniti. Har zuwa yanzu arewacin Afirka ta Musulmi ce kuma Mishanari Kirista suna kiran yankin, "yankin mutanen da ba su ribato.

Bari mu koyi wani abu daga tarihi.

A lokacin canji a duniya, marmarin kawo canji a addini na Huss, Luther, da Calvin ya zo daidai da marmarin mutanen Turai na kawar da bakin mulki na Papa Roma. Haka nan a yau, marmarin Ikilisiyar karkashin kasa game da yada bishara ga 'yan kwaminis da kuma wadanda 'yan kwaminis din suke kuntatawa ya yi daidai da marmarin mutane masu 'yanci na cigaba da kasancewa cikin 'yanci.

Babu wani iko na siyasa wanda za ya iya kawar da kwaminisanci.

'Yan kwaminis suna da karfin nukiliya, kuma a kai masu hari da karfin
soja na nufin sabon yaki da mutane miliyan dari wadanda ka karkashin
Su.

. Kuma an rigaya an cusawa shugabannin kasashen yamma tsoro har basu ma marmarin hambare shugabannin kwaminis. Suna yawan cewa, suna fata shaye-shaye kwaya, kingiyoyin 'yan iska, ciwon sankara da ciwon tarin fuka su kawu, amma ba kwaminisanci wanda yake hallaka mutane fiye da wadannan cututtuka ba.

Wani marubuci dan kasar Rasha mai suna Ilya Ehrenburg, yace, a duk tsawon rayuwar Stalin baya kome sai rubuta sunayen salihan mutane da za ya gallazawa ko ya kashe, sai dai ba ya yi tsawancin ran da za ya iya gama aikin ba. Kruschev ya fadi, a babban taron jami'iyar kwaminis na ashirin, "Stalin ya hallakar da dubban kwamitin jami'yar kwaminis su dari da talatin da tara da aka zaba a babban taron jami'iya na goma sha bakwai, aka kama tasa'in da tara-wato kashi saba'in cikin dari na 'yan kwamitin aka harbe su har lahira."

Yanzu ka yi hasashen abin da ya yi wa Kirista.

Kruschev ya raba gari da Stalin, amma ya cigaba ya aikata abin da Stalin ya yi. Tun daga 1959, an rufe rabin majami'un da suka rage a bude a Tarayyar Rasha.

A kasar China akwai sabon yunkuri na halin dabbanci wanda har yafi abin da Stalin ya yi muni. An rufe dukkan majami'u kwata-kwata. A Rasha da Rumania ana ta kama masu bi. (Mun sami labari da dumi-duminsa ana ta kama Kirista a Rasha).

Ta wurin azaba da yaudara a kasashe masu mutane biliyan guda ana sa matasa suna kiyayya da duk wani abu daga kasashen yamma, musamman Kiristiyaniti.

Ba wani bakon abu bane ka ga jami'an gwamnati sun tsaya a gaban majami'a suna tare yara kada su je majami'a. Idan suka ga yara suna so su shiga majami'a sai su kama su su yi masu duka, su kore su. Ana horon wadanda zasu lalata Kiristiyaniti na kasashen yamma.

Akwai iko guda daya tal wanda za ya iya kawar da kwaminisanci. Shi ne ikon da ya sa Kiristiyaniti ya maye gurbin arnanci na daular Roma.Wannan shi ne ikon bishsara, wanda Ikilisiyar karkashin kasa take wakilta a kasashen kwaminis.

Taimakawa wannan Ikilisiya ta cigaba ba domin amfanin Kirista masu 'yanci kawai ba ne, amma har da akidar gwamnatoci masu - kiyaya
'yancin dan adam.

Ikilisiyar karkashin kasa ta rigaya ta ribato shugabannin kwaminis masu mulki zuwa ga Kiristi. Furaiministan Rumania Gheorghin Dej ya tuba kafin ya mutu bayan ya furta zunubinsa kuma ya canja rayuwarsa ta zunubi. A kasashen kwaminis akwai 'yan kwaminis jami'an gwamnati wadanda ke bin Yesu Kiristi a boye. Wannan na iya yaduwa. Daga nan ne zamu iya sa ran samun canji a akidojin wasu gwamnatocin kwaminis ba canje canje irin na Tito daa Gomulka ba, wanda bayansa sai bakin mulkin kama karya na jami'iyar arnanci ya cigaba amma canji wanda za a juyo zuwa ga Kiristiyaniti da 'yancin dan adam.

Yanzu akwai zarafi na musamman domin wannan.

'Yan kwaminis, wadanda yawancin lokaci suna bin akidarsu da zuciya daya kamar yadda Kirista suke rike imaninsu, yanzu haka suna ratsa mawuyacin hali.

Sun bada gaskiya cewa lallai kwaminisanci za ya kawo 'yan uwantaka a tsakamin al'umman duniya. Yanzu sun ga cewa a maimakon haka sai kasashen kwaminis suke fada da juna kamar karnuka.

Da sun gaskanta cewa kwaminisanci za ya kawo wata aljanar duniya akasin aljanar sama wadda suke dauka jitajita ce kawai. Yanzu ga shi mutanensu suna cikin yunwa. Dole sai an sayo alkama daga kasashe masu akidar jarihujja.

Da 'yan kwaminis sun gaskanta da shugabanninsu. Yanzu sun karanta a cikin jaridunsu cewa Stalin mai kisan ka ne kuma Kruschev dakiki ne.

Haka kuma da mutanen da suke ba daukaka kamar su Gero, Anna Pauker, Rankovic da sauransu. Yanzu 'yan kwaminis sun daina gaskantawa cewa wai shugabanninsu basu kuskure. Suna kama da 'yan kwaminis, ana iya cike wannan kwalogo da Kiristi kadai. Zuciyar mutum tana da son neman Allah. Akwai wani gibi na ruhaniya a cikin kowanne mutum har sai Yesu Kiristi ya cike wannan gibi. Wannan haka yake ga 'yan kwaminis. A cikin bishara akwai iko na kauna wanda za ya iya jan hankalinsu su ma. Na ga wannan ya faru. Na sani yana yiwuwa

Kirista wadanda 'yan kwaminis suka yiwa ba'a da azaba sun gafarta masu kuma sun manta da abin da aka yi masu da wanda ak yiwa iyalansu. Suna yin iyakar kokarinsu su taimakawa 'yan kwaminis su sami Kiristi. Domin su iya yin wannan aiki sosai, suna bukatar taimakon mu.

Ba domin wannan kawai ba don kaunar Kirista domin kowa da kowa ne a duniya.

## GA KIRISTA, BABU BAMBANCI:

Yesu ya ce, rana ta Allah tana haskakawa bisa nagari da mugu. Haka nan kuma kaunar Kirista take.

Shugabannin Kirista dake kasashen yamma wadanda suke abuta da 'yan kwaminis suna kare abin da suke yi da cewa Yesu ya koya mana cewa dole ne mu yi kaunar har masu gaba damu. Amma Yesu ba ya taba koyarwa cewa masu gaba damu kawai zamu nuna wa kauna mu manta da 'yan uwanmu ba, babu.

Suna nuna kaunarsu ta wurin jawowa da kuma cin abinci da mutanen da hannuwansu cike suke da jinin Kirista, ba su nuna babban ci game da albishiri na Kiristi. Amma kuma wadanda 'yan kwaminis din suke kuntatawa an manta da su. Wannan ba kauna ba ce.

Ikilisiyoyi masu ra'ayin bishara da 'yan Katolik na kasashen yammacin Jamus sun bada dalar Amerika miliyan 125 ga masu fama da yunwa a cikin shekara bakwai da suka wuce. Kiristocin Amerika sun bada abin da yafi haka.

Akwai mutane masu jin yunwa da yawa amma basu iya tunanin babu wadanda suka fi jarumawa Kiristi yunwa ko bukatar taimakon Kiristoci masu 'yancin walwala. Idan Ikilisiyoyin Jamus, da Britaniya da Amerika da Scandinvia zasu tara kudi masu yawa domin agaji, ya kamata su ba duk wanda ke cikin bukata, amma da farko su fara ba Kiristocin da ake gana masu azaba saboda Kiristi.

## Haka abin ke faruwa yanzu?

Kungiyar Kiristoci ce ta biya kudi domin fanso ni. Wannan ya nuna cewa ana iya fanso Krista. Duk da haka, ni kadai ne wanda Kirista
daga wata kasa suka fanso. Kuma fanso ni za ya zama zargi ga
kungiyoyin Kiristoci na kasashen yamma akan rashin kulawa su cika aikinsu a wasu fannonin.

Kiristocin farko sun tambayi kansu ko sabuwar Ikilisiyar ta Yahudawa ce kawai, ko har da al'ummai. Sun sami amsar wannan tambaya. Ta wata hanyar wannan matsala ta sake bullowa a cikin karni na ashirin. Kiristiyaniti ba na mutanen yamma ba ne su kadai. Kiristi ba na mutanen Amerika bane su kadai ko na Ingila ko kuwa sauran mutanen kasashe masu akidar dimokaradiya kawai. Lokacin da aka giciye shi, an mike hannunsa guda zuwa yamma kuma guda wajen gabas. Ya nuna yana so ya zama sarki ba na Yahudawa kawai ba, amma har da al'ummai, kuma sarkin 'yan kwaminis, ba na mutanen yammacin duniya ba kawai. Yesu ya ce, "Ku tafi cikin duniya duka kuma ku yi wa'azin bishara ga dukkan halittu."

Ya bada jininsa domin duka kuma duka, su ji su kuma bada gaskiya ga bisharar Kiristi.

Abin da ya karfafa mu yin wa'azin bishara ga kasashen kwaminis shi ne cewa a can, wadanda suka zama Krista suna cike da kauna da kuma niya. Ban taba haduwa da raggon Kirista dan Rasha ba. Matasa 'yan kwaminis suna iya zama fitattun almajiran Kiristi.

Kiristi yana kaunar 'yan kwaminis kuma yana so ya 'yantar da su daga kwaminisanci, kamar yanda yake kaunar dukkan masu zunubi kuma yana so ya 'yantar da su daga zunubi. Wasu shugabannin Ikilisiya na kasashen yamma, a maimakon nuna wannan hali, sai suna nuna wani hali mai nuna amincewa da kwaminisanci. Suna gafarta zunubi, suna taimakawa kwaminisanci ya yi nasara kuma, ta wurin yin haka, suna hana 'yan kwaminis da wadanda 'yan kwaminis ke ganawa azaba tuba su sami ceto.

## ABIN DA NA GANO LOKACIN DA AKA SAKO NI

Lokacin da aka sako ni daga kurkuku, na koma wajen iyali na, Uwar gida na ta tambaye ni abin da nake tunanin yi nan gaba. Na amsa na ce, abin da na sa gaba na shi ne zan kebe kaina domin ruhaniya" Uwar gidana ta amsa cewa ita ma abin da take tunani ke nan.

Lokacin ina saurayi, ina da kwazo sosai amma zaman kurkuku, shekaru da dama a tsare ya canja ni zuwa mutum mai tunani da kuma nazari. Duk wata kuruciya da wani hayaki dake tasowa a zuciya duk sun kawu. Ban damu da kwaminisanci ba. Har ma bani kulawa da shi. Ango na sama ya rungume ni. Na yi addu'a domin wadanda suka gallaza mani kuma ina iya kaunarsu da dukkan zuciyata.

Na kusan fitar da zuciya cewa za a taba saki na daga kurkuku, amma lokacin da tunani ya fara fado mani lokaci zuwa lokaci akan abin da zan yi idan misali aka sake ni, ko da yaushe sai in yanke cewa wani wuri zan je in kebe kuma in ci gaba da zumunta da ango na na sama.

Allah shi ne gaskiya. Littafi Maitsarki shi ne gaskiyar game da gaskiya. Tauhidi shine gaskiya game da gaskiya. Kuma Kirsta suna zaune cikin wannan gaskiya game da gaskiya, kuma saboda su da basu da gaskiyar, ake barinsu da yunwa ana dukansu kuma a kawar da hankalinsu, su manta da tauhidi da kuma Littafi Maisarki.

Mun manta da gaskiyar game da gaskiya kuma saboda haka muka zauna cikin gaskiya. An rubuta, "Dan mutum za ya zo cikin sa'ar da baku zata ba kuma a ranar da baku sani ba." Ba mu iya yin tunani kuma. A cikin sa'o'in da suka fi muni da dufu na azaba. Dan mutum ya zo wurin mu, ya sa bangayen kurkuku suka haskaka kamar azurfa kuma ya cika dokunan kurkukun da haske. Ba wani wuri da nisa, inda masu ba mu azaba suke kisanmu a cikin jiki. Amma ruhu ya yi murna cikin Ubangiji. Ba zamu hakura da wannan murna ba a irin wannan wuri mai kamar fadar sarki.




*Tun sakensa, Pastor Wurmbrand yayi Magana a dubban sujadai Ikilisiya da konfrans masu yawa. Iyalin muryar kuntattatu ta mishan ta sami hadawa yanzu ta wurin hadin kan Krista na kasa da kasa. A kasa an nuna taron tunda farko*



In yaki wani ko wani abu? Babu abin da ya fita zuciyata kamar wannan. Bani fatar in yi wani yaki ko da ina da hujjar da ta isa ta sa in yi. Na fi marmarin in gina haikalin Kiristi wato mutunen da suka yi imani da shi. Da sa ran zan yi zama shiru ina nazarin maganar Allah na baro kurkuku. Na fuskanci wasu kwaminisanci kamar su azaba, a lokacin ina kurkuku. Na sadu da rikakkun masu wa'azi da fastoci na Ikilisiyoyi dabam dabam, kuma har ma da bishop-bishop, wadanda suka furta da bakinsu cewa da sune ke ba 'yan sandan

Asiri labarin membobinsu. Na tambaye su ko sun shirya barin wannan mugun hali na bayar da membobinsu ko da za a daure su? Dukkansu suka amsa "a'a" kuma suka bayyana cewa ba tsoron abin da zai same su ke hana su ba. Sun fada mani wani sabon abu da ya bullo a cikin Ikilisiyoyi wanda a da babu kafin a daure ni shi ne idan suka ki su rika ba 'yan sanda sirin 'yan uwansu, to za a rufe majami'arsu.



*Da alamar zanen kunchi a wuyarsa, baya da kirjinsa, Pastor Wurmbrand ya ganeda wahala da yawancin Krista a Afrika suna jimrewa a kalkashin tsanani. Iyalin mishan ta (VOM) Muryan kuntattatu ta aika da taimakonsu zuwa Afrika tun daga shekaru ta 1960.*

A kowanne gari, akwai wakilin gwamnati mai kula da adini, mutumin zai kasance dan sandan asiri ne na 'yan kwaminis. Yana da ikon ya kira kowanne firis ko fasto a duk lokacin da ya ga dama kuma ya tambaye shi, su wanene suka zo sujada a majami'arsa, su wanene suke cin jibin Ubangiji babu fashi, su wannene suke samo masu tuba, menene mutane suke furtawa, da sauran su. Idan baka bada amsa ba, sai a kore ka a sa wani faston a maimakon ka wanda za ya fadi fiye da abin da ka yi. Inda wakilin gwamnati ba shi da mutumin da za ya cike gurbin ka wanda za ya biya masa bukata (wanda ba ya faye faruwa ba) sai kawai ya rufe majami'ar.

Na ji yaran Kiristan da aka daure suna furta yadda aka tilasta masu su bada bayani game da gidajen da aka yi masu alheri. Ko kuma a yi masu barazanar hana su cigaba da karatu.

Na je taron Baftis wanda aka yi a karkashin tutar 'yan kwaminis: 'yan kwaminis ne suka nuna wadanda za a zaba a matsayin shugabannin Ikilisiyar.

Yanzu na sani cewa shugabannin kowacce Ikilisiya dake karkashin ikon gwaamnati mutanen da jami'iyar kwaminis ta sa aka zaba ne. Daga nan na gane ina ganin la'ana a wurare masu tsarki wadda Yesu ya fada.

Ko da yaushe ba a rasa fastoci da masu wa'azi nagari da munana. Amma yanzu, karon farko cikin tarihin Ikilisiya, babban kwamiti na jama'iyar masu musun kasancewar Allah, wadda ta yi dammarar kawar da Ikilisiya, itace ke zartas da ko wanene za ya shugabanci Ikilisiya.

Ya shugabanci Ikilisiya saboda me? Hakika domin ya taimaka masu su tumbuke addinin Kiristiyaniti. Lenin ya rubuta, "Kowanne tunani ko ra'ayi na addini ko Allah, ko da ma yin wasa da zancen cewa akwai Allah mugun abu ne wanda ba a yarda ma a ambata ba. Duk miliyoyin zunuban da ake aikatawa basu kai hadarin ambata cewa akwai Allah ba.

Dukkan jami'iyun kwaminis dake a dukan tarayyar Rasha masu bin akidar Lenin ne. A gare su addini har yafi ciwon kansa (sankara) da tarin fuka ko tunjere muni. Kuma sune ke zaben wanda za ya shugabanci addini. Kuma da sune shugabanni Ikilisiyoyin dake karkashin ikon gwamnati suke hada kai.

Na ga yadda ake gurbata zukatan yara da matasa da ra'ayin da ke cewa babu Allah, Ikilisiyoyin dake karkashin ikon gwamnati basu da ikon yin kokarin hanawa. Duk fadin babban birnin kasar mu Bucharest babu Ikilisiyar da take yin sonde skul domin yaranta. Ana renon yaran Kirista a makarantar kiyayya.

Daga nan kuma ganin dukkan wannan sai na sani kwami nisanci kamar yadda na tsane shi lokacin da suke gallaza mani. Na tsani kwaminisanci ba don saboda abin da ya sa aka yi mani ba, amma saboda abu mara kyau da ya yiwa daukakar Allah da suna Yesu Kiristi da kuma sa rayukan miliyoyin mutane karkashin bautar shaidan.

Talakawa daga ko'ina cikin kasar suka zo domin su gani kuma su fada mani yadda ake gudanar da tsarin gandu. Suka ce yanzu suna zama bayi mayunwata a gonaki da lambunan da suke nasu a da. Ba su da burodi. "Yayansu basu da madarar da zasu sha, babu 'yayan itace kuma wannan yana faruwa kasar da take da wadata kamar ta kasar kan'ana ta da.

Wani dan uwa cikin Kiristi ya furta a gabana cewa gwamnatin 'yan kwaminis ta maida su barayi da makaryata. Saboda tsananin yunwa dole su yi sata daga abin da yake nasu a da, amma yanzu ya
zaama na gandu. Daga nan su ma dole su yi karya domin su rufe satar da suka yi.
Ma'aikatan sun fada mani irin azaban da ake gallaza masu a ma'aikatun da suke aiki da kuma game da zalumcin da ake yi masu wanda ba a taba yin mafarkinsa a kasashe masu ra'ayin jari hujja ba. Ma'aikatan basu da izinin yin yajin aiki. Dole masu ilimi suka kai wani matsayi da suka dauka cewa babu Allah.



*Shekaru 70 Bible ya zama haramu da littattafan Krista ba a yarda su shiga kasar Soviet Union da wasu kasashe komunis. Krista da yawa sun juyo ga buga Bisharu da wasu kayayaki cikin ramumuka da wasu wurare da an yi masu boyayyun kofoffi. Ana ci gaba da yin irin wadanan ayuka a China (kamar a kasa) yau da gabas ta Tsakiya da wasu kasashe da ba a yarda da Bible a fili.*



Dukkan rayuwa da tunani na, kashi daya bisa uku na mutanen duniya an lalata su.

'yan mata suka kawo kukan an kiraye su' su shiga kungiyar matasan kwaminis kuma an yi masu gargadi da barazana saboda sun sumbaci wani yaro kirista. Kuma aka basu sunan wani wanda shi ne za su yi wa sumba.

## Kome dai ga muni ga karya da rufarufa.

Daga nan na sadu da mayakan ikilisyar karkashin kasa abokan aikina na tuntuni wadansun su ba a taba kama su ba, da kuma wasu da suke shiga cikin gwagwarmayar bayan an sako su daga wakafi ko kurkuku. Suka gayyace ni in sake yi a asirce a inda suke raira waka daga littafin waka da aka rubuta da hannu.

Na tuna da rikakken mai wa'azin nan St. Anthony. Ya yi shekara talatin cikin Hamada. Ya hakura da duniyar baki daya yana rayuwa ta azumi da addua kawai. Amma lokacin da ya ji ana jayayya a tsakanin St.Athanasius da Arius akan Allahntakar kiristi, sai ya baro waccan rayuwa da yake yi ta zaman kebe ya zo Iskandariya domin ya taimaka gaskiya ta yi nasara. Na tuna da St. Bernard de clairvaux. Shi "monk" ne [wato wanda ya kebe kansa domin bautar Allah] can a bisa duwatsu. Amma da ya ji zancen sakarcin da masu yakin addini suka yi, batun cewa kirista suna kashe Larabawa da kuma Yahudawa da 'yan uwansu cikin bangaskiya na wani addinin, domin su kwato kabarin da babu komi ciki. Sai ya yi wa'azin hana wadannan yake yake.

Sai na yanke shawarar yin abin da ake bukatar kowanne kirista ya yi: ya bi gurbin kiristi, da na manzo Bulus da kuma rikakkun tsarkaka, in kawarda tunanin ritaya, in shiga gwagwarmayar.

Buwa tare da ban girma a New Delhi, da Genenva, da sauran taaruruka. A can aka tabbaatar masu cewa kowa yana da 'yancin addini a Rasha.

Wannan karyar ta sa wani shugaba na World Council of Churches ya yiwa bishop, nadin 'yan kwaminis, sumba. Daga nan suka yi masu liyafa da sunan kungiyar World Council of Churches, yayinda aka dafa wa tsarkakan dake a daure a kurkuku hajin da ba a gyara ba kamar wanda na sha ci a cikin sunan Yesu Kirsti.

Ba ya yiwuwa abubuwa su yi ta cigaba haka.

Shi yasa Ikilisiyar karkashin kasa ta yanke shawara cewa idan na sami sarari in bar kasar in zo in sanar da ku Kirista game da abubuwan dake faruwa.
Na yanke shawarar yin allahwadarai da kwaminisanci ko dayake ina kaunar 'yan kwaninis. Ina gani ba daidai bane mutum ya yi wa'azi ba tare daya yi allahwadarai da kwaminisanci ba.

Wasu sun fada mani cewa, "ka yi wa'azin bishara Zallarta." Wannan yana tuna mani cewa 'yan sandan asiri na kwaminis su ma sun taba fada mani cewa in yi wa'azin Kiristi, amma kada in ambaci kwaminisanci. Lallai haka ne, domin su wadanda ke goyon bayan "wa'azin bishara Zallarta" da 'yan kwaminis duk ruhu daya yake zuga su?

Ban san abin da suke nufi da bishara Zallarta ba. Manzo Yohanna Maibaftisma ba wa'azin tuba zalla kawai ya yi ba amma ya kara da cewa "kai sarki Hirudus, baka da kirki mugun mutum ne." Aka fille masa kai domin ba ya tsaya ga koyarwa da kwanakwane ba. Yesu Almasihu ba wa'azi kawai ya tsaya yi a bisa dutse ba, amma ya hada da abin da wasu shugabannin Ikilisiya a yau za su ce ba ya kamata a fada ba; Ya ce "Kaitonku, Marubuta da Farisawa, masu riya...'ya'yan kasaye." Saboda irin wannan wa'azi mara kwanakwana ne aka giciye shi. Da Farisawa ba zasu damu da wa'azin da ya yi a bisa dutse ba.

Dole ne a kira zunubi da sunansa. Kwaminisanci shi ne zunubin da ya fi kowanne muni a duniya a yau. Kowacce bishara wadda bata yi allahwadarai da kwaminisanci ba, to bata cika bishara zalla ba. Ikilisiyar karkakashin kasa tana allahwadarai da wannan duk da yake yana da hadari a gare su. Idan bamu yi haka ba, to ba za a ji mu ba a yammacin duniya.




*Yara makarantar cibiyar kasa da kasa na Stephen ta Nursery da Primary (SC1) da aka kafa don tunawa da Richard Wurmbrand da Sabina Wurmbrand cikin AbeokutaNigeria.*



*Yara ta musamman ta Kaduna da sun rasa Iyayansu a rikice-rikicen addini a Nigeria.*

## Wacce irin gwagwarmaya?

Koyaushe Kiristan dake a kurkuku suna yin addu'a domin masu gaba da su, kuma sun bada shaidu masu kyau gare su. Muradin zuciyarmu shi ne su sami ceto, kuma muna murna duk lokacin da hakan ta samu. Amma ina gaba da mugun abin da tsarin kwaminis yake kunshe da shi kuma ina so in karfafa ikilisyar karkashin kasa wadda ita kadai ce ikon dake iya kawar da mulki na kwaminis na duniya.

Amma a hadu da rashin damuwa da mutanen kasashen yamma suke nunawa game da wannan.

Lokacin da aka daure wasu marubuta 'yan kwaminis su biyu Siniavski da Daniel mutane 'ina cikin duniya sun nuna rashin amincewarsu da abin. Amma ko ma ikilisiyoyi basu nuna rashin amincewa ba lokacin da ake ta jefa salihan kiristoci cikin kurkuku.

Wa ya damu da dan uwa kuzyck, wanda aka daure saboda yana raba takardun addinin kirista? Wa ya san batun dan uwa prokofiev, wanda aka daure domin ya rarraba rubutaccen. Wa'azi? Wanene ya san labarin Balbraniyaen nan kirista, Grunvald, wanda aka daure a Rasha saboda ya raba takardun addinin kirista kuma 'yan kwaminis suka dauke dan karamin yaronsa har yau? Na san abin da na ji lokacin da aka kama ni aka daure ni daga dana mihai. Na ji ciwon abin da aka yiwa Grunvald, Ivanko, Granny Shevchuk, Taisya Tkachenko, Ekataerina vekazina, Georgi vekazin, iyalin pilat a Latvia da sauransu sananun tsarkaka kuma jarumawan bangaskiya na karni na ashirin. Na duka domin in sumbacin sarkokinsu kamar yadda kirista na farko suka sumbaci sarkokin 'yan uwa kirista lokacin da aka kama su zuwa inda za a jefawa dabbobi su cinye su. Wasu shugabannin ikilisiyoyin yamma basu damu da su ba. Sunayen jarumawan bangaskiya ba shi a jeren sunayen da suke da su. Yayinda aka gana masu azaba ana dauri da kisansu, ikilisiyar Baftist ta Rasha wadda gwamnati ce ta nada shugabanninta, kuma, suka juya masu baya, suka ki su, amma kuma wadannan shugabanni ne suka sami karbuwa

Na yanke shawarar in yi allahwadarai da kwaminisanci ba kamar yadda sauran masu adawa da kwaminisanci suke yi ba. Hitler mai adawa da kwaminisanci ne amma duk da haka ya yi bakin mulki. Muna gaba da zunubi amma muna kaunar mai aikata zunubin ya sami ceto.

## ABIN DA YASA NA WAHALA A KASASHEN YAMMA

Na sha wahala a kasashen yamma fiye da yadda na sha a kasashen kwaminis.

Da farko dai wahala ta,ta shafi kewar ikilisiya ta karkashin kasa mai armashin gaske, wadda ta cika abin da ake so, wato bin kiristi sau da-kafa.

A kasar kwaminis, Dan mutum da wadanda ke nasa basu da inda zasu sa kansu. Kiristocin dake a can ba su gina gidaje domin kansu. Amfanin me za ya yi masu? Idan suka gina ma za a kwace a lokacin da aka kama su. Samun sabon gida ma yana kara izawa a kama mutum a jefa kurkuku saboda 'yan kwaminis suna marmarin su sami gidan. A can baka da zarafin bizne babanka ko ka yi ban kwana da iyalinka kafin ka bi kiristi. Wacece mamarka da 'yan uwanka? Ta wajen irin wannan hali, ka yi kama da Yesu. Uwa da 'yan uwa a gare ka , sune wadanda suka cika nufin Allah kawai. Dangantaka ta ruhaniya ta rinjayi ta jiki domin idan tafiya ta yi tafiya, dangantakar ruhaniya ce kadai ke iya tsayawa.

Ikilisiyar karkashin kasa bata da dukiya irin ta duniya amma kuma menbobinta basu da ragwanci ta fuskar ruhaniya. Taron sujada a irin wannan ikilisiya tana kama da sujada ta ikilisiyar farko. Mai jawabi bai san wani dogon turanci akan tauhidi ba, sai gaskiya da gaskiya kawai. Wa'azin irin na manzo Bitrus ne wanda ya yi a ranar fentekos. Yan kwaminis basu san ayoyin littafi Maitsarki sosai ba saboda yana dawuyar samu a kasashensu. Baya ga haka kuma mai yiwuwa ne mai wa'azin ya kwashe shekaru cikin kurkuku babu Littafi Maitsarki. Lokacin da suke bayyana bangaskiya ga uba, tana da zurfi kwarai saboda akwai abin da yasa suka iya

Bayyanawa. Lokacin suna a kurkuku kullum suna rokon wannan uba na cikin sama ya basu abinci kuma a maimakon abinci mai kyau an rika basu jagwalgwalo. Duk da haka suna bada gaskiya cewa Allah uba ne mai kauna. Suna kama da Ayuba wanda ya ce zaya cigaba da bada gaskiya ga Allah ko da Allah za ya kashe shi. Suna kama da Yesu wanda ya kira Allah, "uba "har a lokacin da yake kamar ya yashe shi a bisa giciye. Duk wanda ya san irin armashi na ruhaniya da ikilisiyar karkasin kasa take da shi ba za ya kara gamsuwa da holokon rayuwar ruhaniya da ikilisiyoyin kasashen yamma suke da shi ba.

Na sha wahala a yamma fiye da yadda na sha a kurkukun 'yan kwaminis, saboda yanzu na gani da idanuna yadda ilimin kasashen yamma yake rubewa.

Oswald spengler ya rubuta a cikin littafin sa "Decline of the west " cewa "kuna mutuwa." Na gani cikin dukkan abubuwa alamun rubewa. Ina iya nuna dimbin dukiyarku da dimbin talaucinku, jari-hujja na ku da ra'ayin gurguzu na ku, yake yakenku da juyin juya hali na ku, rashin gaskantawa da kasancewar Allah da rashin begenku, rashin tsarki na ku, kisan aurarraki, kisan haifuwa dake tsiyaye jininku yana kisanku a cikin kwakwalwarku na iya nuna maku cewa wadannan yanayin mutuwar kasashe masu tarihi ne Iskandiriya da Girka da kuma Roma."

An rubuta wannan cikin 1926. Tun daga wancan lokaci, dimokaradiya da wayewa suka mace tuni a rabin nahiyar turai har zuwa kasar Cuba. Sauran bangaren na nahiyar turai ya shiga barci.

Amma akwai wasu da basu barci, sune 'yan kwaminis. Yayinda 'yan kwaminis suke jin kumya, suna kuma karaya, a kasashen yamma kwaminisanci ya zama dafi. Yan kwaminis na kasashen yamma ba rashin yarda da rahotan-nin munannan abubuwan dake faruwa a kasashen kwaminis ba kawai. Suna ta yada aidarsu ba-dare-ba-rana kuma koina har a majami'u. Mu kuma kirista yawancin lokacin bamu goyon bayan gaskiya da dukkan zuciyarmu. muna goyon bayan karya da dukkan zuciyarmu.

Masanan makarantun tauhidi na yamma basu tantauna wani abin kirki a halin yanzu. Wannan ya tuna mani da, yayinda sojojin Mahomet na biyu suka kewaye birinin Constantinople cikin 1493 kuma ya zama dole ne a yanke shawara ko kasashen Balkans zasu zauna karkashin kirista ko masu Mahammadiya majalisar wata majamia tana can cikin wannan birni da aka kawaye tana tantauna wadannan matsaloli: yaya launin idanun budurwa Mai tsarki suke? Mala'iku maza ne ko mata? Menene za ya faru idan ya fada cikin ruwa da aka tsarkake? Shi ma dan ya fada cikin ruwan ya lalace? Wannan kamar wata almara ce kawai a cikin irin halin da ake ciki. Amma sai ka sani cewa a ikilisiya da kuma mujallun ikilisiya a yau suna maida hankali wajen tantauna irin wadannan tambayoyi kawai. Irin barna da kwaminisanci ke yi da kuma wahalolin da ikilisiyar karkashin kasa suke sha ba a faye tantauna su ko ambatonsu ba. Sai muhawarori ba iyaka akan tauhidi da al'adu da wasu abubuwan da basu da muhimmanci.ana wata liyafa sai wani ya yi tambaya ya ce,"idan kana cikin jirgin ruwa wanda yake nutsewa kuma sai ka iya samun kofar tsira zuwa wani tsibiri, kuma kana da dama ka fita da littafi daya kawai daga cikin tarin littafan dake a dakin karatu na jirgin,wane littafi zaka zaba? Sai wani ya ce" littafi maitsarki"wani kuma ya ce, littafin shakes peare."amma wani marubuci ya bada amsar da take
Daidai ya ce, "zan zabi littafin da za ya iya koya mani yadda zan kera kwalakwale domin in ketare zuwa gaba. A can zan sami 'yancin karanta duk abin da nake so."
A kiyaye 'yancin dukkan dariku da dukkan tauhidi ko kuma a yi da-na sanin yin hasara sa, saboda tsanani daga 'yan kwaminis, ya fi muhimmancin da a matsa akan wani ra'ayi na tauhidi.

"Gaskiya tana 'yantarwa," in ji Yesu Kiristi. amma, hakanan, "yanci kadai ke iya bada gaskiya. " kuma a maimakon yin jayayya da juna akan abubuwa marasa muhimmanci, yakamata mu hada kai cikin yakin neman 'yanci daga firiaunancin kwaminisanci.

Na sha wahala kuma Karin samun rabo daga wahalar da ikilisiya ta. kasar kwaminis take sha. Da shike na ratso wadannan wahaloli, ina iya ganinsu cikin zuciyata sosai. Watan Yuni da ya wuce jaridun tarayyar rasha, izvestia da derevenskais jizn sun zargi 'yan darikar Baftis na Rasha da wai suna koyawa membobinsu su kashe yara domin wanke zunubai. Wannan tsohon zargi ne kashi mutane domin ibada wanda aka rika Zargin Yahudawa da shi.

Amma na san abin da wannan ke nufi. Na zauna a kurkukun cluj cikin Rumania a 1959 tare da wani fursuna lazarovici, wanda aka zarge shi da kashe yarinya. Duka-duka shekarunsa talatin da haifuwa, amma duk gashin kansa ya koma fari dare daya saboda azaba.

Ya zama kamar tsoho. Duk an cizge masa farce domin a sa shi ya amsa laifin da ba ya aikata ba. Bayan an shekara ana gana masa azaba sai aka gano cewa lallai ba shi da laifi kuma aka sake shi, amma 'yanci ya daina burge shi. Zuciyarsa ta rigaya ta baci. Wasu sun karanta rahoton zargin da aka yi wa 'yan baftis a jaridun rasha sun yi dariya suka ce wannan sakarci ne kawai. Amma ni na san abin da ake nufi da mutanen da ake zargi. Abin bakin ciki ne ka je yamma ka rika ganin wadannan abubuwa a gabanka. Ina babban Bishop Yermogvn na kuluga [Rasha] da kuma sauran bishop-Bishop bakwai wadanda suna nuna rashin amincewa da matsanancin hadin kai dake tsakanin gwamnatin Rasha da Alexia da kuma babban bisop Nikodim, wadanda suka zama kayan aiki a hannun 'yan kwaminis? Idan da ban ga Bishop din da nuna rashin amincewa da gwamnatin Rumania ya mutu a gado na a kurkuku ba, da ba zan nuna damuwa akan wadannan bishop-bishop mutane Allah ba.

An ladabtar da maaikatan bishara Nikolai Eshliman da Gleb Yakunin saboda sun bukaci 'yancin addini a ikilisiyar su. Kasashen yamma sun san wannan zance soisai. Amma ina a kurkuku tare da fada loan na Vladimireshi, Rumania, wanda irin wannan ta faru da shi. A sama sama ana ganin horon ikilisiya ne kawai,

suna aiki tare da 'yan sandan asiri.

Wadanda shugabannin suka sa karkashin horo kuma an sasu karkashin horon da yafi wannan wato azaba, duka, shan kwaya a kurkuku. Na yi rawar jiki saboda wahalar da wadanda ake tsanantawa a kasashen kwaminis azaba. Na yi rawar jiki saboda kirsta na kasashen yamma wadanda basu taimakawa 'yan uwansu da ake kuntatawa.

A cikin birnin zuciyata, ina son in kiyaye kaina daga shiga wanna gagarumin fadan. Na fi so in kebe wani wuri inda babu hayaniya domin in huta. Amma ba ya yiwuwa. Kwaminisanci yana bakin kofa. Lokacin da kwaminis suka mamaye Tibet sai suka kawo karshen mutanen da basu shiawar kome sai maganar ruhaniya. A kasarmu, sun kawo karshen duk wadanda basu yarda su rungumi kaddara ta zama karkashin akidarsu ba. Suka rushe ikilisiyoyi da wuraren da aka kebe domin nazirin addini. Sai suka bar 'yan kalilan wadanda suke moro domin damfarar baki. Wannan rayuwa a kebe domin hutawa wadda na yi kwadayi don gujewa abin da ke faruwa ne.

Dole ne in jagoranci wannan yakin ko dayake yana da hadari kwarai a gare ni. Idan na bace, ku tabbata cewa 'yan kwaminis ne suka sace ni. Sun kama ni a titi cikin 1984 kuma suka saka ni kurkuku da wani barawon suna.Anna panker sakataren kasarmu na wannan lokaci ya ce da jakadan kasar Sweden sir Patrick von rauterswaerde,"oh yanzu Wurmbrand yana yawo a titinan Copenhagen." Jakadan na Sweden yana tare da wasikar da na rubuta, kuma aka yi sumogal din ta daga kurkuku, a aljihunsa,; ya gane cewa an shiryaa masa karya ne. irin wannan abu yana iya sake faruwa. Idan aka kashe ni, lallai kwaminis ne suka sa a kashe ni. Babu wani wanda yake da nufin ya kashe ni sai dai su. Idan kuka ji wata jita jita game da rayuwata ta tsarki, sata, ludu, zina,rashin rikon amana ta siyasa,

karya ko kuwa kome menene na aikin sha game dani to 'yan sanda asiri ne ke cika barazanar da suka yi mani. Sun ce zasu bata mani shaida. Wata majiya mai tushe ta fada mani cewa gwamnatin Rumania ta yanke shawarar ta kashe ni bayan shaidar da na bayar a gaban'yan majalisar

Dattawa na kasar Am erika. Zasu yi kokarin kashe ni ko su bata mani suna. Zasu yi kokarin bata mani suna ta wurin ba abokaina na cikin Rumania tsoro. Suna da hanyoyin yin hakanan. Ranan ba zan iya yin shiru ba kuma aikinku shine ku bincika dukkan abin da na fada maku da kyau; ko da kuna tunanin cewa ai na ratso abubuwanne, na sha wahala daga azaba iri-iri dole ne ku tambayi kanku wanne irin mugun iko ne kwaminisanci yake da shi wanda yake sa 'yan kasar ke shan bakar wahala.wanne irin iko ne da yake sa mutane daga Jamus ta gabas suke daukar har ma kananan yara a buldoza su ketare ta cikin waya cikin kasa da ko za a harbe dukkan iyalin?

**Kasashen yamma suna barci kuma dole ne a farkar da su**

Mutanen da ke shan wahala suna neman wanda zasu dorawa laifi. Idan suka sami wanda zasu aza wa laifi sun rage nauyin damuwarsu. Ni bana iya yin haka.
Ba na iya sa wa wasu shugabannin ikilisiya na yamma wadanda suka amince da kwaminisanci laifi. Miyagun abubuwan ba daga gare su suke fitowa ba. Sun dade. Su ma wadannan shugabannin sun sami kansu ne cikin wannan dadadden abu. Basu suka kirkiro wannan shirme da ikilisiya take ciki ba. Haka suka sami abin.
Tun da na zo kasashen yamma, na ziyarci makaratun tauhidi da dama. Na ji laccocinsu game da tarihin karaurawa da wakokin sujada, da dokokin rubuta littafi Maitsarki da aka rabu da yin amfani da su ko kuma game da wani horo na ikilisiya wanda yanzu babu shi. Na ga daliban tauhidi suna koyon cewa labarin halitta dake cikin Littafi Maitsarki ba gaskiya bane, haka ma labarin Adamu, da labarin ruwan tufana, da labarin Musa; kuma wai annabce annabce an

budurwa tatsiunniya ce, haka nan tashin Yesu daga matattu; wai kasusuwansa sun kasance a kabarin, wai wasikun manzanni ba na gaskiyar bane, kuma wai Ruya ta Yohanna littafin mahaukaci ne,

Amma baya ga haka Littafin Baibul Littafin Maitsarki ne. (wannan ya bar littafi Maitsarki da zargin yana kunshe da karairayi fiye da jaridan 'yan kwaminis). Wannan shi ne abin da shugabannin Ikilisiya na yanzu suka koya lokacin da suna saminari. Wannan shi ne irin yanayin da suke rayuwa ciki. Me ya sa za su zama da aminci ga Ubangijin da aka fadi irin wadannan abubuwa a kansa? Me ya sa shugabannin Ikilisiya zasu yi aminci ga Ikilisiyar da ana iya koyarwa a sarari cewa Allah ya mutu?

Sune shugabannin ikilisiyar da gwamnati ta san da zaman ta, ba ikilisiyar da take amaryar kiristi ba. Su shugabanni ne a ikilisiyar da ta bashe da Ubangijinta tuntuni. Lokacin da suka sadu da memba na ikilisiyar karkashin kasa ikilisiyar da ke shan zaba, sai su dube shi kamar wata halitta dabam.

Abu na biyu, ba daidai bane ka sharanta mutane saboda wani bangare na halayensu. Idan na yi haka, zamu zama kamar farisawa wadanda a gare su Yesu ba shi da kirki, saboda haka ba ya girmama dokokinsu na asabaci. Wannan ya rufe masu idanu kwata kwata ga abin da yake mai kyau wanda zasu iya gani a cikin Yesu.

Wadannan shugabannin Ikilisiya wadanda suke nuna halin da ba ya dace ba ga kwaminisanci tana yiwuwa sun yi daidai a wasu abubuwa da yawa kuma me yiwuwa ne bakin gaskiyarsu suke yi.

## Har ma a inda suka yi kuskure suna iya canjawa.

Na taba zama da wani dan ikilisiya mai ra'ayin mazan jiya a Rumania. Shi yana goyon bayan kwaminis, yana bashe tumakinsa. Na kama hannunsa kuma na fada masa misalin bataccen da irin kaunar da Allah yake karbar mai zunubi wanda ya juyo wajensa. Yana karba na har ma bishop idan ya tuba."na yi masa wakar kirista.wannan mutum ya tuba.

Na zauna a kurkuku tare da wani firis na ikilisiya mai ra'ayin mazan jiya wanda, a cikin begen sallama, ya rubuta lacca akan cewa babu Allah. Na yi Magana da shi kuma ya yayyage abin da ya rubuta, ta wurin yin haka ya shiga hadarin rashin samun sallama har abada.

**Ba zan iya neman dorawa wani laifi ba, ba zan iya sauke nauyin dake cikin zuciyata ta wurin haka ba.**

* * *

Bani da wani ciwo.har ma abokaina na kurkusa basu fahimce ni ba. Wasu daga cikinsu ma suna zargi na da jin haushi da rena 'yan kwaminis, abin da na san cewa ba gaskiya ba ne. Wani marubuci mai suna Claude Montefiore ya ce, halayyar da Yesu ya nuna wa Marubuta da Farisawa, yadda ya rika yin allahwadarai da su a bainar jama'a baya yi muwafaka da umurninsa na a nuna kauna ga abokan gabarmu kuma mu albarkaci masu la'antarmu ba. Kuma Dr. W. R. Matthews, wanda kwanan nan ya yi ritaya daga shugaban St. Pauls a London, ya yanke shawara cewa wannan rashin ma'ana ne da rashin tsaida Magana ta Yesu. Ya bada hujjar cewa Yesu ba wani mai ilimi bane. Raayin Montefiore game da Yesu ba daidai ba ne kuma muguwar bata ce. Yesu yana kaunar farisawa, koda yake yana yin allahwadarai da su a bainar jama'a. kuma ina kaunar 'yan kwaminis da kuma mutanen da suke mora a Ikilisiya, koda yake ina yin allahwadarai da halinsu.

Babu fasawa ina fada cewa, "A manta da 'yan kwaminis, a yi aiki cikin abubuwa na ruhaniya kawai." Na sadu da wani kirista wanda ya sha wahala a hannun 'yan Nazis. Ya fada mani cewa, matsawar dai ina shaida Yesu kiristi shi yana bayana kwata-kwata, amma kada in fadi ko kalma guda game da kwaminisanci. Na tambaye shi ko kirista wadanda suka yaki Hitler a Jamus sun yi kuskure kuma ko yakamata da an hana su fadin kome game da bakin mulkin Hitler sai dai su koyarda abin da ke cikin Littafi maitsarki kawai?

Ya bada amasa ya ce, "Amma Hitler ya kashe Yahudawa har miliyan shida! Saboda haka dole ne mutun ya yi maganar sukansa." Na ba shi amsa na ce,"kwaminisanci ya kashe mutane miliyan talatin a Rasha kuma miliyoyi a China da kuma wasu wurare. kuma sun kashe yahudawa ma. Sai an kashe yahudawa da Mutanen Rasha ne kawai zamu nuna rashin amincewa? "sai ya amsa ya ce,"wannan kuma wani abu ne dabam."ban sami wani bayani ba.



*Ina ne Ikilisiyar kalkashin kasa suke saduwa? Cikin Gidaje, a sararin rufin daki, kalkashin rusasshen gidan sama, koina da masu bi zasu iya taru a boye, ko kuma a gefen rafi ko kurmi Har wa yau akwai irin wuraren nan a Viyataman, Laos, China, da Gabas ta Tsakiya da wasu kasashe. Yawancin Lokaci yan sanda kan gano irin wuraren da yakan kai a yi masu tara mai yawa ko kama su akaisu kurukuku.*

**A** lokacin Hitler 'yan sanda sun yi mani duka kuma a zamanin kwaminis ban ga wani bambanci ba kuma. Dukansu wahala ce.
Dole ne kiristanci ya yi yaki da fannonin zunubi da yawa, ba da kwaminisanci ba. Bamu damu da wannan matsalar ba.

Amma a halin yanzu, kwaminisanci shi ne babban abokin gabar kiristi kuma wanda ya fi hadari duka. Kuma dole ne mu hada karfi mu yake shi.



In kara fadi kuma, manufar mutum ta zama yana so ya zama kamar kiristi. Babbar manufar kwaminisanci shi ne, ya hana wannan. A kashin gaskiya suna gaba da addini. Sun yi imani cewa bayan mutum ya mutu sai ya zama gishiri da sauran maadanai, fakat. Suna so dukkan rayuwar mutum ta dogara akan jiki. Jama'a kawai suka sani. Kalamansu suna daidai da na iskokan nan na cikin sabon Alkawari wadanda lokacinda aka tambaye su sunansu suka ce,"Mu tuli ne." Ruhun mutum kyautar da Allah ya yiwa mutum wadda tafi kowace kyau a duniya- sun sami mutum da wani littafi da Alfred Adler ya rubuta mai suna" individual psychology."

Yesu yana so mu kasance da ruhanya. Saboda haka babu yiwuwar shiryawa da kwaminisanci. Yan kwaminis sun san wannan. A cikin wata mujalla ta su da suke kira, Nauka I Religia (wato kimiya da Addini)sun rubuta cewa, "Addini ba ya taba haduwa da kwaminisanci. Yana gaba da shi, Tsarin jami'iyar kwaminis shi ne rushe addini kwata-kwata. Tsarin ne domin maida jama'a masu ra'ayin cewa Allah ba ka kasancewa ba, ta wurin haka ne mutane zasu kawar da kangin bauta na addini har abada." Kiristiyaniti yana iya tafiya tare da kwaminisanci? Ga amsar 'yar kwaminis ga wannan tambaya--- "kwaminisanci naushi ne na kisan addini."



## BABI NA BIYAR: FIVE
## YADDUWA IKILISIYAR KARKASHIN KASA

Yanzu zan kara Magana game da ikilisiyar karkashin kasa. Tana aiki a karkashin mawuyacin hali. Arnancin mai musun kasancewar Allah shine addinin kasashen kwaminis. Basu ba da 'yanci ga yadda manyan suke bada gaskiya, amma dole ne a hana matasa da yara su bada gaskiya. Kome da kome a cikin wadannan kasashe radiyo, telebijan, silma, wasan kwaikwayo, 'yan jarida da jaridu, gidajen buga takaradu duka manufarsu ita ce kawar da gaskantawa ga Allah.

Ikilisiyar karkashin kasa bata da wadata har hanyar yin adawa da wannan karfi na 'yan kwaminis. Ma'aikatan bishara na ikilisiyar karkashin kasa dake Rasha basu da horo na aikin wa'azi. Akwai fastoci wadamda basu taba karanta Littafi Maitsarki dukansa ba. Zan fada maku yadda aka nada da yawa daga cikinsu. Mun sadu da wani saurayi dan Rasha wanda yake aikin bishara a asirce. Na tambaye shi wanda ya nada shi. Ya ce ......

"Ba mu da wani Bishop wanda za ya nada mu. Bishop na gwamnati ba ya nada duk wani wanda jami'iyar kwaminis bata amince da shi ba. saboda haka mu samari mu goma kirista muka je kabarin wani bishop wanda ya mutu saboda Yesu. Biyu daga cikinmu, muka daura hannuwan mu a bisa dutsen kabarin . sauran suka yi mana da'ira kuma muka roki Ruhu maitsarki ya nada mu. Mun tabbata ya nada mu ta wurin hannuwan Yesu Kiristi." A ganina, nadin wadannan samari ya sami amicewar Allah. Mutane masu irin wannan nadin ko kebewa, kuma wadanda basu taba samun wani horo daga makarantar tauhidi ba, kuma wadanda yawancin lokaci basu da sani mai zurfi a littafi maitsarki suna cigaba da aikin kirista.

Abin ya yi kama da ikilisiya ta karnonin farko. Wacce saminari ce wadannan wadanda suka girgiza duniya da bisharar kiristi suka yi? Dukkansu sun iya karatu? Kuma daga ina ne suka sami littafi Maitsarki? Allah ya yi Magana da su.

Mu 'yan ikilisiyar karkashin kasa ba mu da manyan majamiu ( Cathedrals). Amma akwai wata majami'a wadda tafi sararin sama kyau wanda muke dubawa lokacin da muke taruwa a asirce cikin daji. Kukan tsuntsaye ke yi mana muzika. Kamshin furanni shi ne turaren mu. Kuma tsummokaran jikin jarumawan Kiristi wadanda aka sako daga kurkuku sun fi bamu sha'awa da rigunan firistoci. Muna da wata a matsayin kandil. Malaiku ne masu kunnawa.

Ba zan taba iya bayyana kyau da armashi wannan Ikilisiya ba. Sau da dama, bayan sujada a asirce, sai a kama kirista a kai su kurkuku. Kiristocin suna farinciki da sarkokin da aka daure su wadda amarya ke sawa a matsayin kyauta mai daraja daga kaunataccenta. Ruwayen dake kurkuku basau motsi. Kana samun sumba da runguma daga gare shi kuma ba zaka so ka musanya wurare da sarakuna ba. A gaskiya na sami kirista wadanda suke murna cikin littafi maitsarki kawai, a Ikilisiyar karkashin kasa da kuma a kurkuku.

Ana kuntatawa Ikilisiyar sosai, amma kuma tana da abokai da yawa- har ma daga cikin 'yan sandan asiri da ma jami'an gwamnati. Wani lokaci wadannan 'yan sandan asiri suna bada gaskiya kuma suna kare Ikilisiyar karkashin kasa. Kwanan nan, Jaridun Rasha suka yi korafin karuwar yawan wadanda a waje ne kawai suke marasa bada gaskiya.

Gidajen jaridun sun bayyana cewa irin wadannan mutane sun kunshi mata da maza babu iyaka, wadanda ke aiki cikin tsakkiyar kwaminis a ofisoshin gwamnati, a ma'aikatun yin furofaganda da kuma ko'ina wadanda a waje a fuska 'yan kwaminis ne, amma a cikin zuciya a asirce membobin Ikilisiya ta karkashin kasa ne.

Gidajen jaridun na kwaminis sun bada labarin wata budurwa wadda ta yi aiki a ofishin furofaganda na kwaminis. Bayan aiki, suka ce, sai ta je gidanta a can zata hadu da mai gidanta wanda ya fito daga wurin aikinsa. Bayan sun ci abinci, ita da mai gidanta sai su tara matasa daga sauran gidajen makwabta a gidansu kuma su yi binciken Littafi maitsarki a asirce da kuma taron addu'a. Irin wannan na faruwa koina a kasashen kwaminis. Dubban mutane irin wadanda ana ganinsu kamar marasa bi a waje suna nan jibge a kasashen kwaminis. Suna jin yafi kyau su kaurace wa majami'u na rufarufa inda za a rika kiwon hankalinsu kuma inda bisharar da ake yi sai 'yan kwaminis sun tace. A maimakon haka sai su rike matsayinsu a gwamnati kuma daga nan su rika shaida kiristi a asirce. Ikilisiyar karkashin kasa, mai aminci, tana da dubban membobi a irin wadannan wuraren. Suna yin tarurukansu a asirce. A Rasha babu wanda ya sake tunnawa da jayayyar da ake yi a da akan baftismar manya ko yara, ko aji zancen fada. Babu zancen goyon baya na masu ra'ayin mulkin Yesu na shekara dubu. Basu iya fasara annabce annabce kuma basu yin jayayya akanus, amma ina mamaki sau da yawa suna iya tabbatarwa masu musun kasancewar Allah cewa akwai Allah Amsoshin da suke ba wadannan arna masu sauki ne: "ldan aka gayyace ka zuwa buki wanda akai kowanne irin nama mai kyau, zaka yarda babu wanda ya dafa naman nan? Amma halittu wani buki ne aka shirya mana. Akwai tumatiri da madara,da zuma, da lemo da sauransu. Wanene ya shirya dukkan wadannan abubuwa domin dan adam? Idan baka bada gaskiya akwai Allah ba, to kai makaho ne, domin yaya zaka iya bayyana yadda wadannan abubuwa da muke bukata da yawa suka kasance? Suna iya nuna tabbatar akwai Allah. Na taba jin wani yana kokarin shawo kan wani mai musun kasancewar Allah, ya ce, "ina jin muna iya Magana da gudajin jinni na farkon ciki a mahaifar uwarsa kuma kana iya fada masa cewa kwanakinsa gajeru ne bayan nan za ya fada rayuwa ta ainihi wadda zata dade. Menene gudajin jininnan za ya amsa maka? Za ya fadi abin da ku masu arnancin ke musun.

Kasancewar Allah kuke bamu amsa lokacin da muka yi maku maganar gidan jinkai da jahannama. Za ya ce, rayuwa ta cikin mahaifar uwarsa ita kadai ce rayuwa kuma kome shirme ne na addini. Amma idan wannan gudajin jini za ya iya yin tunani, za ya ce da kansa, " Nan hannu ya tuko a jikina. Ba ni bukatarsu. Ba na ma iya mike su. Menene yasa suka tuko? Me yiwuwa ne domin wani mataki na rayuwa nan gada wanda zan bukaci yin aiki da su kafafu sun tuko, amma na bar su a lankwashe a kirji na. Me yasa suka tuko? me yiwuwa ne rayuwa a duniya mai fadi da zata biyo baya, inda zan bukaci in yi tafiya . idanu sun fito, ko dayake ina kewaye da dufu kuma bani bukatar su a cikin mahaifa. Me yasa na ke da idanu? Me yiwuwa ne duniyar da take da haske da launuka zata biyo baya. Saboda haka, idan gudan jinni na farkon ciki za ya yi tunani game da yadda ya faro, za ya san wani abu game da abin da ya gani ba. Haka yake a gare mu. Matsawar dai muna samari, da kuzari, amma ba mu da tunanin yin amfani da shi daidai. Lokacin da shekaru suka fara yawaita, mun karu da sani da kuma hikima, makara tana jiranmu ta kaimu kabari. Me yasa ya zama wajibi a yi girma cikin sani da hikima wadanda ba kuma zama iya mora ba?Me ya sa hannuwa, da kafafu da kuma idanu suke fitowa gudan jinni na farkon ciki? Domin abin da zai biyo baya ne. haka yake a gare mu a nan. Muna girma muna karuwa da sani da hikima domin abin da zai biyo. An shirya mu domin mu yi wa wanda yake gaba da kowa hidima bayan wannan sai mutuwa."

Game da Yesu, tauhidin 'yan kwaminis shi ne, wai ba a taba yin sa ba. Ma'aikatan ikilisiyar karkashin kasa sun bada amsa mai sauki akan wannan sukan ce,"wacce jarida ce kake dauke da ita a aljihunka? Jaridar Pravda ce ta yau ko jiya? Bari in duba. Af. 14 ga watan jannairu 1964. 1964, daga yaushe aka fara kidayar? Amma kuna kidayar shekaru tun daga haifuwarsa? Lokaci ya kasance kafin sa. Amma lokacin da ya zo, sai dan adam ya ga cewa duk abin da aka yi a da kafin zuwansa, ya zama a banza kuma lokaci na ainihi yanzu ya fara. Jaridunku na kwaminis kansu sun tabbatar cewa zance Yesu kiristi ba tasuniya bace."



*Kasadar kai da yanci, Jakunan Allah Bible tsirbi ana amfani da su kamar hanyoyi na kai maganar Allah ga mayunwanta masu bi a kasashe da ke hana a shiga da Bible, masu gadi a Gabashin Jarmus sukan huhuda jikin mota don neman Bible da mai yiwuwa an boye.*

Fastocin dake yamma yawancin lokaci suna dauka cewa lallai membobinsu sun san gaskiyar kiristiyaniti, kuma a gaskiya basu sani ba. Da wuya ka ji an yi waazi wanda ke nuna tabbatar gaskiyar bangaskiyarmu.

A kasashen kwaminis, mutane wadanda basu taba samun horo ba, suna ba wadanda suka tuba fandeshon mai kyaun gaske.

Babu wani bango da ya raba Ikilisiyar karkashin kasa da ikilisiyar da gwamnati ke daurewa gindi. Sun sansance da juna. Fastoci da yawa na majamiun rufa na gwamnati suna yin aikin wa'azi gaskiyar kiristi a asirce suna ketare iyakar da gwamnati ta sa masu. Ikilisiyar gwamnati, Ikilisiyar da take hada baki da 'yan kwaminis tana da dogon tarihi. Ta fara ne nan da nan bayan 'yan gurguzu na Rasha sun yi juyin-juya hali da"Rayayyar Ikilisiya " wadda wani firis mai suna Sergius ke shugabanta.

A lokacin, Rayayyar ikilisiyar tana fada,a bainar jama'a, a birnin Moscow cewa, "manufarmu ba ta sake gina Ikilisiya ba ce, amma a kawar da ita, a shafe dukkan addini" wannan shiri ne mai kyau domin ikilisiya! A kowacce kasa muna da wasu kamar Sergius. A Hungary, a cikin 'yan katolik, wani ne Fada Balogh. Shi da wasu masu waazi yan furotestant suka taimaka wa 'yan kwaminis su kama kasar. A Rumania, 'yan kwaminis sun kama mulkin kasar da taimakon firis na ikilisiya masu ra'ayin mazan jiya mai suna Burducea, wani dan jami'iyar masu ra'ayin danniya (Facist) wanda ya nemi rufe zunubansa ta wurin kara aikata zunubi. Wannan firis ya tsaya kusa da sakataren kasar Rasha vishinki, yana murmushi na nuna yarda da abin da ke faruwa daga baya a wurin kaddamar da gwamnatin kwaminis ya ce, "wannan gwamnati zata gina aljannar duniya kuma ba zaku kara bukatar aljanna ta sama ba."

Game da babban bishop na Rasha Nikodim kuwa, babu wata tantam cewa shi dan leken asiri ne na gwamnati. Major Deriabin, wanda ya balle daga 'yan sandan asiri na Rasha, ya bada shaidar cewa Nikodim yana yi masu leken asiri.

Wannan shi ne irin halin da kusan dukkan darikun suke ciki. Shugabannin darikar Baftist ta Rumania gwamnati ce ta dora su da karfin tsiya. Ta musunci kirista na ainihi. A Rasha, shugabannin baftist na can su ma haka suke. Shugaban Adventists na Rumania, Tachici, ya fada mani da kansa cewa yana yiwa 'yan sandan asiri na kwaminis leken asiri tun daga ranar da suka kama mulkin kasar.

A maimakon su rufe kowacce majamia ko dayake sun rufe dubbai-yan kwaminis cikin riya, suka shawarta su bar ikilisiyoyi kalilan su cigaba karkashin ikon kwaminis kuma suna yin amfani da su a matsayin tagar da zasu iya lura, da mulkawa da kuma lalata ko kawar da kirista da kiristiyaniti a kwana a tashi. Suka shawarta cewa yafi kyau su bar gine-ginen majamiu a tsaye kuma su maida su kayan aiki na kwaminis na mulka kirista da kuma yaudarar baki masu zuciya ziyara kasashen su. An nemi in yi fasto a daya daga cikin irin wannan majami'a bisa kaidar zan rika bada rahoton membobi na ga 'yan sandan asiri. Da alamun cewa mutanen yammacin duniya sun saba da dukkan, "baki da fari" duka wannan hanyar ko waccan basu iya fahimtar wannan. Amma Ikilisiyar karkashin kasa ba zata taba yarda da yan Ikilisiyoyi kalilan da ke karkashin ikon kwaminis a maimako Ikilisiyoyi ta ainihi, mai himmar shaida bishara ga "kowacce halitta" har da matasa.

Amma a Ikilisiyoyi da ke mallakar gwamnati akwai mutane da dama masu ruhaniya duk da munafukan shugabanni da gwamnati ta shuka. (Ina da ra'ayin cewa a Ikilisiyoyi da yawa a yammacin duniya al'amarin kamar wannan ne. Jama'ar Ikilisiya wani lokaci suna da aminci ba don saboda shugabanni da suke da su).

Ba a canja wakokin sujada na Ikilisiya mai ra'ayin mazan jiya ba, kuma tana ciyar da zukatan membobinta ko da wa'azin bakoncin ne a kwaminis. Su ma 'yan Lutheran, da presbyterian da sauran 'yan furotestant, suna raira wadannan tsofoffin wakoki. Ko wa'azin masu bada asirin Ikilisiya dole ne ya kunshi wani abu daga maganar Allah. Mutane suna tuba su karbi Kristi a hannun mutanen da suke munafukai masu bada 'yan uwansu, kuma sun sani cewa wadannan mutane zasu fada wa 'yan sanda asiri labarin tubansu, mutane da yakamata su boyewa, kuma ta wurin karkataccen 'wa 'azinsu ne suke tuba.

Wannan babban al'ajibi ne na Allah, wanda a Leviticus 2 an rubuta game da shi kamar haka, "Idan bangare na gawa (wadda bisa ga dokar Musa tana bata tsarki) ya fada bisa irin da zaka shuka, irin ya tsakaka--."

Gaskiya ta sa dole ne mu fadi cewa ba dukkan shugabannin Ikilisiya ne suke 'yan kwaminis ba.

Akwai membobin Ikilisiya ta karkashin kasa da suke fitattu a Ikilisiyoyi gwamnati, sai dai akwai wasu da ya zama dole ne su boye kansu. Kuma suna daukar kristanci ba wani abin wasa ba ne amma yaki ne na bangaskiya. Lokacin da 'yan sandan asiri suka zo don su rufe wurin koya sanin Littafi Maitsarki dake a Viadimirshti cikin Rumania kuma da irin wadannan wurare a Rasha basu sami abin da sauki ba. Wadannan 'yan kwaminis sun biya da rayukansu farashin laifin kokarin hana yin addini.

Amma Ikilisiyoyi malakar gwamnati suna ta karkacewa. Ban tabbatar ba ko har yanzu akwai majami'u dubu biyar zuwa shidda a Tarayyar Rasha (Tarayyar Amerika wadda take da yawan jama'a kusan daya da Rasha tana da majami'u dubu dari uku). Kuma yawancin wadannan majami'u na Rasha 'yan kananan dakuna ne ba majami'u irin yadda muke tunani baki masu ziyara sukan ga majami'a a Moscow ta yi cunkoso-wadda ita kadai ce majami'ar Furotestant a birnin kuma sai su rika yabawa da yancin addini da suke ganin kamar akwai. Sai suna bada rahoto, "majami'u har suna cika suna batsewa." Ba su ganin irin hadari da bakin cikin da Ikilisiyar Furotestant mai membobi miliyan bakwai suke ciki ba. kuma daga cikin irin kananan majami'un nan kashi tamanin daga cikin dari na mutanen Rasha basu iya zuwa saboda nisa. Wadannan tarin jama'a dole, ko dai a manta da su, ko kuma a kai masu bishara ta wurin dabarar wa'azi irin ta Ikilisiyar karkashin kasa. Babu wani zabi.

Kwaminisanci na kara habaka, Ikilisiya tana kara juyawa zuwa ga hidima ta karkashin kasa.

A wuraren da aka rufe Ikilisiya mallakar gwamnati sai a cigaba da yin taruruka na kungiyoyi masu gaba da Allah.

## YADDA IKILISIYA KARKASHIN KASA KE "CI"DAGA LITTAFAN MASU MUSUN KASANCEWAR ALLAH

Amma Ikilisiyar karkashin kasa ta san yadda take yin amfani da irin wadannan littafan masu cewa babu Allah kamar yadda hankaka suka ciyarda anabi lliya. Masu musun Allah suna gwada gwaninta da dokin yiwa littafi maitsarki batanci da kuma kokarin karyata ayoyin da ke cikinsa. Suna buga Litattafai da suke kira"The Comical Bible" da kuma "The Bible for Believers." Sun yi kokarin tozarta ayoyin Littafi maitsarki. Mun ji dadin ganin wadannan litattafai na su, saboda zargen da suka yi a ciki duk shirme ne kuma babu wanda ya kula da abin da suke yi. Amma sun buga miliyoyin kwafi na littafi ciki da ayoyin littafi maitsarki wadanda suke da kyau wanda yafi gaban fada duk da kokarin yan kwaminis na bata su. A zamanin da, ana kona wadanda suka yi ridda a bainar jama'a bayan an sa masu tufafin da aka yi zane na ba'a a jikinsu. Kuma wadannan mutane da aka zarga tsarkaka ne na sahiha. Saboda haka gaskiyar ayoyin littafi maitsarki ta na nan daram babu canji koda shaidan ya more su don biyan bukatun kansa.madaba'ar kwaminis ta yi farin cikin samun dubban wasiku ana rokonsu su kara buga wadannan littafi maitsarki domin yin masu ba'a . basu sani ba wadannan wasiku sun fito ne daga Ikilisiyar karkashin kasa, wadda bata da wata hanyar samun wasu litattafan addinin kirista.

Kuma mun san yadda muke moron tarurukan arna masu musun kasancewar Allah.

Wani shehun malami (furofesa) na kwaminis ya nuna, a wani taro, cewa Yesu ba wani bane dan dabo ne kawai. Furofesan ya aje tulun ruwa a gabansa. Ya zuba hoda cikin tulun, sai ruwan ya koma ja. Sai ya ce,"wannan shi ne abin da ake kira al'ajibi." "Yesu ya boye hoda a cikin rigarsa kamar wannan , daga nan sai ya yi wa mutane rufa ido wai ya canja ruwa zuwa ruwan anab ta hanya mai ban mamaki. Amma ni zan iya yin abin da yafi na Yesu. Zan iya sake

Canja wannan ruwan anab ya koma ruwa kamar yadda yake da farko." Sai ya sa wata hodar cikin ruwan sai ruwan ya koma da launinsa na ruwa. Ya sake sa wata hodar ruwan ya sake rikidewa ja.

Sai wani kirista ya tashi tsayi ya ce, "Furofesa, ka bamu mamaki da abin da kake iya yi. Zamu tambaye ka ko kuwa roke ka abu guda kawai, ka sha kadan daga cikin ruwan anab din da ka yi. " sai Furofesan ya ce, "ba zan iya yin wannan ba. Domin hodar da na mora tana da dafi." Sai wannan kirista ya amsa ya ce, "wannan shine bambancin dake tsakaninka da Yesu Almasihu. Yesu da ruwan anab nasa, ya bamu murna da farin ciki shekara dubu biyu, amma kai ka bamu dafi da irin naka ruwan anab din." Sai aka kama wannan kirista aka jefa shi kurkuku. Amma labarin abin da ya faru ya bazu da nisa kuma ya karfafa bangaskiyar masu bi. Bamu da karfi kamar kananan Dauda, amma mun fi Goliath na marasa Allah karfi domin Allah yana wajenmu. Mu ked a gaskiyar.

Wata rana aka ba wani dan kwaminis lacca game da musun kasancewar Allah. Aka bukaci dukkan ma'aikatan kamfanonin su halaci laccar kuma a cikinsu akwai kirista. Suka zauna shiru suna jin dukkan hujjojin da ake kawowa na karyata kasancewar Allah da kuma wawancin gaskantawa da kiristi. Sai mai bada laccar ya cigaba da kokarin nuna cewa babu wata rayuwa cikin ruhu bayan mutuwa babu Allah, babu Kirista kuma babu wata rayuwa bayan mutuwa, mutum jiki da rai kawai gare shi babu wani ruhu. Ya yi ta maimaita wannan.

Wani Kirista ya tashi, ya tambaya ko zan bar shi ya fadi wani abu. Aka ba shi izini. Sai Kiristan ya dauki kujerarsa ya jefar da ita. Ya tsaya yana kallonta Daga nan sai ya je ya mari dan kwaminis din dake yin laccar. Sai mai laccar ya hazala. Fushinsa ta murtuke don haushi. Sai ya daka masa tsawa da zagezage kuma ya kira wani dan kwaminis din ya ce ya kama wannan Kirista. Ya ce, yaya kake da gabagadin mari na?. Menenen dalilin marin?



*Richard da Sabina Wurmbrand da yanuwa a Afrika.*



***Krista suna sujada a masujadarsu da Musulmi masu zafin hali sun lalata.***

Kiristan ya amsa yace, " ka karyata kanka yanzu nan. Ka ce kome yana da jiki ne kawai babu wani ruhu. Na dauki kujera na jeffar da ita, da yake bata da ruhu bata yi fushi ba, wannan ya tabbatar mana cewa jiki kawai take da shi. Amma lokacin da na mare ka baka yi kamar yadda kujerar

ta yi ba saboda kana da ruhu. Wanda bashi da ruhu ba ya fusata amma kai ka fusata. Saboda haka, dan uwana furofesa, laccar ka ba gaskiya ba ce. Mutum ya wuce jiki kawai, yana da ruhu. Ta wurin wadannan hanyoyi masu yawa kirista na Ikilisiyar karkashin kasa suka rika karyata masu gardamar kasancewar Allah da gidan gobe.

A kurkuku, ofisa mai kula da gudanarwa ya tambaye ni da zafin rai,"Har yaushe zaka cigaba da rike wannan addinin naka na banza?" na ce da shi, " na ga marasa Allah da yawa suna da-na-sani a lokacin mutuwarsu saboda sun yi rayuwa babu Allah, suna kiran Kiristi. Kana zaton Kirista za ya yi da-na-sani a lokacin mutuwa, cewa shi Kirista ne kuma ya yi kiran Marx ko Lenin su ceci shi daga bangaskiarsa? Ya fara dariya ya ce, " wannan amsa ta ka akwai; Hikima. " Na cigaba na ce, "Lokacin da injiniya ya gina gada, don keken dawaki ya bi kan gadar wannan baya nuna cewa gadar tana da kyau ba. Dole sai jirgin kasa ya bi kan gadar kafin a tabbatar da nagarinta. Wai don kana musun Allah cikin kwanciyar hankali wannan baya nuna cewa ra'ayin cewa babu Allah gaskiya ba ne. Idan wahala ko jaraba ta auko maka ba zaka iya tsayawa kan wannan ra'ayi ba." Sai ka yi amfani da litattafan Lenin domin in tabbatar masa da abin da na fada. Ko lokacin da Lenin yake shugaban gwamnatin Tarayya Rasha ya kan yi addu'a lokacin da wahala ta taso.

Mun yi shiru muna jiran abubuwan da zasu faru. 'Yan kwaminis ne suke tsaye, saboda babu salama cikin rayukansu. Kuma sun shiga kamfen gadan-gadan na kawar da addini daga zukatan mutane. Ta wurin yin haka suna cika abin da St. Augustine ya ce, "Babu salama cikin zuciya sai idan ta sa dogara a cikin ka ya Ubangiji."

## ABIN DA YASA AKE IYA RIBATO HAR MA 'YAN KWAMINIS ZUWA GA KRISTI

SIdan ku Kirista masu 'yanci kuka taimaka wa Ikilisiya ta karkashin kasa, zamu ribato 'yan kwaminis kuma mu canja

Fuskar duniya. Zata ribato su, saboda Allah baya halicci mutum don ya zama dan kwaminis ba. Ko kare ma yana so ya sami nasa kashin. Zuciyar 'yan kwaminis tana yin tawaye kan hakinta da kuma shirmen da suke gaskantawa.




*Masu bada gaskiya a Soviet Union suna amfani da radio domin yada labarunsu ta murya kuntattatu (VOM) don su shirya su kuma buga don su raraba kayayakinsu na Krista domin su sa Ikilisiya ta zama a fadake kwanakin duhu na komunis.*



НАУЧНЫЙ АТЕИЗМ

КЛЕРИКАЛЬНАЯ
РАДИОПРОПАГАНДА—
ОРУДИЕ
«ПСИХОЛОГИЧЕСКОЙ
ВОЙНЫ»

*Shekaru (30) talatin da suka wuce muryar kuntattatu (VOM) ta yi amfani da radio da kyau ta kuma watsa Bishara ga kamammu yan kurkuku masu bi, kamar yadda yake a bisa.*

Lokacin da dan kwaminis ke cewa babu wani ruhu sai jiki kawai wai bayan mun mutu zamu zama gishiri da sauran ma'adanai. Wannan ma ya isa a tambaye su, "yaya aka yi 'yan kwaminis a kasashen kwaminis da yawa suka bada rayukansu saboda abubuwa da suka yi imani da su? Dunkulen jiki kawai babu ruhu yana da ra'ayi? Ma'adanai suna iya bada kansu domin jin dadin wasu? Basu da amsar wannan tambaya. Sai kuma rashin imani. Allah baya halicci mutum ya zama mara imani ba kuma baya jimirin ganin marasa imani. Mun ga yadda rashin imanin shugabanin Nazis ya rushe, wadansu daga cikinsu suka kasha wasu kuma suka tuba suka furta zunubansu.

Akwai wani abu game da yawan shaye-shaye kasashen kwaminis. Akwai yunwar rayuwa mai fadi wadda kwaminisanci baya iya basu. Talakawan Rasha suna da zuciyar bayarwa hannu sake. Kwaminisanci ba shi da zurfi wajen al'amuran rayuwa. Yana neman zurfafan al'amura na rayuwa kuma baya samu a ko'ina, yana nema har a cikin barasa.yana bayyana fargabansa cikin rayuwa ta wurin shan barasa da kuma rayuwa cikin riya. Barasa tana ba zuciyarsa'yanci na kankanen lokaci amma idan za ya iya gano gaskiya ita ce zata bashi'yanci na dindindin. A Bucharest, lokacin da Rashawa suka mamaye kasar na taba jin lallai ne in shiga bah. Na kira matata mu tafi tare. Lokacin da na je nag a wani kaftin na Rasha rike da bindiga yana yiwa kowa barazana, yana cewa a karo masa giya. Mai bah din yaki kara masa, saboda ya rigaya ya bugu. Mutane suna ta zaman dardar. Na je wurin mai bah din, da yake na san shi n ace ya ba kaftin din nan giyar da yakeBukata,na yi alkawarin zan zauna da shi kuma in ga cewa ya yi shiru baya tada hankali ba.
Aka yi ta kawo mana giya kwalba bisa kwalba. A bisa teburin akwai kofi uku. Sai kaftin din nan ya cika duka kofin uku ya shanye su duka. Ni da matata babu wanda ya sha. Ko dayake ya shawu sosai duk da haka hankalinsa na aiki. Ya

rigaya ya saba da barasa. Na yi Magana da shi game da kiristi kuma ya saurara da kyau fiye da yadda na yi zato.
A karshe sai ya ce," yanzu ka fada mani ko kai wanene,Ni ma zan fada maka ko ni wanene. Ni firis ne na Ikilisiya mai ra'ayin mazan jiya kuma ina daya daga cikin wadanda suka fara yin musun Yesu kiristi lokacin da aka fara yi wa kirista tsanani a karkashin stalin a Rasha. Na je daga wannan kauye zuwa ẏancan don in bada lacca cewa babu Allah kuma a matsayina na firis dama yaudara nake yi. "Ni mayaudari ne haka nan kuma dukkan sauran firistoci. "haka na rika fada wa mutane. Na sami farin jini wurin kwaminis saboda himma ta har aka maida ni ofisa na 'yan sandan asiri. Horon da yake bani shi ne da wadannan hannun nawa nake kashe kirista, bayan na gana masu azaba. Yanzu kuma sai dai in ta shan giya ba tsaitsayawa domin in manta da abubuwan da na yi. Amma duk a banza abin na ta damu na."

'yan kwaminis da yawa sun kashe kansu. Haka nan gogaggun marubuta wakokin nan Essenin da Maiakovski da wani marubuci fadeev. Fadeev ba ya dade daga marubuta wani littafi da ya kira "farin ciki" ba a inda ya bayyana cewa farinciki na samuwa ta wurin yi wa kwaminisanci aiki tukuru. Shi kansa ya yi murna da abin har ya harbe kansa bayan ya gama rubuta littafin. Saboda karyar da ya yi tafi karfinsa. Joffe, tomkim- rikakun masu yaki domin kwaminisanci a zamanin mulkin zara Rasha basu iya daurewa da ganin hakikanin yadda kwaminisan ci yake ba. Su ma sun kare da kashe kansu.kwaminis basu da salama. Haka ma rikakkun masu mulkin kama karya nasu. Stalin bai sami salama ba. Bayan ya kashe kusan dukkan tsofoffin abokan sa, ya kasance cikin tsoron kada a sa masa guba a kashe shi. Yana dakunan kwana guda takwas wadanda ke da makulli irin na randar kudi ta banki. Babu wanda ya taba sanin ko wanne daki zai kwana daga cikin wadannan dakuna. Bay a taba fara cin abinci ba sai bayan wanda ya kawo masa ya dandana a gabaansa. Kwaaminisanci baya taba sa wani farin ciki ba har ma shugabannin kama-karya na su. Suna matukar bukatar Kiristi Yesu.

Idan muka hambare kwaminisanci, ba wadanda 'yan kwaminis ke gana ma azaba kawai zamu 'yantar ba, amma har ma da su 'yan kwaminis din kansu.

Ikilisiyar karkashin kasa atana wakiltaar babbar bukata ta mutanenmu da aka bautar. Ku taimaka mata.

* * *

Babban abin da Ikilisiyar karkashin kasa ta yi fice akansa shine amincinta cikin bangaskiya.

Wani ma'aikacin bishara wanda ya yi fice a karkashin "George" ya fada a cikin littafinsa game da "Allah a karkashin kasa" cewa.

Wani kaftin na sojan Rasha ya zo wurin wani mai wa'azi a kasar Hungary, ya roki ya gana da shi a kadaice. Sojan dai wani dan saurayi ne wanda yana jin irin nasarar da yake samu. Lokacin da suka shiga wani dan daki suka rufe sai ya kada kai wajen giciyen da ke rataye bisa bango.

Yace, "ka sani wancan abin karya ne, wata dabara ce kawai ku masu wa'azi ke mora domin rudar matalauta yadda masu hannu da shuni zasu ji saukin danne talakawa. Yanzu dai mu kadai ne ka fada mani gaskiya cewa baka taba gaskantawa cewa Yesu Kiristi Dan Allah ne ba." Sai mai wa'azin ya yi murmushi ya ce, "Amma ya kai dan saurayi na gaskanta wannan gaskiya ne. Gaskiya ne Yesu Dan Allah ne."

Sojan ya ce, "Ba a yarda ka yi wasa da hankali na ba, don ba wasa nake yi ba. Kada ka tsaya kana yi mani dariya." Sai ya ciro bindiga daga aljihunsa ya dana ta ya dunguna wa wannan mai wa'azi
yace "Idan baka yarda cewa Yesu ba Dan Allah bane zan harbe ka." Sai mai wa'zin nan ya ce, "Ba zan iya yin musun wannan ba domin gaskiya ne Ubangijinmu Yesu hakika Dan Allah ne."

Sai kaftin din nan ya jefar da bindigar sa kasa, kuma ya rungume wannan mutumin Allah ya yi kuka ya ce, "Gaskiya ne, Gaskiya ne, ni ma na gaskanta da haka, amma ban tabbatarwa cewa mutane na iya
mutuwa saboda wannan bangaskiya ba, sai yau da na gano da kaina. Na gode maka. Ka karfafa bangaskiya ta. Yanzu ni ma ina iya mutuwa domin Kiristi don ka nuna mani yadda ake mutuwa dominsa."

Na san wasu abubuwa makamancin wannan da suka faru. Lokacin da Rashawa suka mamaye kasar Rumania, wasu sojoji su biyu suka shiga wata majami'a da bindigoginsu a hannu. Suka ce, "Ba mu gaskanta da bangaskiyarku ba. Duk wadanda ba su yi watsi da wannan bangaskiya ba zamu harbe shi take. Wadanda suka yi musun bangaskiyarsu su koma hannun dama." Wasu suka koma hannun dama, sai suka umurce su su tafi gida. Wadanda suka yi musun aka barsu suka ruga gidajensu domin su tsira da rayukansu. Lokacin da wadannan sojoji 'yan Rasha suka ga an bar su da wadanda suka ki musun bagaskiyarsu sai suka rungume su, suka fada masu cewa su ma Kirista ne, amma suna so su yi zumunta ne kawai da wadanda suke shirye su mutu domin gaskiya."

Irin wadannan mutane sun yi yaki domin bishara a cikin kasarmu. Kuma sun yi fada ba domin bishara kawai ba, har da afada domin samo 'yanci.

A gidajen Kiristoci da yawa a kasashen yamma suna kashe awoyi wajen sauraren kide-kide na duniya. A gidajenmu ana iya jin kide-kide masu kara amma domin su rufe maganar bishara da muke yi kuma da aikin Ikilisiyar karkashin kasa yadda makwabta ba zasu ji su kaiwa 'yan sandan asiri rahoto ba.

Masu bi namu suna jin dadi duk lokacin da suka yi sa'ar saduwa da Kirista na ainihi daga kasashen yamma.

Wanda ya rubuta wadannaan layuyuka ba wani mutum ba ne. Amma ni ne muryar wadanda ba su da murya, wadanda aka sanyawa takunkumi kuma ba taba wakiltar su a kasashen yamma ba. A cikin sunansu ina rokon a maida hankali sosai cikin bangaskiya da kuma fuskantar matsalolin Kiristiyaniti. A cikin sunansu ina rokon addu'oin ku da kuma taimako na kowanne iri ga amintattu cikin bangaskiya na Ikilisiyar karkashin kasa wadanda ke shan tsanani a kasashen kwaminis.

* * *

Zamu yi nasara da kwaminis. Da farko dai saboda Allah yana wajenmu.

Na biyu, saboda sakonmu yana taba bukatu mafiya zurfi na zukatan mutane.

'Yan kwaminis wadanda suka taba zuwa kurkuku a karkashin Nazis sun furta amani cewa sun yi addu'a a lokacin tsanani. Na ga hafsoshi 'yan kwaminis suna mutuwa da kalmomin nan 'Yesu, Yesu" a lebunansu.

Zamu yi nasara saboda dukan al'adun mutanenmu na goyon bayan mu. Rashawa suna iya hana dukkan rubuce rubucen zamani na Kirista. Amma akwai litattafan Tolstoi da Dostoievschi, kuma mutane suna samun hasken Kiristi a cikinsu. Haka nan yake da Geothe a Jamus ta Gabas, Szienkiewicz a Poland da kuma sauransu. Marubucin da yafi rika a Rumania shine Sadoveanu. 'Yan kwaminis sun bugan littafinsa mai suna. "The Legend of Saints." Amma har ma karkashin wannan suna, misalan rayukan tsarkaka da aka bayar sun zuga mutane.

Basu iya kawar da zane-zanen Raphael, Michaelangelo, Leonardo da Vinci daga tarihi na marubuta. Wadannan hotuna suna Magana a kan Kiristi.

Duk lokacin da na yi Magana da dan kwaminis game da Kiristi, yunwar ruhu dake cikin birni zuciyars ake taimaka mani.

Abin da ya fi yi masa wahala shine kada ya amsa tambayoyi na. Babbar wahalarsa duka shine yadda za ya taushe muryar lamirinsa wadda take goyon baya na. babbar wahala shine yadda za ya taushe murya lamirinsa wadda take goyon baya na.

Na san wani furofesa na Marisacin wanda, kafin ya bada lacca ta arnanci. Na san wasu 'yan kwaminis dake zuwa taro a asirce can da nisa. Lokacin da aka gano su, sai suka yi karya cewa su ba su je taro na karkashin kasa ba. Daga nan suka yi kuka da bakin ciki da kuma da-na-sani saboda rashin gaba-gadi da suka nuna wajen tsayawa bisa bangaskiyarsu wadda ita ce ta sa har suka halarci taron, su ma fa maza ne. Da zarar mutum ya gane gaskiya ya kuma tuba, bangaskiyarsa zata yi ta girma. Mun tabbata cewa zata yi nasara saboda mu 'yan Iklisiyar karkashin kasa mun ga yadda take yin nasara.

Kiristi yana kaunar 'yan kwaminis. Ana iya, kuma dole a ribato su zuwa ga kiristi. Ikilisiyar karkashin kasa wadda ke a kasar kwaminis ita ce kadai wadda ke iya ribato su. Duk wanda ke so ya biya muradin Yesu kiristi na ceto ga rayukan dukkan 'yan adam, Lallai ya sa hannu wajen rike Ikilisiya ta karkashin kasa a cikin aikinta. Yesu ya ce. "ku koyawa dukkan al'ummai. "Ba ya ce kada mu shiga kasar kwaminis ba. Yiwa Allah aminci da kuma Umurni mafi Girma ya sa mu kokarin kai bishara ga 'yan kwamins wadanda aka bautar.

Muna iya kai masu bishara ta wurin yin aiki tare da Ikilisiya ta karkashin kasa, wadda ta ke a can.

## IKILISIYAR KARKASHIN KASA TA KUNSHI KUNGIYOYI UKU: DA FARKO FASTOCI DA MA'AIKATAN BISHARA WADANDA KWAMINIS SUKA TSIGE DAGA IKILISIYOYINSU

Akwai Kungiyoyi uku da Ikilisiyar karkashin kasa wadda ke a kasashen kwaminis ta kunsa. Kungiyar farko ta kunshi dubai bisa dubai na fastoci da ma'aikatan bishara wadanda aka kore su daga Ikilisiyoyisu, aka kawar da su daga dumakin su saboda sun ki gauraya bishara da kwaminisanci.

Da yawa daga cikin irin wadannan fastoci da ma'aikatan bishara sun taba yin zaman gidan yari na shekaru kuma sun sha azaba saboda bangaskiyarsu. An sako su kuma nan take suka koma aikin bishara a asirce kuma da himma suna yada bishara a Ikikisiyar karkashin kasa. Ko dayake 'yan kwaminis sun rufe majami'unsu ko kuma an canja su da wasu wadanda suke goyon bayan kwaminis, sun cigaba da aikinsu har ma fiye da, ta wurin yin wa'aza a asirice cikin tarurukan da ake yi a boye a cikin rumbuna,cikin daji da sauransu da dare ko kuma ko 'ina masu bi suka taru a asirce. Wadannan mutane sune jarumawan bangaaskiya wadanda ba zasu taba daina bishara ba, kuma wadanda tsoron dauri da azaba.

## NA BIYU MEMBOBIN IKILISIYA

Kashin na biyu daga cikin kungiyoyi da wannan Ikiklisiya ta kunsa shi ne na membobi masu dimbin yawa wadanda suka bada kansu ga kyautata bishara. Ina so a fahimta cewa babu kirista rabi-da-rabi ko kuma raggo a cikin kiristocin dake a Rasha ko China. Farashin da kirista suke biya domin kasacewarsu kirista ya yi yawa. Abu na gaba damu tuna shine ko dayake tsanani yana haifar da kirista nagari - kirista masu shaida bishara masu ribato rayuka zuwa ga kirista ya koma kansu saboda ya haifar da sayayyun kirista wadanda suka bada ransu irin yadda ba sosai ake samun haka ba a kasashen da kirista suke da 'yanci. Wadannan mutane basu iya fahimtar yadda mutum za ya zama kirista kuma ba ya son ya ribato kowanne mutum ya hadu da shi. Jaridar sojan Rasha, mai suna Red Star ta zaigi kiristocin Rasha cewa, "Masu bautawa kirista suna so su kuma kowa su shigar cikin kungiyarsu. "Amma hasken Yesu kiristi dake cikinsu ke jawo masu kauna da mutunci a wurin mutanen gari da makwabatansu. A kowanne kauye ko gari, kiristoci aka fi nunawa so da kauna. Lokacin da wata ta kamu da rashin lafiya mai tsanani har ba ta iya lura da iyalinta, sai mata kirista sun zo sun rika lura da yaranta. Lokacin da namijin ba shi da lafiyar har ba ya iya faskare, sai kirista maza su zo su yi masa hidima.

Suna rayuwa irin ta kirista na ainihi shi ya sa lokacin da su ka fara shaida bishara mutane suna sauraransu kuma sun bada gaskiya sabonda sun gan kiristi a cikin rayuwansu.Tun da babu mai iko yin Magana a cikin majami'a sai fasto mai lasin, miliyoyin tsayayyun kirista a kowace kusurwa a kasashen kwaminis suna ribato rayuka zuwa ga kiristi, suna shaida bishara a kasuwa, a wuraren diban ruwa a kauyuka ko 'ina suka nufa.

Jaridun kwaminis sun shaida cewa mafauta kirista suna saka kasidu na bishara cikin takarda da suke kunshe naman da suke sayarwa. Gidajen jaridu na kwaminis, sun shaida cewa Kiristan da suke aiki a madaba'u na kwaminis suna komawa da dare su buga takardun Kirista da yawa kuma su rufe, su koma gida kafin gari ya waye. Kuma gidajen jaridu na kwaminis sun kuma-shaida cewa ya'yan Kirista a Moscow sun sami bishara ta wata hanya kuma suka juyi wasu sassa da hannu. Daga nan sai yaran su saka abin da suka juya a cikin aljihun rigunan malamansu wadand ke a rataye a wurin ajiya a makarantar. Membobin Ikilisiyar karkashin kasa suna da iko, himma, masu ribato rayuka wadanda suna nan a kowace kasar kwaminis. A kasar Cuba, mishanari na da, sun ce, 'yan Ikilisiya sun fara gundanar da Ikilisiya asirce dashik gwamnatin kwaminis ta kame faston ta ta tsare, wasu kuma an kore su, kana wasu kuma gwamnati ta maye gurbin wasu da fastoci masu taka rawar 'yan kwaminis. Wadannan miliyoyin bayin Allah wadanda suka sadakar da rayukansu ga kiristi wadanda ke cikin wannan Ikilisiya wutar tsanani ta 'yan kwaminis wadda 'yan kwaminis ke sa ran zata kawar dasu, a maimako haka ta tsarkake su.

**NA UKU FASTOCI DA MASU WA'AZI NADIN GWAMNATI WADANDA BASU YARDA SU KAUCEWA GASKIYA KO SU KAME BAKINSU WAJEN WA'AZI GASKIYA BA.**

Kashi na uku na kungiyoyi da Ikilisiyar karkashin kasa ta kunsa. Ita ce kungiyar fastoci masu aminci cikin harkar gwamnati amma ana ja masu linzami kuma ana rufe masu baki: Ita dai Ikilisiya karkashin kasa tana da dangantaka da Ikilisiya mallakar gwamnati kwaminis. A kasashen kwaminis da yawa, kamar su Yugosavia, Poland da Hungary, fastoci nadin gwamnati da yawa suna aiki a Ikilisiya karkashin kasa a asirce. A wasu kasashen ma, da Ikilisiyar karkashin kasa da Ikilisiya mallakar gwamnati sun garwaye. Wadannan fastocin basu da izinin yin Magana kiristi a waje sai cikin 'yar karamar majami'ar su. Ba su da izini tara yara da matasa. Wadanda ba kirista ba suna tsoron su je kusa da su. Ba a yarda wadannan fastoci su yi wa membobinsu marasa lafiya addu'a a gidajensu ba. Dokokin gwamnati sun yi masu shinge ta kowace lokaci wadannan fastoci suna gamuwa da janlinzami daga gwamnati wanda ke maida 'yancin yin ibada ba'a, saboda haka wadannan fastoci sukan yi karfin hali su yi kasadar gudanar da wa'azi a asirce wanda ya wuce iyakar da 'yar kasaminis suka masu. Wadannan fastoci suna gudanar da bishara ga yara da matasa a asirce. A asirce suna yin bishara a gidaje kirista. Suna samu litatafai na kiristiyaniti a asirce suna kuma rarraba wadannan litartafai ga rayuka masu yunwar Ruhu. Suna na yin watsi da iyakar da gwamnati ta sa masu yin wa'azi ga rayuka yunwar Ruhu Maisarki dake kewaye da su. A waje kamar masu biyaya da kafirci gwamnati, amma asirce suna sayar da ransu domin yadda maganar Allah a asirce. Kwanannan a Rasha gwamnati ta gano da yawa daga cikin irin wadannan masu wa'azi ta kuma kame su. An basu shekaru masu yawa a gidan sarka.

Wannan itace kungiya ta uku cikin muhimman kungiyoyin da Ikilisiyar karkashin kasa ta kunsa. Masu bishara na da wadanda kwaminis suka kora kuma suka yi wa tsanani: membobin Ikilisiya da fastoci nadin

gwamnati wadanda suke gudanar da aikin bishara a asirce fiye da iyakar da 'yan kwaminis suka sa masu dukkan wadannan suna aiki da Ikilisiyar karkashin kasa. Kuma wannan Ikilisiya zata cigaba har ranar da aka kawar da kwaminisanci: A wasu kasashe, wani sashen yafi wani kokari amma dukkansu suna nan, suna yin aiki domin Kiristi a cikin hadarin gaske. Wani mutum wanda yake yawan zuwa kasashen kwaminis kuma wanda yake da sha'awar tambayoyi kan addini, ya dawo ya kuma rubuta cewa ba ya taba haduwa da wata Ikilisiyar karkashin kasa ba.

Abin yana kama da zuwa Afirka ta tsakkiya cikin kabilu marasa ilimi kuma ka dawo ka ce, "Na yi bincike sarai. Na tambaye su duka idan suna Magana da harsuna, Dukkansu sun ce ba su yi". Amma gaskiyar ita ce, dukkansu suna Magana da wasu harsuna ba tare da sun san cewa maganganun da suke yi cikin harsuna bane.

Kiristan farko basu sani cewa su Kirista ba ne. Idan da ka tamabaye su game da addininsu, da sun baka amsa cewa su Yahudawa ne, Israilawa ne, masu bada gaskiya ga Kiristi a matsayinsa na Masihina, yan'uwa, tsarkaka kuma 'ya'yan Allah ne. Sunan nan "Kirista" an sa masu ne daga baya a Antiyok.

Babu wani mai akidar Luther da ya sani cewa shi Lutheran ne. Luther kansa ya nuna rashin amincewa da wannan sunan. "Ikilisiyar karkashin kasa" suna ne da 'yan kwaminis da kuma mutanen yamma masu bincike akan halin da addini yake ciki a kasashen kwaminis suka ba kungiyar masu bi na ainihi da suka kafa a asirce a kasashen 'yan kwaminis domin rura bangaskiyarsu. Membobobin wannan Ikilisiya basu kira kungiyarsu da wannan sunan. Suna kiran kansu Kirista, masu bada gaskiya ga Yesu Kirista, da kuma 'ya'yan Allah. Amma suna gudanar da aiki a karkashin kasa, suna yin taruruka asirce, suna yada bishara a taruruka masu hadari wadanda wani lokacin har ma baki wadanda suke cewa sun ga Ikilisiyar karkashin kasa suke halarta.

Wannan suna ne wanda baya dace ba wanda abokan gaba da kuma wadanda suke kallon wannan kungiya daga waje suke bada.

Kana ratsa dukkan kasashen yammacin duniya ba tare da ka ga wata alama ta 'yan kungiyar leken asiri na Rasha ba, amma wannan ba ya nuna cewa ba su ba. Sai dai baya zama sakarci bane su nun kansu ga matafiya.

A babi na gaba na dauko wasu kalamai daga jaraidun Tarayyar Rasha wadanda suke tabbatar da cewa akwai Karin muhimmanci na wannan kungiya ta Ikilisiyar karkashin kasa.



# BABI NA SHIDDA:SIX

## YANDA KRISTANCI KE CIN NASARA AKAN KWAMINISANCI

Na fadi abin da muka gamu da shi cikin yada bishara a asirce a cikin sojojin Rasha da kuma kasar kwaminis ta Rumania. Na yi roko gare ku, ku taimaka a yi wa'azi kiristi ga 'yan kwaminis da kuma mutanen da ake dannewa. Kalubala ta nuna hangen nesa kuma za ta yiwu?Tana da ma'ana?

Yanzu haka akwai Ikilisiyar karkashin kasa a Rasha da sauran kasashen kwaminis? Har yanzu yana yiwuwa a gudanarda aikin bishara ta karkashin kasa a wadannan kasashe? Muna iya bada amsoshin wadannan tambayoyi da labari mai dadi.'Yan kwaminis suna bukin murnar cika shekara hamsin da kafa gwamnati, amma nasara su ta fadi. Kiristiyanti ya yi nasara ba da kwaminisanci ba. Gidajen jaridu na Rasha, wadanda kungiyarmu ta rarake sarai, cike take da labarin Ikilisiyar karkashin kasa. Karon farko **Ikilisiyar karkashin kasa ta yi karfi har ma tana iya yin aiki kusan a bainar jama'a, tana tsorotar da 'yan kwaminis.** Wani bayani da muka samu daga wasu kafofi sun tabbatar da rahotannin gidajen jaridu na 'yan kwaminis.

Ka tuna, Ikilisiyar karkashin kasa tana kama da babban dutse na kankara. Yawancin jikin dutse yana karkashin ruwa, amma wani dan sashe ya dono kai a sarari. A cikin shafuffukan dake tafe na bada dan gajeren bayani na labaran da suka fi muhimmanci.

### GOSHIN DUTSEN KANKARAR.

Ran 7 ga watan Nuwamba 1966, a wani gari mai suna Suhumi (Caucsus) Ikilisiyar karkashin kasa ta yi babban taro a sarari masu bi da yawa suka zo daga sauran birane don halartar taron.

Bayan an yi kira masu son su tuba su fito mutane arba'in da bakwai matasa suka zo suka karbi Kiristi kuma aka yi masu baftisma nan take a cikin tekun da ake kira Black Sea kamar gadda aka rika yi a zamanin Litafi Maitsarki.

Da, babu wani lokaci na bada ka'idodi. Bayan an share shekaru hamsin a karkashin mulkin firi'aunanci na kwaminis, babu Littafi Maitsarki ko wasu litattafai na addinin Kirita kuma babu saminari ko Baibul Skul, kuma masu wa'azi na Ikilisiyar karkashin kasa basu da horo na aikin wa'azi. Amma ko Filib ma ba deacon ba ne. Kuma lokacin da wani baba, wanda me yiwuwa ne ya yi awa yana Magana da shi, ya roke shi ya ce,

"Duba ga ruwa, me za ya hana a yi mani baftisma?" Filibus ya ce, "Idan ka bada gaskiya da dukan zuciyarka, sai a yi: Ya amsa ya ce, ina bada gaskiya Yesu Kiristi Dan Allah ne ... suka shiga ruwa ... ya yi masa batfisma." (Ayyukan Manzanni 8:36-38).

Akwai wadataccen ruwa a tekun "Black Sea" kuma Ikilisiyar karkashin kasa ta fara yin irin yadda masu bi suka yi a zamanin Littafi Maitsarki.

Wata mujallar malamai mai suna Uchitelskaia Gazeta ta 23 ga Agusta 1966, ta bada labari cewa a Rostov-on-Don, 'yan Baftis wadanda suka ki yin rijistar majama'arsu bisa ga dokokin gwamnatin kwaminis kuma suka ki yin biyayya da shugabannin da kwaminis suka nada masu suka shirya zanga-zanga a bisa titina.

Rana daya ga watan Mayu, kamar yadda Yesu ya yi mu'ujuzai ranakun asabaci ya karya kaidodin farisawa abokan adawarsa, Ikilisiya ta karkashin kasa ma, ta zabi lokacin bukukuwan 'yan kwaminis domin karya dokokin kwaminis.

Daya ga watan Mayu rana ce da kwaminis suke yin buki na babbar zanga-zanga wadda dole ne kowa da kowa ya halarta. Amma a wannan karon kungiya wadda ita ce ta biyu a karfi cikin Rasha Ikilisiyar karkashin kasa ta bayyana a bisa titi a wannan ranar.

Masu bi dubu daya da dari biyar suka fito kan titi. Abin da ya matsa masu har suka fito shi ne kaunar Allah kadai. Sun sani suna cikin hadarin yin hasarar 'yancinsu. Sun sani yunwa da azaba iri-iri suna jiransu a kurkuku.

Kowanne mai bi dake cikin Rasha ya san da wata kasida da ake kira "Secret Manifesto" wadda Evangelical Christians suke bugawa a asirce a Narnaul. A cikin wannan mujallar an bayyana yadda 'yar uwar Hamara ta kauyen kulunda, ta sami
labari cewa mai gidanta ya mutu a kurkuku. Yanzu ita gwamruwa ce da 'ya'ya hudu kanana. Lokacin da aka kawo gawar mijin na ta tana iya ganin kufan ankwa a hannuwansa. An kona hannuwansa, da kafafunsa da kuma tafin kafafunsa, kasan cikinsa akwai shaidar yankan wuka. Kafasa ta dama ta kumbura. A duka kafafun akwai shaidar duka. Dukkan jikin cike yake da raunuka da aka ji masa da duka.

Kuma suna sani cewa wannan jarumin bangaskiya da ya bada ransa ga Allah wata uku kawai da suka wuce bayan tubansa, an rufe shi a gaban babban taron masu bi wadanda suka rika daga kwalaye masu rubutu haka."Rai gare ni shine Kiristi kuma mutuwa ribace." "Kada ku ji tsoro wadanda suke iya kashe jiki wadanda ba su iya kashe ruhu." "Na gani a karkashin bagadi wadanda aka kashe saboda Maganar Allah."

Misalin wannan jarumin bangaskiya ya zuga wadanda ke a Rostov-on-Don. Suka fito suka yi tururuwa a bisa titi kewayen dan gidan. Mutane a ko'ina wasu a bisa itatuwa kamar zakka na zamanin da. Mutane tamanin suka tuba a wurin kuma dukkansu matasa. Daga cikin wadannan Matasa, ashirin da uku da 'yan Komsomols ne (membobin kungiyar matasan kwaminis).

Masu bin suka ratsa birni zuwa rafin don a inda aka yi baftisma.

.Motoci cike da 'yan sandan kwaminis suka zo suka kewaye masu bin a bakin rafin.Suna so su kame wanda yake shugabantar taron. (Basu iya kama duka mutane dubu daya da dari biyar ba).

Nan da nan masu bin suka durkusa suka yi addu'a ga Allah ya kare mutanensa kuma ya basu izinin su sami yin sujada a wannan ranar. Daga nan 'yan uwa suka tsaya suka kewaye shugabannin taron da sa zuciyar zasu hana 'yan sanda su kama su. Al'amarin ya yi tsanani.

Uchitelskaia Gazeta ya bada rahoto cewa kungiyar Baftis wadda aka haramta a Rostov tana da madaba'ar buga takarda a boye. (Kalmar nan Baftist a wurin mutanen Rasha tana nufin dukan darikun da ba 'yan Katolika ba). na buga takardun kiran matasa su tsaya akan bangaskiyarsu. A daya daga cikin irin wadannan takardu da ake bugawa a boye, ana yin kira ga iyaye Kirista su yi, abin da nake tsammani yana da kyau kwarai. "Su rika kai 'ya'yansu zuwa wurin jana'iza domin su koyi kawar da damuwa game da abubuwa masu wucewa." An yi kira ga iyaye su rika ba 'ya'yansu ilimi na Kirista a matsayin maganin arnanci da musun Allah wadanda ake gurbata zukatansu da shi a makarantun kwaminis.

Uchitalskaia Gazeta ta rufe bayaninta da tambaya, "Menene ya sa malamai suke cudanya da iyalan da aka maida 'ya'yansu sakarkaru (ta wurin addini)?"

Wata mujalla kuma mai suna "Teachers Magazine" ta bayyana abin da ya faru a shari'ar ma'aikata wadanda aka yi wa baftisma a asirce.

Matasa masu bi da aka kirawo su bada shaida suka nuna wa kotun kwaminis reni. Suka rika nuna fushi da kuma zakewa. Matasa 'yan mata kallo suka nuna sha'awa ga wadannan matasa da kuma rashin amincewa da arna."

Membobin Ikilisiyar karkashin kasa suka tarbi hadarin duka da dauri suka je roko a kara masu 'yanci a hedkwatar jami'yar kwaminis a Rasha.

Muna da wata kasida da wani kwaminis boye na Evangelical Baptist Churches na Tarayyar Rasha suka rubuta. Gaba da takunkumin da kwaminis ke makalawa "Baptist Union" karkashin jagoranci kareV, wanda yake yabon

tausayin 'yan kwaminis masu kisan kirista kuma ya daukaka 'yancin dake akwai a wata mujalla Soviet Life Today (No. 6, 1963). An yi sumogal kasidar zuwa kasashen yamma a asirce.A cikin wannan mujialla an bamu labarin zanga zanga da aka yi a bainar jama'a a brini Mascow kansa.na fasarta wannan daga abin da aka tsara:sadarwa ta gaggawa yan uwa mazada mata, Albarka a gare ku da kuma salama daga Allah ubanmu da Ubangijinmu Yesu Kiristi muna hanzarin fada maku cewa wakilan ikilisiyoyin Evangelical Baptist Christians, wadanda yawansu ya kai dari biyar, wadanda suka yi tattaki zuwa Moscow ranar 16 ga wata Mayu 1966 domin su katse hanzarin mahukumtan kwaminis na koli, sun je har ginin kwamitin tsakkiya na jami'yar kwaminis ta Tarayyar Jamhuriyar Rasha, da rokon a karbe su kuma a saurare su. “Muka mika kukanma a rubuce ga babban sakataren jam'iya, Brezhnev.”

A cikin “manifesto” an ce, wadannan mutane dari biyar sun tsaya a gaban ginin dukan yini. Wannan ne zanga-zanga a bayyane ta farko mai gaba da kwaminis da aka yi a Moscow. Kuma wakilan ikilisiyar karkashin kasa ne suka yi ta, A karshen yinin, sun mika kukansu na biyu zuwa ga Brezhnev wanda a ciki suka yi kukan cewa wani dan uwa mai suna Stroganov ya ki mika wa Brezhnev bukatunsu kuma ya yi ma lafiyarsu da'yancinsu barazana.

Wadannan wakilai dari biyar sun kasance a titin dukan dare. Mutane suka rika tuka motoci suna bi kusa da su domin su watsa masu laka kuma su zage su. Ko dayake an yi ruwa kuma an yi masu wulakanci irin wannan, sun tsaya a wurin har wayewar gari a gaban wannan gini na Jami'yar Kwaminis.

Kashe-gari an shawarta cewa su duka dari biyar din nan su shiga cikin ginin domin saduwa da kananan jami'an jami'iyar kwaminis, amma ganin cewa masu bi da suka taba ziyartar mahukumta an basu kashi lokacin da suka shiga ginin inda babu wasu shaidu saboda haka sai wakilan suka ki shiga suka cigaba da jira Brezhnev ya karbe su.”

Daga nan sai abin da babu makawa za ya faru, ya faru. Da karfe 1.45 na maraice, motocin safa-safa ashirin da takwas suka dira kuma aka fara gallazawa masu bi. “Sai muka yi da'ira ko kawanya muna rike da hannun juna, kuma raira waka mai cewa:” The best days of our life are the days when we can bear a cross” ma'ana, Ranakun da suka fi dadi a rayuwarmu sune ranakun da muka dauki giciye. Sai'yan sandan asiri suka shiga dukanmu ba-ji-ba-gani. Suka ja wasu 'yan uwa zuwa safa safa ta hanyar kama gashin kansu. Lokacin da wadansu daga cikinsu suka yi kokarin barin wurin, an yi masu dan Karen duka har suka galabaita. Bayan sun cika safa-safa da wadannan masu bi, sai suka kai su wani wurin da ba wanda ya sani. An ji wakokin 'yan uwa na fitowa daga safa-safa na 'yan sandan asiri. Duk wannan ya faru a kan idanun dimbin jama'a.”

Yanzu kuma sai wani abu mai kyau kwarai ya biyo baya. Bayan an kama mutanen nan dari biyar kuma tabbaci hakika ana ta gana masu azaba, sai yan uwa G. Vins da Horev, (makiyaya na ainihi na tumaki Kiristi) har yanzu suna da gaba-gadin zuwa wannan kwamitin Tsakkiya na Jami'iyar kwaminis kamar yadda ya faru baya an kama Yohanna mai yi Baftisma, Yesu ya fara wa'azi a bainar jama'a wurin da aka kama shi kuma da kalmomin da saboda sune Yohanna ke shan wahala yana cewa, “ku tuba domin Murki sama ya kusa.” Vins da Horev sun nemi su san inda Kiristan da aka kama suke kuma suka bukaci a sako su. Wadannan 'yan uwa biyu masu suna a kurkuku Lefortovskaia. Wannan abin da ya faru ya razana kirista na Ikilisiyar karkashin kasa? Ina! Nan-da-nan wasu kiristan suka sake yin kasadar kira a basu 'yanci, suka buga labarin dake gabanmu, suka bada labari abin day a faru suna cewa a gare su, “Gama a gareku am bayas sabili da Kiristi, ba bada gaskiya gareshi kadai ba, amma shan wahala kuma dominsa.” (Filib. 1:29) sun gargadi 'yan uwa, Domin kada kowa shi yi rauni saboda wadannan masifu, gama ku da kanku suka ambaci Ibraniyawa 12:2 kuma suka

kirawo masu bin suka ce, ku duba Yesu shugaban bangaskiyarmu da mai ciki ta, shi wanda ya jimre da giciye domin farin zuciya da aka sa gabansa, yana rena kumya, ya kuwa zamna ga hannu dama na Allah."

Ikilisiyar karkashin kasa ta bayyana rashin amincewarta a Rostov da Moscow da kuma dukan Rasha. Suna yaki da yadda kwaminis suke gurbata zukatan , matasa da kuma yaki da munafukan shugabanni Ikilisiya nadin gwamnati wadanda suka rubuta labarinsu a cikin kasidarsu manifesto, " A zamanin nan, shaidan ke bada umurni kuma Ikilisiyar karya tana karbar dukkan shawarin da aka basu wadanda ke gaba da dokokin Allah." (an dauko daga jaridar Pravda Ukraini ta Oktoba 4th 1966).

Jaridar Pravda Vostoka ta buga shari'ar dan uwa Alesxei Nenerov, Boris Garmashov da Axen Zubox, wanda ya tsara kungiyoyin sauraron bishara da ake bazawa daga Amerika. Sun dauki wadannan sakoni a tef, wadda suke zagawa da shi daga baya.

Kuma an zarge su da cewa suna shirya tarurukan bishara a sirce da sunan yawon bude idanu. Ta wuri haka ne Ikilisiyhar karkashin kasa ta ke yin aiki kamar dai yadda Ikilisiyar farko ta yi a cikin kaburbura da ake kira Catacombs na Roma.

Jaridar Sovietskaia Moldavia ta 15 ga watan Satumba 1966, ta yi korafin cewa Iklisiyar karkashin kasa ta buga wasu 'yan litattafai. Suna taruwa a wuraren shakatawa na jama'a ko dayake doka ta hana, kuma suna zuwa daga wannan wurin zuwa wancan suna shaida Kiristi.

Wannan jarindar ce kuma ta tuno da yadda, a cikin jirgi kasa daga Reni zuwa Kirista, wasu matasa uku maza da hudu mata suka raira wakar Kirista mai cewa "Let us dedicate our youth to Christ" wato bari mu bada kuruciyarmu ga Kiristi. Mai bada rahoton ya ce sai da ya nuna rashin amincewa, saboda masu bi suna yin wa'azi a titin, da tashoshi, da cikin jirgin kasa da safa-safa kuma har ma a makarantun gwamnati. Wannan aikin Ikilisiyar karkashin kasa ne wadda ke cikin Rasha a yau.

A lokacin shari'ar wadannan Kirista an karanta hukumcin da aka yanke masu saboda an kama su da laifin yin wakar kirista a bainar jama'a, sai wadanda aka yankewa hukumcin suka durkusa suka ce, "Mun mika a kanmu cikin hannunka ya Allahnmu. Saboda wannan bangaskiya." Daga nan sai 'yan kallo, bisa jagorancin wani dan ganikashe-ni kirista Mr. Madan a kotun suka raira wakar da 'yan uwa suka yi wadda akanta ne aka yanke masu hukumcin dauri da azaba.

Ranar daya ga watan Mayu, Kiristanci akauyukan Copceag da Zaharovka ganin cewa basu da ginin majam'iu sai suka shirya sujada a sirce cikin daji. Suna shirya taruruka da sunan bukin tunawa da haifuwar wani cikinsu. (Da yawa daga cikin iyalin kirista masu Mutum hudu ko biyar zasu yi bukin kewayowar ranar haifuwarsu har sau talatin da biyar a shekara a matsayin hanyar rufe tarurukan asiri).

Babu wani kurkuku ko azabar da zata iya tsoratar da Kirista na Ikilisiyar karkashin kasa. Kamar yadda ya faru a Ikilisiyar farko, tsanani yana kara zurfafa sadaukar da kai.

Jaridar Pravda Ukraini ta 4 ga Oktoba 1966 ta yi Magana game da danuwa Prokofiev daya daga cikin shugabannin Ikilisiyar karkashin kasa a Rasha wanda dama ya taba zuwa kurkuku har sau uku, amma da zarar an sako shi sai ya cigaba da shirya Sonde Skul a asirce. Yanzu an kama shi.

Ya rubuta a manifesto da ake bugawa a asirce cewa, "Bada kai ga ka'idodin dan adam (yana nufin dokokin kwaminis) Ikilisiya mallakar gwamnati tana hana ma kanta samun albakun Allah."

Kada ku dauka cewa kurkukun kasashen kwaminis irin na kasashen yamma ne, a duk lokacin da kuka ji cewa an jefa wani dan uwa a kurkuku a Rasha. Kurkuku a kasashen kwaminis yana nufin yunwa, azaba da sangartar da hankali. Wata mujalla "Nauka I Religia " (kimiya da addini) Lamba 9 ta 1966 ta bada rahoto cewa Kirista sun baza litattafan addinin Kirista a cikin bango wata mujalla mai kama da "Look" ko "Time." Suna bada litattafai wadanda a bangonsu zaka ga an rubuta "Anna

Karenina" sunan wani littafin tatsuniya da Leo Tolstoy ya rubuta, amma a ciki ayoyin Litafi Maitsarki ne aka rubuta. Suna raira wakoki kamar wadanda muryoyi su suka yi kama da wakar "The Communist International," amma kalmomin na yabon Kiristi ne. (jaridar kazakstanskala Pravda, Yuni 30, 1966).

A cikin wata wasika ta asiri da aka buga Bafti nadin gwamnati sun lalata Ikilisiyar da bayinta na Farisawa suka bayar kamar yadda manyan Firistoci da Farisawa suka bayar da Yesu ga Bilatus."Amma aminitaciyar Ikilisiyar karkashin kasa suna cin gaba da aiki.

Amaryar Kiristi tana cigaba da yi masa hidima. 'yan kwaminis da kansu sun yarda cewa abin da nake fadi game da cewa Ikilisiyar karkashin kasa zata ribato yan kwaminis zuwa ga kiristi gaskiya ne. ana ribato su.

Jaridar mai suna Bakinskii Rabocii (wato ma'aikatan Baku) ta 27 ga watan Afrilu 1966 ta buga wata wasikia ta Tania Cingunova (wani memba na kungiyar matasan kwaminis) wanda aka ribato shi zuwa ga kiristi. Mahukumtan kwaminis ne suka kwace wasikar. Wasikar tana kamar haka.



*Kara **akan** Fasakorin fita a Rasha (Russia) da aka sa hannu a 1453 wata **uwa** a Rasha (Russia) da aka cire yaranta ta wurin Jam'iyar komunis. **Laifinsu** ya zama ne idan sun kuskura su koya masu kaunar Yesu Kristi.*

Zuwa ga mama Nadia, ina maki da albarku daga kaunatacen Ubangijinmu. Mama Nadia, yana kaunata sosai. Mu ba kome bane a gabansa. Mama Nadia, ina bada gaskiya cewa kin fahimci wadannan kalmomi. “Ka kaunaci makiyanka, ka albarkaci masu la'antar ka, ka yiwa masu kinka alheri kuma ka yi wa masu Cutarka addu'a.”

Da dai 'yan kwaminis suka sami wannan wasika, sai suka kama Peter Sereb rennikov dan uwa wanda ya kawo kuma wasu matasan kwaminis zuwa ga kiristi aka jefa shi cikin kurkuku. Jaridar kwaminis ta dauko wasu kalamai daga cikin jawabansa inda ya ce, 'Dole ne mu gaskanta da mai cetonmu a matsayin abu na farko da kirista za ya yi. A gare mu dokar da tafi kowace itace Litafi Maitsarki; baya ga wannan babu wani abu da muka yarda da shi. Dole ne mu hanzarta ceto mutane daga zunubi, musamman matasa. "Lokacin da aka fada masa cewa dokar Rasha ta hana fadawa matasa. Maganar Kiristi sai ya ce,"A gare mu Litafi Maitsarki ne doka" amsa da ta dace inda mugun arne ke mulki kama karya a kasar.

Daga nan jaridar kwaminis ta bayyansa wani mugun hoto wai matasa maza da mata suna raira wakokin ruhaniya, an yi masu baftisma kuma suna tsare munafukar koyarwa ta cewa wai a yi kaunar abokan gaba."

Jaridar Bakinakii Rabocii ta ce matasa da yawa maza da mata, wadanda suke da katin shaida na kasancewa memba na matasan kwaminis a gaskiyar kirista ne.jaridar ta kare labarinta da wadannan kalama: "Makarantun kwaminis basu da ido, sai gundura da kuma rashin haske har fastoci suna iya kware masu almairainsu daga fuskar malamai dabam-dabam.

**Jaridar kazakstanskain Pravda ta 30 ga Yuni 1966 ta gano cewa dalibin daya yi zara duka, kirista ne.**

Jaridar Kirgizskaia Pravda ta 17 ga Jannairu 1966 ta dauko wani kalami daga wata kasida da wata kirista 'yan Ikilisiyar karkashin kasa ta rubuta: "Bari mu hada karfi muna bada kokari da kuma yin addu'a, mu ceto 'ya'yanmu daga yaudara ta duniya.

An sami nasara a cikin wannan kokarin. Jaridar kwaminis ma ta shaida wannan. Kiristiyanti yana cigaba a cikin matasa.

Wata jarida daga Celiabinsk, Rasha, ta bayyana yadda wata 'yar kungiyar matasan kwaminis mai suna Nina ta zama kirista. Ta zama kirista ta wurin zuwa taro da kirista suke yi a asirce.

Mujallar Sovietskaia Justgitia lamba 9 ta 1966 ta bayyana irin wannan tari na karkashin kasa ta ce, " An yi taron ne da tsakar dare, a wani wuri a boye mutane sun fito daga wurare dabam-dabam. 'yan uwa suka cika dan dakin mai duhu wanda yake da silin kasakasa. Sunyi yawa har babu wurin da mutum za ya durkusa. Saboda rashin iska, 'yar fitilar da suke amfani da ita ta mutu. Suna ta zufa. Sa'annan kuma akwai wani a bisa titi yana dubawa koda 'yan sanda zasu zo. "Amma Nina ta ce a irin wannan taro aka karbe ta hannu biyu-biyu. "Suna da, kamar yadda nake da ita yanzu, bangaskiyar mai kawo haske bangaskiya cikin. Ubangiji Allah. Yana lura da mu. Bari mutanen komsomols wadanda suke son na su wuce ni ba gaisuwa. Bari su dube ni da reni su kira ni kamar suna mari na, "Baftis Bari su yi haka! Bani bukatar su."

Matasa 'yan kwaminis kamar ta da yawa sun yanke shawarar bautawa Yesu Kiristi har iyakar rayuwarsu a nan duniya.

Amsoshin da Kirista na Ikilisiyar karkashin kasa suke badawa duk lokacin da aka kawo su gaban kotun kwaminis daga Ruhu Maitsarki suke zuwa. Wani mai shari'a ya yi tambaya: "Menene ya sa kuke kama hankalin mutane zuwa ga haramtaciyar kungiyarku? Sai wani kirista ya amsa yace, "Burin mu shine mu ribato dukkan duniyar nan zuwa ga kiristi."

A wata shari'ar kuma mai shari'ar ya ce da yarinyar da ake tuhuma, "Addininku yana gaba da ilimi kimiya? Sai yarinyar wata daliba ce ta ce, "ka fi Einterin da Nowaton sanin kimiya? Su kuma masubi ne. duniyar mu tana da sunan Eintein. Na koya a makaranta cewa sunan wannan duniya shine Einstaininian Universe. Einstein ya rubuta cewa, "Idan muka tsarkake Yahudanci na annabawa da kuma kiristanci, kamar yadda Yesu Kiristi ya koyar da shi, daga abubuwan da suka shiga cikinsa daga baya, zamu sami addini wanda za ya iya ceton duniya daga dukkan mugunta.

. Jihadi ne na kowane mutum ya iyakar kokarinsa ya ga an kawo wannan nasara ta wurin addini." Kuma ka tuna da rikakken masanin halayyar dan adam paviov. Litattafanmu basu fada mana cewa shi kirista bane? Ko ma Karl Marx a cikin gabantarwa ta litafinsa mai suna "Das capital" yace "Kiristiyaniti, musammun ma irinna furotestant, shine addini nagari wanda ke iya canja halayen mutanen da zunubi ya lalata! Ina da hali wanda zunubi ya lalatar, Marx ya koya mani in zama kirista idan ina so in gyara wannan hali. Yaya kai da kake bin akidar Marx zaka shari'anta mani domin wannan?

Abu mai sauki ne a fahimci abinda mai shari'ar ya rasa abin da za ya ce da ita.

Gama dai da wannan zargi na gaba da ilimin kimiya, wani kirista ya amsa a gaban kotu cewa, "Na tabbata mai Sharia, kai ba babban masanin kimiya ba ne kamar Simp-son wanda ya gano Chloroform da kuma sauran magunguna. Lokacin da aka tambaye shi a ganinsa wane ya fi girma cikin duka abubuwa daya gano a chikin iliminsa, sai ya amsa ya ce.

"Ba Chloroform bane. Babban abin da na gano shine cewa ni mai zunubi ne kuma alherin Allah yana iya ceto na."

Rai da jininsu da su ke a shirye su bada domin bangaskiya su shine babbar hujjar da kiristiyaniti ke gabatarwa ta wurin **Ikilisiya karkashin kasa.**wannan Ikilisiya ta zama abin da wani **mashahurin** Misshanari a Afirka mai suna Albert Schweiter ya kira, "Zumuta mai tsarki ta mutanen da suke da shaidar wahala. "Zumuta wadda Yesu yake ciki. Ikilisiyar Karkashin kasa kanta hade yake ta wurin kauna zuwa ga mai cetonta. Wannan madaurin kaunar shine ya hada membobin Ikilisiyar da junansu. Babu wani a cikin duniyar nan da za ya iya samun galaba bisan su.

A cikin wata wasika da aka aika a asirce, Ikilisiyar karkashin kasa ta ce, "Ba mu yi addu'a don mu zama kiristan da suka fi sauran kirista, amma muna addu'a mu zama irin kiristan da Allah yake so mu zama: kirista masu kama da kiristi, wato kirista masu daukar giciye da yardar rai saboda daukakar Allah."

Da hikima kamar maciji, bisa ga koyaswar Yesu, kiristocin, koyaushe suna kin fadin ko su wanene shugabanninsu kome tambayar da kotu zata yi masu.

Jaridar PraVda (wato gaskiyar akan kasashen gabas) ta 15 ga watan Jannairu 1966 ta fadi yadda wata kirista mai suna Maria SeVciuk da aka tambaye ta wanda ya kawo ta ga kiristi sai ta amsa: "Allah ne ya jawo ni a taron mutanensa."Wani kuma ya tambaya, "Wanene taron shugaban ku? Amsa, "Bamu da shugaba dan adam."

Aka tambayi yaran kirista, wanene ya koya maku ku bar kungiyar yara ta kwaminis ku shiga kungiyar kirista. "Sai suka amsa, "Mun yi ne don ra'ayin kanmu. Babu wanda ya koya mana."

Koda yake a wasu wurare goshin dutse kankara ya dumburo kai, a wasu wurare, Kirista suna yi wa kansu baftisma domin kada a kama shugabannisu. A wasu wurare ana yin baftisma a rafi kuma mutum guda za ya yi baftisma kuma wadanda za a yiwa baftisma sai su rufe fuskarsu da wani yadda babu wanda za ya iya daukar hotonsu.

Jaridar Uchiteiskaia Gazeta ta 30 ga wata Jannairu 1964 ta bada labarin wata lacca ta masu musun Allah a wani kauye Voronin, na gundumar Volnecino Korskii. Da dai mai laccar a sarari ta wurin jefa tambayoyi," wadanda shi mai bada laccar ba ya amsawa. Sun yi tambaya "daga ina ne ku 'yan kwaminis kuke samun kaidodi da'a da yin daidai da kuke kirarisu, amma ba ku yin biyayya da kamar su kada a yi sata, da kuma kada a yi kisan kai? " Kiristocin sun nuna wa mai bada laccar cewa dukkan wadannan ka'idoddin an samo su ne daga cikin Litafin Maitsarki, wanda 'yan kwaminis ke yaki da shi. Mai laccar ya rufe kuma laccar ta kare da nasara a wajen kirista.

## TSANANIN DA AKE YI MA IKILISIYAR KARKASHIN KASA YA YI KAMARI

Kirista na Ikilisiyar karkashin kasa a yau suna shan wahala fiye da da. ana tsanantawa dukan addinai a Rasha.Ga kirista abin karya zuciya ne su san yadda ake ci wa yahudawa mutunci a kasashen kwaminis. Amma wanda aka fi kaiwa hari shine Ikilisiyar karkashin kasa.

Gidajen jaridu na Rasha sun bada rahotannin kame da tuhumar kiristoci. A wani kirista tamanin da takwas aka jefa gidan mahaukata. Guda ashirin da hudu daga cikinsu suka mutu bayan 'yan kwanaki saboda doguwar addu'a. " Yaushe ne addu'a mai tsawo take kisa? Kana iya hassashen abinda suka ratsa?

Masifar da ta fi muni wadda aka dora masu ita ce, idan aka kama su suna koyaswa 'ya'yansu zance kiristi, sai a dauke 'ya 'yan daga wurinsu har abada kuma basu da izinin su ziyarci inda suke.

Tarayyar Rasha ta sa hannu akan yarjeniyar da kasashen dake cikin majalisar dinkin duniya suka yi cewa "ba za a rubuta cewa, "iyaye suna da iko su tabbatar cewa ilimin addini da da'a na 'ya 'yansu ya yi muwafaka da abinda su iyaye suka yi imani da shi." Mai cin amana kareV, shugaban Ikilisiyar Baptist Union" ta kasar Rasha wadda take mallakar gwamnati, ya ce wai Rasha tana bin wannan ka'ida ta Majalisar Dinkin Duniya wadda muka ambata a baya kuma munafukai suka gaskanta da Maganarsa. Yanzu ka saurari abin da jaridun kasar Tarayyar Rasha suka fada.

Jaridar Sovietskaia Russia ta 4 ga Yuni 1963 ta bayyana yadda aka dauke yara daga Ikilisiyar Baftis Makrinkowa saboda an koya masu sanin kiristi da bangaaskiyar kirista kuma an hana su su daura alamar kwaminis a wuyansu.

Lokacin da uwar yaran ta ji hukumcin da aka yanke abin da tace kawai shi ne, "Ina shan wahala saboda da bangaskiya. Dole ta biya kudin wurin kwana na yaran da aka dauke daga wurin ta. Ga shi yanzu ana gurbata zuciyarsu da arnanci. Iyaye kirista suna juyayin irin bakin cikin da ta shiga.

Jaridar Uchitelskaia Gazeta ta fada mana cewa irin haka ta faru da wani Ignatii mullin da matarsa. Mai shari'a ya bukace su da su yi musun Yesu kiristi. Mai shari'ar ya ce, "ku zaba tsakannin Allah da diyarku. Kun zabi Allah? Mr. Ignatii mullin ya ce, "Ba zan yi musun bangaskiya ta ba. "Bulus ya ce, "Dukkan abubuwa suna aikatawa zuwa ga alherin" Na ga irin wadannan yara wadanda aka rena cikin kiristi an dauke su daga iyayensu kuma an sa su a makarantun kwaminis. A maimakon a gurbata zukatansu da arnanci sai bangaskiya da suka samu daga gida ta bazu zuwa ga sauran yaran dake tare da su. Littafi Maitsarki y ace, dukkan wanda yake kaunar 'ya 'yansa fiye da Yesu ba ya isa binsa ba. Wadannan kalmomi suna da ma'ana sosai a kasashen kwaminis.

Ka jaraba rabuwa da 'ya 'yanka mako guda ba tare da ka sa su a ido ba. Daga nan zaka san irin wahalar da 'yan uwa suke sha a Rasha. Ba zai zama an kyauta ba idan yi maganar Ikilisiyar Furotestant ta karkashin kasa kawai.

Kirista na Ikilisiya mai ra'ayin mazan jiya (orthodox) da ke a Rasha sun canja kwata-kwata. Miliyoyinsu sun je kurkuku. A can ba su da zabi, babu giciye, babu mutumi na tsarkaka, babu turare kuma babu kandir da zasu kunna. Membobi suna kurkuku babu keben firis. Firis babu inifam na firis, babu gurasa, babu uwan anab babu mai maitsarki, babu litattafan da za a karanto tsararrar addu'a. Kuma sun gane cewa suna iya rayuwa ba dukkan wadannan abubuwa ba ta wurin•zuwa Allah kai tsaye cikin addu'a. Sai suka fara yin addu'a kuma Allah ya fara zubo masu da Ruhunsa bisansu. Farkawa ta samu a cikin 'yan Ikilisiyar Orthodox a Rasha.

Sai ya kasance cewa a Rasha da kuma kananan kasashe na kwaminis, an sami Ikilisiyar Orthodox ta karkashin kasa, wadda a
gaskiya tana da ra'ayin shela bishara wato Evangelical, kuma 'yar gani kashe ni bishara kuma kurkusa da Allah. Ikilisiyar Orthodox ta karkashin kasa ta haifar da jarumawa na bangaskiya. Wanene yake iya fadin inda dattijon nan babban bishop Yermogen na kaluga yake yanzu?

Ya yi gaba-gadin nuna rashin amincewarsa kan munafuncin da ke cikin hadin kan da ke tsakanin shugabannin Orthodox da gwamnatin marasa Allah ta kwaminis.

Shekaru hamsin na mulkin kwaminis. Jaridun Rasha suna cike da labarin nasarar da Ikilisiya ta karkashin kasa ta samu. Ikilisiyar ta ratsa wahala wadda tafi gaban fada, amma duk da haka ta rike amincinta cikin kiristi kuma ta cigaba da habaka.

Mu a kasar Rumania, mun shuka iri ta wurin aiki cikin sojojin Rasha asirce. Haka na kuma wasu suka yi a Rasha kanta kuma da cikin sauran kasashen da Rasha ta mamaye. Irin da muka shuka yana bada 'ya'ya.

Ana iya ribato duniyar kwaminis zuwa ga kiristi. 'yan kwaminis suna iya zama kirista. Haka nan ma wadanda ake kuntatawa idan dai zamu taimaka masu.

Tabbatar cewa abin da nake fadi gaskiya ne shi ne, ikilisiyar karkarshin kasa tana habaka a Rasha, da China da kuma kusan dukkan kasashen kwaminis. Domin a nuna kyaun' yan uwanmu kirista wadanda ke karkashin mugu yanayi, ga wasu kadan daga cikin wasikun da suka rubuta daga Rasha ta karshen kurkukun Rasha.

## YADDA WATA YARINYA'YAR KWAMINIS MAI SUNA VARIA, TA TUBA. TA SHAIDA SHI. KUMA TA ZAMA BAIWA

Wasikun farko guda uku duk sun fito daga Maria yarinyar da ta kawo Varia zuwa ga kiristi.

### WASIKAR FARKO

Na cigaba da zama a nan. Ana kaunata. Kuma akwai wata memba a nan kurkukun komsomol (kungiyar matasan kwaminis) wadda ke kaunata sosai. Ta fada mani cewa, "Ban iya fahimtar ko wacce irin mutum ce ke". A nan mutane da yawa, suna zagin ki kuma suna kuntata maki amma duk da haka kina kaunarsu duka.

Na amsa na ce Allah ya koya mana mu kaunaci kowa, ba abokanmu kadai ba, amma har da masu gaba da mu. Da wannan yarinya ta bata mani da yawa, amma na yi addu'a dominta da aniya. Lokacin da ta tambaye ni idan ina iya kaunarta ita ma, sai na rungume ta kuma muka fara kuka. Yanzu muna yin addu'a tare.

Idan kun yarda ku yi addu'a domin ta. Sunanta Varia.

Lokacin da ka ji wadanda suke musun Allah suna fada da karfi sai ka yi zaton da gaske suke yi. Amma rayuwar yawancinsu, ko dayake suna la'antar Allah da lebunansu, zukatansu suna marmarinsa. Kuma kana iya jin zukatansu suna nishi --- Wadannan mutane suna neman wani abu kuma suna son su rufe yunwar Ruhu dake cikinsu da amincinsu.

Yar Uwarki Cikin Kiriksti Maria

**Wasika ta Biyu**

"A wasika ta da ta gabata na rubuta maku zancen wata yarinya mai ra'ayin musun kasancewar Allah, mai suna Varia. Yanzu ina hanzarin fada maku, kaunatattu na, game da babban farin cikinmu: Varia ta karbi Kiristi ya zama mai cetonta, tana shaidawa a fili gaban kowa.

## Wasika ta uku

" Jiya biyu ga watan augusta, na sami yin magana da kaunatacciyar mu Varia a kurkuku. Zuciyata tana kuna duk lokacin da na tuna ta. A gaskiya har yanzu yarinya ce. Shekarunta goma sha tara kawai. A matsayin ta na mai bin Yesu Kristi ita jaririya ce cikin ruhaniya. Amma tana kaunar Ubangiji da dukan zuciyarta, kuma gaba daya ta fara da hanya mai wahala.Tana cikin yunwa kwarai. Lokaci damu ka ji cewa tana cikin kurkuku, sai muka fara aika mata da kunshin abubuwa na bukata. Amma sai kadan ta samu daga cikin abubuwan da muka aika mata.

Na tambaye ta, cikin rodiddika na kurkuku nace, Varia, ba ki yin da- na-sani kan abin da kika yi? Tace, "a'a,kuma idan suka sake zuwa zan fada masu zance kaunar Kristi. Ki daina tunanin ko ina shan wahala.Ina yin murna cewa Ubangiji na kauna ta kwarai da gaske kuma yana bani farin ciki in jimre saboda sunansa

Ina roko ku yi addu'a musamman daga birnin zuciyarku saboda ita. Me yiwuwa ne a aika da ita Siberia. Sun kwace mata tufafinta da dukkan abin da ta mallaka. Tana zama babu komai sai kayan jikinta kawai. Bata da yan'uwa kuma dole ne mu tattara mata abubuwan da take bukata. Na kebe kudin da kuka aiko mani, idan aka fitar da Varia zuwa wata kasa ko wuri, zan bata. Na gaskanta Allah zaya karfafata kuma zaya bata ikon jimrewa na gaba. Allah ya kiyaye ta!" Ta ku Maria.

## Wasika ta Hudu

"Zuwa ga Maria, A karshe dai na sami damar da zan iya rubuta maki. Mun iso nan ---Lafiya. Inda aka aje mu ya kai nisan mil goma daga cikin gari. Ba zan iya bayana yadda rayuwar mu take ba. Kin sani. Ina so in rubuta dan bayanni kadan game da ni kai na. Ina godiya ga Allah da ya bani lafiya kuma ina iya yin aiki da hannuwa na. Ni da yar'uwa "X" an sa mu mu yi aiki a ma'aikatar gyaran injuna. Aikin yana da wuya kwarai kuma yasa lafiyar"X" tana tabarbarewa. Ya zama dole ne in yi aikin nawa da nata. Ina fara gama nawa daga nan in taimake ta ta gama na ta. Muna yin aikin har tsawon awa goma sha biyu zuwa sha uku a rana. Bamu da isasshen abinci kamar ku. Amma ba Saboda wannan ne na rubuta maki wannan wasika ba.

Zuciyarta tana godiya da yabon Allah saboda ta wurin ki ya nuna mani hanyar ceto. yanzu ina tafiya a bissa wannan hanyar,rayuwata tana da bege kuma na san inda na nufa da wanda nake shan wuya dominsa.

Ina marmarin fada wa da kuma shaidawa game da babbar salama da murnar samun ceto wadda ke cikin zuciyata. Wanene za ya iya raba mu da kaunar Allah wadda ke cikin Kristi? Babu mutumin ko kuma wani abu da za ya iya. Ko kurkuku ko wahala ba za su iya ba. Wahalolin da Allah ya aiko suna kara mana karfi ne cikin bangaskiyarmu. Zuciyata ta cika da murna da alherin Allah har ma ya na zuba. A wurin aiki suna zagi da horo na kuma suna kara mani aiki saboda bana iya rufe bakina, amma dole ne in fadawa kowa abin da Ubangiji ya yi domina. Ya mayar da ni sabuwar halitta ni wadda da nike bisa hanyar hallaka. Bayan wannan babban alheri ina iya kame baki na? Ina. ba shi yiwuwa. Dai bakina yana iya Magana, zan shaida wa kowa zancen wannan babbar kauna ta Allah.

A hanyarmu ta zuwa wurin da ake tsare mu, mun hadu da yan uwa cikin Kristi da yawa. Akwai ban mamaki mutum ya rika ji a cikin ruhunsa cewa wadannan duk 'ya'yan Allah ne lokacin da ka fara gamuwa da su. Babu amfani mutum yayi kokarin bayyana irin murnar da yake ji. Daga ganinsu mun san su wanene.

Yayinda muke a wurin da ake tsare da mu, a wata tashan jirgin kasa, wata mata ta zo ta bamu abinci kuma ta fadi wadannan kalmomin kawai. Allah na nan.

Yammar farko bayan mun iso nan (dare yayi sosai) sai aka kai mu wani barikin soja dake a karkashin kasa. An marabce mu da wadannan kalmomi, "salama gare ki". Abin da ya faranta mana rai shine, "Mun karbe ku da salama." Kuma da wannan maraice muka ji cewa muna cikin wani iyali.

I' a gaskiya haka yake. Muna nan tare da mutane da yawa wadanda suka bada gaskiya ga kristi a matsayin mai cetonsu. Fiye da rabin fursunonin duk masu bi ne.

A cikin mu akwai rikakakun mawaka da masu wa'azin bishara na gaske. Da maraice, lokacin da kowa ya hallara bayan aiki mai yawa, akwai dadi a zauna tare a yi addu'a a kafafun

Tun da Ubangiji ya bayyana mani kaunar sa mai tsarki, ina daukar kaina a matsayin wanda yafi kowa farin ciki a

Duniyar nan. Tsananin da dole ne in ratsa, ina daukar sa a matsayin wani alheri na musamman. Ina murna da ganin cewa Ubangiji ya bani gatancin shan wahala dominsa tun daga farkon tuba na. Dukkan ku, ku tuna da ni cikin addu'a yadda zan kasance da aminci ga Ubangiji har karshen rayuwata a nan duniya.

Ubangiji Allah ya kwaye ku duka, kuma ya karfafa ku domin jihadinsa.

Ni da yar'uwa "X" muna yi maku sumba. Lokacin da aka aika damu zuwa --- me yiyuwa ne mu sami damar sake rubuta maku. Kada ku damu akan mu. Muna cike da murna da farin ciki, saboda ladanmu a cikin sama mai girma ne. Matta 5:11-12.

Ta ku Varia.

Wannan ce wasikar Varia ta karshe budurwar nan 'yar kwaminis wadda ta sami kristi, ta bada shaidarsa, kuma aka jefa ta kurkuku ta yi aiki kamar baiwa saboda tana shaida Yesu Kristi. Daga wannan wasika ba a kara jin labarinta ba, amma kyakyawar kauna da shaidar kristi da take yi sun nuna iiin armashin, amintacciyar ikilisiyar karkashin kasa acikin kashi daya cikin uku (E) na mutanen duniya wadanda suke karkashin kangin bauta da firi'aunanci na' yan kwminis.



## BABI NA BAKWAI: SEVEN

## YADDA KIRISTOCIN KASASHEN YAMMA ZASU IYA TAIMAKO

## SAKONA ZUWA GARE KU DAGA IKILISIYAR KARKASHIN KASA

Ana kira na, "muryar ikilisiyar karkashin kasa." Ba na jin na isa in zama muryar wannan irin sashe mai girma na jikin Kristi.
Duk da haka, na shugabanci ikilisiyar karkashin kasa a kasar 'yan kwamins har tsawon 'yan shekaru. Ta wurin ikon Allah na iya ratso azaba da zaman kurkuku na shekara goma sha hudu, har da shekara biyu a dakin mutuwa"na cikin kurkuku. Ta wurin ikon Allah kuma aka fitto da ni daga kurkuku aka mika ni ga kasashen yamma domin in yi Magana da ikilisiyar da take da 'yanci'.
Ina Magana a madadin 'yan uwa wadanda ke kwance a cikin kaburbura marasa iyaka. Ina Magana a madadin yan'uwa wadanda yanzu haka suna taruwa a asirce, a cikin daji da wasu wurare a boye.
Ikilisiyar karkashin kasa da ke a Rumania ta shawarta cewa in baro kasarmu, in kawo ma Kirista masu 'yanci dake a duniya sakko. Ta wurin ikon Allah, ga shi na iya fitowa kuma kawo sakonsu dake cikin kunci, da hanzari, wahala kuma suke mutuwa a kashashen kwaminis, suka bani .
Sakon da na kawo daga ikilisiyar karkashin kasa ṣhi ne.
"kada ku manta da mu"
"kada ku juya mana baya"
Kada ku hakura damu"

"ku bamu kayan aiki da muke bukata. A shirye muke mu karbi sakamakon yin aiki da su".

Wannan shi ne sakon da aka aiko ni in fada ko kuwa in mika maku. Ina Magana a madadin ikilisiyar da ake rufewa baki, ikilisiyar karkashen kasa, kurmar ikiklisiya, wadda ba ta da izinin Magana. Ku ji kukan'yan uwanku wadanda ke kasashen kwaminis. Basu rokon a Kwato su, ko a tsare lafiyarsu ko kuma a kawo masu saukin rayuwa. Abin da suke roko shi ne kayan aiki domin su maganci gurbatan zukatan matasansu-manyan-gobe-da ake yi da koyarwa arnanci. Suna rokon littafi maitsarki da yawa wanda zasu mora domin yada maganan Allah. Idan basu da maganan Allah a hannunsu, ta yaya zasu iya yada ta?

Ikilisiyar karkashin kasa tana kama da likita wanda yana tafiya da jirgi, sai jirgin ya yi karo da wani jirgin kuma daruruwan mutane suna kwance a kasa, cikin raunuka, suna mutuwa, likitan yana zagawa cikin mutanen da suke mutuwa, suna kuka a sakamakon raunukan da suka samu likitan yana cewa, "idan da inna da kayan aiki a nan --- idan da kayan aikina suna nan." Da da wadannan kayan aiki, da ya iya ceto rayuka da yawa. Yana da niyar taimakawa --- amma babu kayan aikinsa wannan shine irin halin da ikilisiyar karkashin kasa take ciki! Tana da niyar ta bada dukkan abin da take da shi. A shirye ta ke ta shiga hadari fadawa kurkuku har tsawon shekaru da dama. Amma dukan wannan niya ta ta ba zata zama da amfani ba idan babu kayan aikin da zata mora wajen yin aikin. Rokon amintattu cikin kristi, ikilisiyar karkashin kasa mai gaba-gadi zuwa gare ku, ku dake da 'yanci,shi ne, "Ku bamu kayan aiki littafi maitsarki da litattafan addinin Kirisita sune taimako kuma mu zamu yi sauran abin daya rage."

## YADDA KIRISTOCI MASU 'YANCI ZASU IYA TAIMAKO

Kowanne kirista mai 'yancin walwala yana iya yin taimako nan take ta wadannan hanyoyin.

Masu musun kasancewar Allah su mutane ne wadanda basu yi imani cewa ransu ya samo asali daga wani wuri da ba a iya gani da wannan idannun ba. Ba su da sani da kuma tunanin abin al'ajibin da ke cikin duniya da kuma cikin. Rayuwa, kirista suna iya taimakonsu sosai ta wurin yin tafiya cikin bangaskiya, suna rayuwa cikin zumunta da Allahmu wanda ke boye.

Suna iya taimaka mana sosai ta wurin yin rayuwa irinta tsayayyun Kirista, rayuwa ta sadaukarwa ga Kristi. Suna iya taimakawa ta wurin nuna rashin amincewa a sarari da tsananin da ake yiwa Kirista.

Kirista na yammacin duniya suna iya taimakonmu ta wurin addu'a domin 'yan kwaminis su sami ceto. Irin wannan addu'a ana ganinta kamar shirme. Muna yin addu'a domin 'yan kwaminis kuma suna ganna mana azaba wanda har tafi wanda suka yi mana kafin mu yi addu'a saboda su. Amma haka addu'ar Ubangijin Urshalima ta kasance. Suka giciye shi bayan ya yi wannan addu'a. amma bayan wasu kwanaki, suka buga kirji kuma mutane dubu biyar suka tuba cikin rana guda. Ga sauran ma, basu yi asarar addu'ar ba. Kowacce addu'ar da bata karbu ga wanda ka yi dominsa ba, zata komo maka da albarku masu yawan gaske kuma ta zama la'ana ga wanda ka yi wa addu'ar. Domin cika maganar Kristi, ni da sauran Kiristoci da yawa, muka rika yin addu'a domin Hitler da mutanensa. Kuma na tabbata addu'ar mu ta taimaka wajen cinye Hitler da yaki da kuma harsasan sojojin kawance.
Lallai ne mu kaunaci makwabtanmu kamar ranmu. 'Yan uwa kwaminis makwabtanmu ne kamar sauran mutane.

Kwaminisanci sakamakon rashin cika maganar Kristi ne da ya ce, "Na zo in bada rai kuma rai a yalwace. "Kirista har yanzu basu wadata kowa da kowa da ran nan ba. Sun bar wasu suna fama da duk abin da ransu ya dauki mahimmanci ko daraja. Irin wadannan ne suka yi tawaye suka hadu suka zama 'yan jami'yar kwaminis. Yawanci lokaci mutane ne da aka yi wa kwara wajen hakinsu. Yanzu suna jin zafin abin kuma suna nuna rashin imani. Dole ne mu yake su. Amma Kirista, ko da suna fada da abokin gaba, suna fahimta kuma su kaunace shi.



*Kasa da shekaru goma da suka wuce ana kone su Bible bisa tsarin komunis a Soviet Union ta da. Bible nan a bisa an kwato shine daga harshen wuta lokacinda hanya ta budu, an yi yunwa mai yawa na maganar Allah har ma da yansanda suna wasoso.*



Muna da alhakı a kasancewar wasu 'yan kwaminis. Muna da alhaki ta wurin a kalla, rashin kulawa da aikinmu.

Saboda wannan, lallai ne mu biya ta wurin nuna masu kauna(wadda wani abu ne wanda ya bambanta da sonsu) kuma mu yi ta addu'a dominsu.

Ban gaskanta cewa kauna kadai ce zata iya magance matsalolin kwaminis ba. Ba zan ba hukuma shawara ta magance matsalar izgilanci da kauna kawai ba. Dole a sasance da 'yan sanda, alkalai da kurkuku saboda maganin 'yan iska, ba fastoci kadai ne za su yi wannan aikin ba. Idan dan iska ya ki ýa tuba, dole a tsare shi a kurkuku. Ba zan taba yin amfani da kalmar nan ta Kirista game da "kauna" domin tarbar 'yanci na siyasa, tattalin arziki ko al'adu domin yaki da kwaminis ba, ganin cewa basu wuce iskanci ba. 'Yan iska suna satar jika,, har da satar kasa baki daya.

Amma lallai ne fasto da sauran mutane su yi bakin kokarinsu su kawo 'yan kwaminis zuwa ga Kristi ko ma wanne irin laifi ne ya aikata da kuma wadanda suke kuntatawa. Lallai ne ya rika yin addu'a dominsu tare da fahimta.

## ANA MATUKAR BUKATAR LITTAFI MAITSARKI DA LITATTAFAN BISHARA DA GAGGAWA

Abu na biyu shi ne, Kirista masu 'yanci suna iya taimakawa ta wurin aikawa da Littafi Maitsarki da litattafan bishara. Akwai hanyoyin aikawa da su zuwa cikin kasashen kwaminis. Tun da na fito, na rigaya na aika da wasu da yawa, wadanda sun isa can lafiya. Hakika akwai hanyoyin aikawa da su, idan dai ku Kiristoci masu 'yanci, zaku bada domin 'yan uwanku na ikilisiyar karkashin kaša. Lokacin da ina a Rumania, ni ma na sami littafi Maitsarki da yawa wadanda aka kawo ta su hanyoyin aikawa da su, a dai bayar da su kawai.

yan'uwa suna cikin matukar bukata. Dubban Kiristoci a can basu ga Littafi Maitsarki ko wasu litattafan bishara ba har tsawon shekara ashirin zuwa hamsin a Rasha da kuma kashashen kwaminis.

Wata rana, lokacin ina Rumania, wasu kazaman kauyawa suka zo gidana. Sun zo daga kauye domin aikin kwashe kankara daga kan hanya da sauransu domin samun 'yan kudin da suke sa ran sayen ko da tsohon Littafi Maitsarki su kai kauyensu. Saboda na sami Littafi Maitsarki da yawa daga Amerika, sai na basu sabon littafi

Maitsarki ba tsoho ba. Sai suna ganin abin kamar mafarki. Suka yi kokari su biya ni da kudin da suka samu daga aikin kwashe kankara, na ki amsar kudinsu. Sai suka yi hanzari suka koma kauyensu da Littafin. Bayan 'yan kwanaki na sami wasika mai bayyana matukar murna da godiya saboda maganar Allah da suka samu, kauyawa talatin ne suka sa hannu akan wasikar. Sun raba Littafi Maitsarki gida talatin, kowanne ya dauki bangare guda, idan wannan ya gama da nasa sai su yi musanya da wani.

Abin tausayi ne ka ji mutumin Rasha yana rokon a bashi ko da shafi daya tak na Littafi Maitsarki. Yana ciyar da ruhunsa akan wannan shafi. Suna jin daddin su bada san iya ko akuya a basu Littafi Maitsarki. Akwai wani mutum da na sani wanda ya bada zoben aurensa musanya da fatattakakken sabon alkawari. Ya'yanmu basu taba ganin katin Kirisimati ba. Idan da zasu sami guda, da dukkan yaran kauyen zasu taru domin su gani, kuma wani tsoho ya bayyana masu labarin jariri Yesu, da budurwa maitsarki daga nan kuma labarin Kristi da ceto. Dukkan wannan --- daga katin kirisimati guda. Muna iya aikawa da Littafi Maitsarki da litattafan addinin Kirista. Wannan wata hanya ce wadda zaku iya yin wani abu. Abu na uku, dole mu buga kuma mu aika da Litattafan addinin Kirista na musamman domin mayar da martani a kan harin da koyarwa arnanci take yi don gurbata zukatan matasanmu tun suna kanana har girmansu. Yan kwaminis sun shirya, wani Littafi mai suna, "The Atheits Guide book." Shine kundin arnanci na yan kwaminis. Sun shirya irinsa na koyawa yara kanana da kuma mai tsauri don koyawa wadanda suka yi girma, wato ana biye da su, suna girma ana gurbatar zuciyarsu.

Har yanzu Kirista basu buga wani littafi wanda ya ba wannan littafi "The Atheit's Guide book" amsa ba. Muna iyawa, kuma dole ne ma mu buga kuma mu aika da amsar Kirista ga wannan koyarwar arnanci mai dafin gasket. Dole mu yi wannan ba tare da jinkiri ba, domin ikilisiyar karkashin kasa bata da wasu litaffafan da za su ba wadannan matasa da aka gurbata zuciyarsu da wannan muguwar koyarwa ta wannan littafi. Hannuwan ikilisiyar karkashin kasa a daure suke a baya har sai ta sami irin wadannan litattafai a cikin harsunan mutanen kasashen kwaminis.

Matasanmu wadanda aka gurbata zucciyarsu suna da amsa amsa ta Allah amsa ta Kirista-amsarmu. Wannan ma wani abu ne da zaku iya taimakawa a yi, ta wurin bada litattafi irin masu koyar da sanin Allah a matsayin amsa ga wannan littafi "The Atheit's book.

Abu na hudu, dole ne mu hada hannu tare da membobin ikilisiyar karkashin kasa kuma mu basu taimakon kudi domin su iya yin tafiye-tafiye a jirgi domin yada bishara. A halin yanzu, da dama daga cikinsu suna dabaibaye a gidajensu saboda rashin kudin tafiye-tafiye, da motoci da kuma abincin da zasu ci a cikin tafiye- tafiyensu. Saboda wadannan bukatu, sun yi turus basu iya motsawa su zagaya, yayinda kauyuka masu nisan mil ashirin zuwa talatin kawai ana ta kiransu domin taro amma basu iya zuwa saboda rashin kudi. Ta wurin basu yan kudi kamar fan biyar zuwa goma (£5 £10) kawai duk wata muna iya kwance masu dabaibayin su je su amsa kira masu iya zuwa kauyuka da garuruwa masu dan nisa domin kai maganar Allah.

Fastoci na da wadanda aka taba daurewa saboda bangaskiyarsu, suna da kwazucin isar da sakon bishara, suna da kauna sosai ga batattun rayuka amma basu da halin kai masu sakon zuwa kauyuka da garuruwansu. Yan kudi kalilan duk wata zasu basu damar kai sakon. Dole ne a taimakawa Kirista na wannan wurare domin, saboda kasancewarsu Kirista ta sa basu da ko isashen abinci,

da kome wanda zasu iya mora domin zuwa kauyuka da garuruwa don yada bishara. Wannan shi ne aikin al'ajibi, yan kudi kadan sun ishe su su yi aikin.
Fastocin ikilisiyoyi mallakar gwamnati wadanda suke gudanar da aikin yadda bishara ta ainihi a asirce dole ne a taimaka masu da kudi domin yin wannan aikin. Gwamnatin kwaminis ce ta yanka masu albashi wanda kuma yayi kankanta kwarai. Niyar wadannan fastoci ta sa yancinsu cikin hadari ta wurin yin watsi da ka'idodin kwaminis kuma suna wa'azin bishara ga yara, matasa da manya a taruruka na asiri, amma suna ganin duk wannan bai isa ba. Dole ne su sami halin da zasu iya gudanar da wannan aiki na su mai alfanu.

Fan biyar ko goma a wata taimakawa irin wadannan membobi na Ikilisiyar karkashin kasa sosai wajen yada bishara. Wannan ma wata hanya ce da zaku iya taimakawa Ikilisiyar kaskashen kasa.

Daga nan kuma dole ne mu yada bishara ta hanyar radiyo zuwa cikin kasashen kwaminis. Ta wurin yin amfani da tashoshin radiyo dake a kasashe masu 'yanci, muna iya ciyar da Ikilisiyar karkashin kasa, wadda ita ma kanta tana da bukatar gurasa ta rai, da abincin ruhaniya. Saboda gwamnatocin kwaminis kansu suna moron tashoshin radio masu gajeren zango domin yada furofagandarsu zuwa ga mutanensu, miliyoyin mutanen Rasha da kuma sauran mutanen da ake dannewa suna da radiyoyi wadanda suke sauraron shirye-sherye. Yanzu kofofi a bude suke domin baza bishara ta hanyar radiyo a kasashen kwaminis. Dole ne a fadada wannan aiki. Dole ne Ikilisiyar karkashin kasa ta sami abincin ruhaniya da irin wadannan shirye-shirye gidan radiyo ke badawa. Wannan ma wata hanya ce da zaku iya taimakawa Ikilisiyar karkashin kasa dake a kasashen kwaminis.

## MUMUNAN HALIN DA IYALAN JARUMAWAN BANGASKIYA SUKE CIKI

Dole ne mu taimakawa iyalan Kiristan da aka kame. Dubban irin wadannan iyalai yanzu haka suna cikin matsananciyar wahala wadda tafi gaban fada. Lokacin da aka kama memba na Ikilisiyar karkashin kasa muguwar wahala ta afkawa gidansa. Babban laifi ne a wurin gwamnatin kwaminis wani ya taimakawa iyalin wanda aka kama. Wannan wani shiri ne da kwaminis suka yi domin su kara wahalar da mata da yaran da aka bari baya. Lokacin da aka aika da Kirista kurkuku kuma yawanci lokaci ana yi masa azaba wani lokaci har da mutwa wahala farawa aka yi. Iyalinsa sun shiga wahala babu iyaka. Ina iya fada maku gaskiya, idan da Kiristoci na kasashen yamma basu aiko mani da iyalina taimako ba, da ba zan taba rayuwa har in iya kasancewa tare da ku kuma in rubuta wadannan kalmomi ba.

Tun da aka sako ni, kungiyar, "The European Christian Mission" ta rigaya ta aika da taimako mai yawa zuwa ga iyalan Kiristocin da aka kama saboda Yesu Kiristi. Abin da aka rigaya aka yi kalilan ne idan aka kwatanta da abin da za a iya yi da taimakonku.

A matsayina na memban Ikilisiyar karkashin kasa wanda ya rayu har kuma ya kubuto, na kawo maku sako, da roko daga 'yan uwana wadanda na baro cikin kunci.

Sun aiko ni in baku wannan sako daga garesu. Ta wurin alherin Allah na rayu har na iya baku sakon.

Na fada maku bukatar gaggawa ta kai bisharar Kiristi ga duniyar 'yan kwaminis. Na fada maku bukatar gaggawa ta taimakawa iyalan Kiristocin da aka kama aka jefa kurkuku. Na fada maku wasu hanyoyin da zaku iya yin taimako ga Ikilisiyar karkashin kasa ta cika aikinta na yada bisharar Almasihu.

Lokacin da aka buge ni a tafin kafa sai harshe na ya yi kuka. Menene yasa harshe na ya yi kuka? Ba shi aka buga ba. Yayi kuka domin da harshe da kafa duka gabobin jiki guda ne. Kuma ku kirista masu 'yancin walwala ababuwan jikin kiristi ne wanda yanzu haka ake dukansa a kurkukun 'yan kwaminis wanda yanzu haka yana bada jarumawan Kiristi.

Kuna iya jin radadin da muke ji?

Ikiliisya ta farko da dukkan kyaun ta, da sadaukarwarta ga bisharar Kiristi ta sake bayyana a kasashen kwaminis.

Yayinda Ubangijinmu Yesu Kiristi yake cikin addu'a da bakin ciki a lambun Jatsamani, Bitrus, da Yakub da kuma Yohanna sun zama duwatsun da aka jefar daga rikaken wasan tarihi amma fa suna cikin barci ne mai zurfi kwarai. Yaya yawan kauna irin ta Kirista da kake nunawa zuwa ga wannan bukata ta taimakawa wannan jarumar Ikilisiya? Ka tambayi fastonka da shugabannin Ikilisiyarku abin da ake yi a cikin sunanku domin taimakawa 'yan uwanku dake a kasashen kwaminis.



*A farkon shekarun 1969 Balon-balo dauke da Bisharu an kadamar da su zuwa Korea ta Arewa. An ci gaba yau da irin wannan buga rubutu ta musamman ta Bishara a Balon-balo da ke nuna Hanya zuwa ga Allah.*

Yanzu haka wani sabon kame-kamo na masu bi ya barke a Rasha da kuma wasu wurare. Ko da yaushe ana samun Karin jarumawan Kiristi ko dayake suna tafiya zuwa kaburburansu da ladansu, iyalansu suna rayuwa cikin mumunan hali. Muna iyawa kuma dole ne mu taimake su. I' gaskiya ne dole mu taimaki mutanen dake cikin yunwa a Indiya da Afirika. Amma wanene yafi bukatar taimako daga cikinsu masu fama da yuuwa ko kirista da iyalan mutane da suka mutu domin kiristi ko kuwa wadanda aka gana ma azaba a cikin kurkukun 'yan kwaminis saboda bangaskiyaarsu?

A kurkukun kasashen kwaminis ana sake maimaita irin jarumtakar da Ikilisiyar farko ta nuna amma Ikilisiyoyin da suke da 'yanci suna barci.

'Yan uwanmu da ke a can, ba tare da taimako ba suna yakin da yafi kowanne bukatar gaba-gadi a wannan karni daidai da jarumtaka da sadaukarwa irin na Ikilisiyar farko. Kuma Ikilisiyoyin da suke da 'yanci suna barci mai zurfi har basu san gwagwarmaya , da 'yan uwa suke sha ba, kamar yadda Bitrus da Yakub da kuma Yohanna suka yi barci a lokacin da mai cetonsu ke cikin bakin ciki.

Ku ma zaku yi barci yayinda 'yan uwanku cikin Kiristi suke shan wahala da kuma yaki domin bishara su kadai?

Zaku ji sakonmu: ku tuna da mu, ku taimake mu?

"Kada ku juya mana baya."

Yanzu na baku sako daga aminitacciyar Ikilisiya ta karkashin kasa wadda ke a kasashen kwaminis daga 'yan uwa, maza da mata wadanda suke shan azaba a karkashin kangin bauta na kwaminisanci.

**VOICE OF THE CHRISTIAN MARTYRS NIGERIA**
P.M.B 210778 Ikeja, Lagos.
E-mail: stephens@skannet.com
Website: www.stephens-persecution.com
Tel: 234-1-4720530, 4724614




Richard Wurbrand, wanda jikinsa ke dauke da tabbai na azaba da hakuba da ya sha har tsawon shekaru goma sha hudu a kurkukun 'yan kwaminis, ya bada shaidar karfin hali da jimirin cigaba cikin bangaskiya na daruruwan kirista.

An yage su daga kaunatattunsu, an wulakanta jikunansu amma acikin ruhu, sun cigaba babu ja da baya acikin bangaskiyarsu ta masu bin Almasihu.

# SHAN AZABA DOMIN KRISTI

## Voice of the Christian Martyrs Publications


**Nigeria:** P.M.B 21078 Ikeja, Lagos. Tel: 234-01-4720530, 08033082342, e-mail : stephens@skannet.com

**Kaduna:** P. O. Box 9311, Kaduna. Kaduna State

**Ghana:** P.O.Box CT. 3016, Accra, Ghana